💫 ALKAWARIN ZUCIYA 💫

PROMISE OF THE HEART 💔

✍🏻M SHAKUR

1️⃣
~UK~
Tundaga nesa take leke babban building din datake dumfara tana bin uban tulin cars din wajen da kallo kaman akwai abinda take nema kafin daga bisani idanuwanta su sauka kan wata white Bentley car, gashinan kar kar ko alamun a single dust babu ajikin motan, ajiyan zuciya tasauke ahankali murya chan kasa tace “Alhamdulillah he’s still around” sanan tashiga sauri takarasa gaban wajen da ake kira da Cozy, harzata saka hannu tabude kofan tashiga tadanyi jim tsaya kafin ahankali tabi jikin ta da kallo tana sanye dawani white jeans daya kamata tsam dawata yar dark blue top mai shegen kyau wacce da kadan tasauka daga kan cibiyanta, saidan gyalen data yana kanta white shima dayamata kyau sai gashin kanshi dakenan kusan rabi awaje anmata kalaba da attachment kanana dayamata kyau shima, hannunta rikeda wasu books guda biyu dakuma phone nata kirar iPhone 13, sai wata yar karaman jakan datake rataye da ita, ajiyan zuciya takara saukewa kana ganinta kasan she’s nervous sanan ahankali tasa hannu tabude kofan wajen tashiga ciki.

Hadaden eatery ne and bar mai shegen kyau, babu wasu mutane dayawa awajen wayanda suke wajen yawancinsu turawa ne fararen fata maaikatan wajenma fararen fatane hakan yasa zaka gane wajen na bature ne, ahankali take tafiya tanabin wajen gabaki daya da kallo da gefen idanunta, kafin takarasa gaban kanta taja kujeran wajen ta zauna sanan tasauke books dinta agabanta da wayanta, daidai baturen Bar attendant din yakaraso yana kallonta yace “what can I get you miss” dan waigawa tayi kaman tana neman abu awurin tace “Pierre Zēro Rosé please, two shot” ganin duk tana maganan ne batare datama kalleshi ba yasa yace “gotcha” sanan yajuya yakoma yadauko wine din datai order yazuba mata a cups guda biyu sanan yadawo gabanta ya ijiye yace “here we go” dan juyowa tayi da sauri takallai sanan tasauke jakanta da sauri tadauko kudi taba shi tace “keep the change” kafin ma yay magana tasake juyarda kanta tana bin mutanen wajen da kallo one after d other…..

“Kai Zayn look” wani hadadden chocolate guy daga tachan karshen babban falon wajen da aka cikada kujeru ne kowa na zaune yana abinda yake yataba wani kyakkywan thick farin guy dake zaune kan kujera ya lumshe idanu pipe din shisha na bakinshi yana zuka yana fitarda hayakin ta hanci, yana sanye da riga da wando both black na LV, farine shi kal yanada cikan jiki dayake rigan dayasa short sleeve ne hakan yafito da kakkauran murdadden hannunshi, irin guys dinan ne masu manyan gabobi dakuma murdadden jiki, dudda idanunshi a lunshe but idan ka kalleshi

bazaka so kadauke idanunka ba dan yanada wani irin kyau kaman mace, lips dinshi sunyi wani kalan masifan ja kodan shishan dayake shane oho, yanada dogon hanci siriri dayazauna akan fuskanshi gwanin ban sha'awa, sai gashin giranshi baki sidik kuma acike yanada tabon salla agoshi sai gashin kanshi baki sidik shima dake kyalli sun nannade kaman na buzu sanan gawani kwantaccen saje a fuskanshi Masha Allah, koda ace shiyay kanshi bazaiyi kanshi da wanan kyau dinba ballema bashi yayba.

Ganin baida niyyan amsashi yasa Mamu ya fizge pipe din shisha dake bakinshi yace "kafara ko ina maka magana kamin banza" ahankali yabude idanunshi dasuka wani lumshe sukai yaushi da idanda zai kalli mace dasu sai lissafinta yarikice sanan yazubasu kan Mamu kaman ance yay magana dan dole yace "what"? Dan murmushi Mamu yayi da hannu yamai alamu yace "look over to the counter ga budurwanka chan, stalker dinka tazo sai kallon ka take wlh, haba Zayn kaiko bazakaji tsoron Allah ka kula yarinyar nan koda sau daya bane tunda dai ta kasa maka magana for morethan 2months yarinyar nan kullum binka take tana stalking naka tana kallonka u know she really really likes u waikai maisa kacika wulakanta mata ne eh? Anyway I don't blame you ni wlh in mace ne banmaga abin so ajikinka ba mutum dukgaka nan kalan asibiti farin fata kalan cuta, duk baku da karfi" dan murmushi yayi dan yasan Mamu so kawai yake yajashi suyita surutu this afternoon shikuma baida time dinan, hannunshi yamikamai alamun yabashi shishi shi, ijiye pipe din shishan Mamu yayi kan table din gabansu yace "Ya isheka hakanan gashinan duk idanunka sun chanza launi, munada lectures yanzun nan fa I think in the next 5min" dan tsaki yaja yasa hannu yadauki pipe din shisha yacigaba dasha abinshi yana daddanna wayanshi yana hura hayakin ta hancinshi batare dayama daga kai ya kalli inda Mamu yacemai yarinyar nan takeba Mamu nabinshi da kallo yarasa yanda zaiyi yaraba Zayn da shisha, shima bawai bayasha bane no but occasionally yakesha, shiko Zayn zai iya wuni yanashan shisha hakanma yasa baya iyacin abinci sosai, ganin yasake lumshe idanu yasa Mamu yaja tsaki yamike tsaye yace "dalla Malam wuce mutafi" bude idanunshi yayi dasuka dan kankance sukaija sanan ya watsama Mamu harara kafin ahankali ya ijiye pipe din yamike tsaye dogon namiji ne nagaske, budadde sanan kuma cikakke irin mazan nanne da ake kira da burin mata, car key dake kan table din yadauka yana rikeda wayanshi yay gaba abinshi batare daya cema Mamu komi ba yay hanyar kanta.

Tundaga nesa ta hangoshi ya dumfaro gaban kanta, duk taku daya dazaiyi saita jishi har kirjinta yana amsawa, tun kafin ya iso wajen wani kalan kamshin dayakeyi dayake neman sata ta haukace sabida sonshi ya lullube mata hanci ganin ko'ina najikinta yadau kyarma yasa ahankali tasa hannu tadauki cup na drink dinta takai bakinta still tana kallonshi ta gefen idanunta daidai ya iso ya tsaya dab da ita dasauri bartender din yazo yace "u done sir" bai amsashi ba yasa hannunshi a wandonshi yaciro wallet dinshi yabude yana kokarin zaro kudi ko kadan batasan drink din yamakai saman hancinta ba tsabagen yanda take kallonshi kawai numfashin dazata shaka ta shaki wine din wani irin mahaukacin shakewa tayi dabama tasan lokacin data saki cup din akasa ba tana wani kalan mahaukacin tari wine nabin hancinta suna fita idanunta sunyi ja kwalla yacikasu dawani kalan sauri daga Bartender din harshi suka juyo suna kallonta dasauri Bartender din yataho ta saitin gabanta yace "sorry Miss" dudda tarin datake kokarin danne tarin

take tana kakalo murmushi dan wanan kwafsin haka har ina baki tabude zatai magana wani tarin yakara sarkaketa wine din na fitowa daga bakinta yana diddiga akan white wandonta duk yay staining sabida Jan wine ne, kaman daga sama taga wani clean white handky agabanta kamshin da ajikin mutum daya tall a duniyan nan takejin kamshi taji yana fitowa daga hanky ahankali tadago kanta sama tanabin Tundaga handkerchief din dakallo harzuwa white hannun dake rikeda shi zuwa kan fuskan Zayn dake kallonta in the eyes, wani sabon bugawa zuciyanta yashiga yi hannunta har rawa yake tasa takarba zatakai kan fuskanta dan sharewa shikuma yajuya ya ijiye kudaden dayariga yaciro daga wallet dinshi yadaura kan kantan yajuya yawuce batare daya kara bata second look ba, ahankali ta janye handky dagakan bakinta tabishi da kallo harsaida yabace ma ganinta sanan tasauke ijiyan zuciya kafin ahankali tasauke kanta tana kallon handky din ko kadan tama manta inda take rungume handky tayi akirjinta tana murmushi sosai.

💫 PROMISE OF THE HEART 💫

ALKAWARIN ZUCIYA 💔

✍🏻M SHAKUR

2️⃣

Murmushi Bartender din yayi inda sabo yasaba yasan yanda yarinyar nan ke crushing on that guy like hell, not just her da many other ladies ma, sabida guy dinan cinikin dasukeyi yanzu a eatery dinan is mind blowing, dazaran ansan yana ciki yammata zasu fara tururuwa suna shigowa from no where so koshima he’s happy for her at least yau yakulata, he hope suyi relationship dudda guy din dumping yammata yake anyhow kaman trash kuma ko ajikinshi dan yasan yanda suke binshi, he just hopes wanan will not be one of his victims, dan yana using babes kaman yanda yake using pen na rubutu idan yagaji da wanan ya yar yadauki sabo.

Tadade awajen ita kadai sai murmushi take tana daddaura handkerchief din akan fuskanta tanajin dadi daga bisani wayanta yashiga kara, dasauri ta kalli wayan ganin Juliana Munari ke kiranta yasa dasauri tadauka tana murmushi sosai tace “Hi Babe ya” daga tachan bangaren wata yarinya tace “ina apartment dinki amman bakinan Ayshu where are you? Ba tundazu muka gama lectures ba” murmushi tayi sosai tace “ina Cozy” dan jim Jully tayi tace “for Godsake Aisha when will u get sense? Eh, look at the way Kabeer ke binki Ayshu yaron nan loves you like a mad man amman kina nan kina stalking wanan heartbreaker da the worst part baimasan kina existing ba” dasauri Aysha tai fari da ido tace “says who, wayace miki baisan ina existing ba? Wlh yasani infect right now ma yanzu haka handkerchief dinshi nake kallo a hannuna it feels warm and smells succulent, OMG it smells just like him wlh, I feel kaman Zayn dina ne

anan wajen” shiru Jully tayi saikuma chan tace “Ayshu I am ur friend and I will always tell you the truth, forget that guy he’s nothing but a dream and face the reality face wanda ke sonki ba wanan ba da kowa in our university sunsanshi ba wajen using yammata yay dumping nasu, Ayshu enough of this stalking, sabida yaron nan kin chanza gida kin dawo apartment din dayake, kin biya kudi double of the normal amout sabida acire tenant din dake zaune adakin dakenan directly opposite nashi kinyi parking kin koma compund din, Aysha sabida yanda kike stalking guy dinan kinsan karfe nawa yake tashi, karfe nawa yake fita gym, karfe nawa yake shiga school, sau nake yake da lectures kinsan all his spots, grades dinki kullum low suke karayi sabida soyayyan wanda baisan dakeba ke gabanki kum…” “Jully please enough, allow me to leave my life, ana so by force ne banson KB ki rabudani da maganan shi, kuma zaki gani Zayn will notice me and I will date him” dasauri Jully tace “dating Ayshu bakince min Islam dating babu kyau ba” dan yatsine fuska tayi tace “Jully is because bakisan guy dinan bane saisa, irinsu idan kika basu kanki ne kawai zasu zauna dake, dan gayu ne nafitina kaman ba muslim ba, boko tashigeshi, I want him to be addicted to me kaman yanda yakenan addicted to shisha, I am ready to give him anything, wlh Ina bala’in sonshi, just wait for me, ki dafa mana abinci gani nan zuwa”
tana maganan ta katse waya shiru Jully tayi, at this point zubama Ayshu ido zatayi dan Allah yama Ayshu taurin kai batajin shawara, kuma yaron nan will only break her heart, she will only chop breakfast a hannunshi a nothing will happen yaron da har lecturorin su mata crushing suke akanshi, anyway she just hope for the best.

Wuraren 6 ta shigo gidan, kana ganin gidan kasan na mugun yaran masu kudi ne, elevator ta shiga zuwa floor dinsu sanan tawuce Dakinsu tana kallon nashi dakin datana gani tasan baidawo ba daman baya dawo da wuri kullum sai 11 ko 12 nadare kuma kullu yaumin bata iya bacci saitaga dawowanshi wata rana tai kuka duk randa zai dawo da mace wata tana kuma tai murmushi, the truth is baifiye neman mata ba, wani zubin zaiyi 2month baidawo dakowace mace ba wani zubin kuma saiya dawo da mace zasuyi kusan kwana uku ko hudu tare saikuma shikenan bata kara ganinta dudda batasan dalili ba but kawai haka take gani, kuma baka taba ganinshi da babe din dabataci sunanta babe ba, duk tana tunanin nan tana tafiya ne tana kaiwa gaban Dakinsu tabude kofa tashige ciki tana ihu kitchen tafada tawani irin rungume Jully tana nuna mata handky tace “Jully look” murmushi Jully tayi tana kallon handky sanan tace “Ya akayi yabaki handky shi”  nan tabata labarin from A to Z tana murna, murmushi Jully tayi tace “nidai jeki wanka kizo muci abinci dan Jerry zaizo yadauken” gira daya Aysha tadaga mata tace “Iyye love birds” tai maganan tana wucewa bedroom nata tashiga sanan ahankali ta ijiye handky kan pillow dinta tareda shafawa sanan tawuce ta shiga wanka agurguje tana fitowa tazo sukaci abincin tare sanan Jully ta shirya ta wuce abinta, komawa tayi ta kwanta kan gado tadauki handky tana kallon shi kafin ahankali tace “Zayn! I love you so very much Zayn” rungume handky tayi akirjinta tsamtsam tanaji kaman shita rungume, ahaka bacci ya kwasheta 11 dot na bugawa ta bude idanunta tsam shi kanshi gangar jikinta yasaba da stalking nashi, fitowa falonta tayi tai hanyar window ta ta tsaya dayake wutan dakin akashe ne ta tsaya tana kallon kofarshi tana tsaye awajen kam wajejen 11:30 saigashi ya shigo yana tafiya nan cikeda isa akuma

hankali tundaga wajen saida kamshin dayake yadaki hancinta bude kofanshi yayi ya shiga sanan ya maida yarufe kafin ya kashe wutan falon, murya chan kasa tace “good night My love, asuba tagari” sanan ahankali tasauke window blind din tajuya takoma daki ta kwanta saikuma kaman wani abu yafado ranta dasauri ta tashi tadauki handky tafada bayi ta wan ke shi tsaf sanan ta shanya tafito tazo ta kwanta, shida dot tabude idanuwanta agurguje tafada bayi tadauro alwala tafito sallan ma agurguje tayi bama ta tsaya cire hijabin ba tafito ta daga window blind ta tsaya jikin window dan 6:30 dot yake fitowa tafiya gym, tana tsaye saigashi yafito cikin kayan workout gajeren wando da singiletin Riga da safa da canvas, cinyanshi tabi da kallo amunmurde kaman na yan wrestling sanan yaja kofan dayake da pin suke bude kofan yawuce yana jogging yatafi abinshi murmushi tayi ahankali sanan tace “good morning  baby na” sanan tajuya handkerchief din tadauka tai ironing nashi, sanan ta shiga wanka tadade sosai abayin sanan tafito tana ganin 8 saura da sauri tawuce wajen window Wuraren 8 yashigo yana zufa murmushi tayi dasauri tajuya tashiga ciki wani hadaden short gown ta saka daya sauka daga guwiwabta da kadan pink yamata kyau Wanan Karan batasa dankwali ba sai turaren data feffesa sanan tai parking gashin ta in a stylish way sanan ahankali tadauki handky tana kallon kanta agaban madubi ahankali tace “Ya Allah kadaurani akanshi” sanan ta zura slippers dinta tawuce tafita falo ahankali tabude kofa tafito daga flat dinshi sanan kaman wacce abi yafashewa aciki tai hanyar dakin shi kirjinta na daukan uku uku tawuce gaban dakinshi tadade atsaye kafin ahankali ta danna door bell, ankai kusan 5min kaman bazaa budewa farat aka bude kofan gabadaya dasauri tadaga kanta suka hada ido wani irin faduwa gabanta yake tana kallonshi yana daure da bathrobe ajikinshi kirjinshi duka abude gashin kirjinshi akwance ruwa nabi sai karamin towel a hannunshi yana goge kanshi da alamu daga bayi yake, da mamaki yadan kalleta batare datai magana ba, lips dinta har rawa yake sanan ahankali tadaga hannunta dake rikeda handkerchief din murya chan kasa tace “ahhhhhmmm dama, dama, I brought your handkerchief back ne” tai maganan tana wani irin nishi sama sama kaman numfashinta sai dauke, kirjinta nawani irin racing, this is the first time take ganinshi ahaka, ganin still kallonta yake ba yabo ba fallasa kuma bai fasa abinda yake ba wato sharekanshi da karamin towel din dayake rikedashi, yasa taji wani bala’in fargabanshi na cikata jin baice komiba dakyar tadaga hannunta tamai pointing kofan dakinta dake kallon nashi tace “actually that’s my flat, yanzun nan naganka shine nace uhmmm bari nakawo ma” dan yatsine fuska yayi amugun wulakance ya kalli handky datake mikamai tundazu har hannunta na neman sagewa yace “I don’t need it, discard it” yaja kofan zai maida yarufe da sauri tace “uhmmm wait please” chak ya tsaya yana kallon fuskanta da fuskanshi dababu alamun rahama akai face dinshi looking kaman zai maketa, tagefenshi taleka tana kallon indomie da taga yafito dashi zai dafa yacika ruwa a babban pot yazuba albasa aciki ya fasa kwai aciki ruwan na kumfa sosai, dan murmushi tayi cikeda shakkanshi tace “are you trying to cook indomie”? Yana kallonta still a bala’in wulakance yace “uhn” kaman dole akace yay maganan, murya chan kasa cikeda shakkan abinda zatace tace “that’s not how to, lemme cook it for you p…..please” wani kalan wahalallan tsaki yaja ko kunyanta baijiba yace “banso” sanan yay slamming door din on her face batare dayama jira maitake shirin cewaba, kuka taji yazo mata wuya tadaure tahanashi fitowa tadade ahaka awajen sanan ahankali tajuya tawuce takoma dakinta zama tayi tana kallon handkerchief din tama rasa meke mata dadi, tunda take bata taba shakkan wani namiji ba sai wanan menene shi? Jibeta fa tanada kyau babu namiji da bazata iya daukemai hankali ba shi waye, enough of

all this, tashi tayi fuu tai kofan tabude tafice sanan direct tai dakinshi ta danna door bell baa wani dauki lokaci ba wanan karan tabude kofan koyana expecting wani ne oho, churus ya tsaya ganin yarinyar dazu, wani irin faduwa gabanta yayi ganinshi dagashi sai dogon wando na Jean da Riga a hannunshi dabai Riga yasaba yanada wani irin broad chest ga cikakken shoulder parts garai, kasa magana tayi saiwani kalan kallon kirjinshi datake lips dinta na rawa tana kallon dark aroelas dinshi, ahankali tace "I…..l….ove……you…..Z….Zayn" Tundaga sama har kasa yake kalleta sanan yace "ke kikama kanki" wanan Karan wani slamming kofan yayi on her face saida yataba goshinta ahankali tajuya kaman an kashe mata yaran ciki tawuce side nata ta zauna dirshan akasa, tana zaune awajen taji fitowanshi yafice, kiri kiri kasa zuwa class din datake dashi tayi sabida yanda komi baya mata dadi.

💫 ALKAWARIN ZUCIYA 💫

PROMISE OF THE HEART 💔

✍🏻M SHAKUR

3️⃣

~Nigeria~

Wata babbar mace ce doguwa chocolate skin tsaye cikin wani lafiyayyen hadadden kitchen ginin zamani, tana sanye dawata doguwan rigan Atampa mai kyan bala'i ga kallabi daure akanta da kana gani kasan daura dankwalin kawai tayi amman hakan baihana kwantaccen black gashinta dake gauraye da farare lekowa ba, tana tsaye agaban wani hadadden babban gas a kitchen tanama wata yar aiki dake juya basmati rice a tukunya dawani wood spoon magana sukaji wata zazzakan murya dake ratsa zuciya na y'a mace ta kwala ma matar uban kira. "Mama nadawo, nakawo miki wasu kawayena ki gansu" wani irin kwashewa da dariya yar aikin dake juya abinci a tukunya tayi takalli Matar da aka kira da Mama datai tsaye kawai tama rasa ta cewa tace "Hajiya wlh tun ina iya kirga yawan kawayen Khairy harna bace a kirgan" kwafa kawai Matar da aka kira da Mama tayi tace "karasa juya abincin sai ki kwashe a warmer Ladid….." bata idasa maganan ba aka kara rangadamata kira da wanan zakakkiyar muryan kaman ana busa sarewa. "Mamaaaa kina ina zoki gansu" dafa goshinta Matar tayi cikeda takaici tace "Allah nagode maka dakabani wanan yarinya, ina ganin Ummulkhairy ce zata bani hawan jini aduniyan nan" tai maganan tana fitadaga kitchen din ta hanyar bude kofa tafice, tana fitowa dining tai kicibus da yammata kusan su tara a zazzaune kan lafiyayyun kujerun falon suna maganganu suna hira suna kallon lafiyayyen hadaden falon dayaji Cubana furnitures, ganin Matar da kallo daya suka mata suka gane itace mahaifiyar Khairy yasa duk suka zubo daga kan kujerun cikeda girmamawa duk suka gaidata. "Mama ina yini, Mama barka da rana, Mama ina gajiya" lafiyayyen murmushi ta sakin musu tana karasowa tsakiyan falon tana bindi

da kallo daidai tace “Masha Allah sassannunku da zuwa yammata yakaratu”? Kafin subata amsa wata kyakkyawan budurwa yarinya chocolate skin color, yar doguwa bachan sosai ba dabazata wuce 20yrs, skin dinta nawani kalan glowing fuskanta babu ko kuraje guda, tanada dan dogon hanci yet kuma dan karami dan diss afuskanta but fitacce, tanada manya manyan pure white eyes, idanunta are very big sunada wani kalan adorable spherical shape that is just damn gorgeous, dan kana kallonta the first thing dazasu fara daukan maka hankali a fuskanta are her big white eyes, ga eyelash dinta dogaye bakake cikakku, hakama gashin giranta, tanada goshi wanda kusan yarabu biyu ne rabi duk gashi ne dayake nan baki sidik sun kwanta daya karama fuskanta wani kalan kyau dan zaka dauka buzuwa ce sai dayan rabin kuma fatarta ne dayataho har gira, tana sanye da dogon rigan atampa itama da dan kwalinta akanta, tawani buga uban ihu da saida falon ya amsa gabadaya. “Mamaaaa” yanda ta kwala mata uban kiran nan yasa  mahaifiyar nata tadago da kanta tareda juyowa ta zuba mata idanuwanta kurii irin na jama’a yaya zanyi da wanan yarinyar ne? Wani irin washe baki Khairy tayi cute saitin white teeth dinta suka bayyana tashiga saukowa daga stairs din dagudu kaman ba ita Mamar kema kallon zaki ganeba kawai tawani irin fada jikin Maman nata tana ihu sosai tana rawa ta kankame Maman kamkam. “Wayyooo Mama wlh nai missing naki, inata nemanki nadauka kin fita ne har hankalina yatashi ashe kina kitchen, Mama tun safe yau banganki ba awa nawa yanzu bansaki a idona ba karfe biyar fa, nai kewanki Maman mu, Mamana, I miss you Mommy Ummulkhaiyr” tai maganan tana kara kankamet Mama cikeda tsananin murna, dudda yanda Mama ke mugun kule da ita saida tai murmushi har cikin ranta duk cikin yaranta babu wanda ke sonta kaman yanda Khairy ke sonta, idan Khairy tadawo gida batanan wani zubin har zazzabi takeyi, Son da Khairy ke mata dabanne, gabaki dayan kawayenta baki suka sake suna kallon Khairy yanda ta kankame mamanta cikeda murna tana rawa kaman wata yar karaman yarinya, murmushi kawai Maman takeyi ganin yanda kawayen ke kallon Khairy sabida wayan nan wasu new set ne basu saba ganin haukanta agidaba yasa Mama tace “ke dalla cikani kije kitchen kitaya Ladidi ku kwaso abinci kiyi serving friends naki kuci” sakin Mama tayi ahankali tana murmushi dake bala’in kara mata kyau tana kallon Mama tace “tom Mama” sanan tawuce kitchen da ihunta ta shiga kitchen din. “Ladi kwas kwas!” Tsabagen yanda Ladidi tafirgita batasan lokacin data saki cokali data rike a hannunta kasa ba, kwashewa da dariya Khairy tayi ganin yanda Ladidi tafirgita, Ladidi ta watsa mata harara tana dafa kirjinta da hannu jin yanda yake  bugawa tace “aniyarki tabiki Khairy bani zaki sawa bugawan zuciya ba wlh” dariya Khairy tayi tadauki spoon tazo kusa da ita tana kallon tukunyar tana murmushi tace “uhmm smells good, let’s have a taste” abincin tadeba takai baki tana lumshe ido, harara Ladidi tabita dashi tana kallon long full lushy eyelash dinta dazakaji kaman ka cire kasama naka sabida kyau, dan murmushi tayi tace “yayi dadi Khairy? Kinga nasa coconut milk dakikace nadinga sawa” bude idanu Khairy tayi ta kalleta sanan ta yatsine fuska tace “yayi dadi ba laifi amman ba kaman nawa ba” batarai Ladidi tayi hakan yasa Khairy tafashe da dariya tace “ki zubamana nida kawayena kizo ku gaisa” hararanta Ladidi tayi tace “Malama ki tsaya ki dauki abincinku ki kaimusu ba inda zani nagaji da gaisawa da kawayenki, nibansan ko kamfani gareki na kawaye ba” turobaki Khairy tayi tace “bakinciki kikemin kinga inada kawaye masu sona ke bakida kawa ko daya” dasauri Ladidi tanuna kanta tace “ni Khairy bakin ciki ana zaune lafiya, kawayenki sunfi dari, ni idan Allah yabani kawaye ko sama da biyu ne bansan yanda zanyi dasu ba” hararanta Khairy tayi tadauki Baban tray da Ladidi tajera musu different abinci akai a different plate guda 5 tafita dasu taje

takai musu sanan tadawo ladidi na kallonta tace “yanaga kin dawo” akufule tace “su tara ne plus ni goma, kuma is just 5 plate of food nafita dashi” kasa magana Ladidi tayi kawai tashiga zuba wasu sababbi tass abincin yakare Ladidi tace “yayyinki suka dawo maizasuci” “oho” ta amsata akufule tafice abinta takaimusu abinci suka shiga ci suna hira shaaaa kakeji sun cika falon da hayaniya kadauka biki ake kowani liyafa aka hada, lekosu Ladidi tayi daga kitchen kwafa tayi tace “yo wlh ban kara daura wani girkin barima kiga tafiyata zanyi, masu gida nakema aiki ba kawayenki ba, yarinya kowani kare da doki kawayenki ne, mijinki zai sha fama Khairy” tai maganan tana komawa ciki, hada yan kayanta tayi a handbag dinan sanan tabi takofar kitchen tafice abinta daman inhar tagama aikin yamma indai Hajiya na sama tafiyanta take saidai in tana kasa ne saitaje tamata sallama tawuce.

Sai wuraren 6 sanan kawayen nata suka fito bayan takaisu sama sunma Mama sallama har compound tarakosu inda sukai parking motocin su duk suka shishiga, daya daga cikinsu taleko bayan tama motarta benz key tace “wai Khairy yaushe zaki farajan mota kine eh? Gamu duk mu munaja ke kadaine kullum driver ke kawowa” kaman zatai kuka tace “ba su Mama bane da Baba wai tsoro suke su barni nafara tuki wai nacika rawan kai kumafa na iya wlh Paddy” dariya dukansu sukayi wacce ta kira da Paddy tace “ke da karfin hali zakisa su barki kifara tuki wlh daukan mota kawai zakiyi wataran ki fice, Babe magrib tayi bari muwuce see you tomorrow at school” hannu tadaga musu tace “see yah girls” gateman dinsu yabude musu gate suka fice motoci biyar daidai kuma motocin yayinta na shigowa gida na Baban su biyeda su, washe baki tayi tana tafi ahankali tana kallon motar Baban su dake shigowa last tace “oyoyo Baba” motan na parking tai wajen motan da gudu batare databi na yayyinta da kallo bama.

💫 ALKAWARIN ZUCIYA 💫

PROMISE OF THE HEART 💔

✍🏻M SHAKUR

4️⃣

Kafin ma Baba yabude kofa tasa hannu tabudemai kofan jikinta har rawa yake tanajin dadi. “Baba oyoyo, Baba sannu da zuwa” wani magidancin mutum ne babba sosai yana sanye da babban riga yanada gemu dayacika da furfura, ga kuma katon ciki irin na manya wayanda suka manyanta dinan, exactly idanunsu iri daya da ita manya saidai nashi daya soma kankancewa sabida tsufa, wani kalan kyayataccen murmushi yasakin mata, cikin kamilallen muryanshi irin na magidantan nan yace “yarinyar Babanta” yay maganan yanajan dan hancinta, murmushi tayi

sosai tace “sannu da zuwa Baba” fitowa daga motan yayi yace “to akwasomin kaya akai ciki” gyadamai kai tayi tace “to Baba” yawuce yana kallon yaranshi maza su uku da duk suke tsaye suna jiran fitowanshi, Manaf wanda yake Babba yanada 27yrs, sai Mu’az shima 27yrs twins ne shida Manaf saidai ba identical twins ba ko kadan ma basuyi kamaba idan baa gayamaka yan biyu bane bazama ka yardaba, Manaf na kama da Mama, Mu’az na kama da Baba, sai Maheer dakenan 24yrs, dukansu sun gama makaranta duk a company Baba suke aiki yanzu.

Gaida Mahaifin nasu sukayi cikeda girmamawa kana ganinsu kaga yaran dakeda tarbiya dakuma natsuwa. Cikin so da kauna ya amsasu yana tambayan kowa ya aiki sanan suka wuce masallaci, itakuma kayan Baba su files da wasu yan tarkace tafito dasu daga motan sanan tai cikin gida.

Sama tayi direct zuwa lafiyayyen hadadden falon Baba, ijiye kayan tayi sanan tajuyo tabude kofa ahankali, ganin Mama tsaye abakin kofan kaman ita take jira daman yasa takarasa fitowa tareda maida kofan tana rufewa tana kallon fuskan Mama dake kallonta tana murmushi, harara Mama ta watsa mata tace “ba murmushi nace kimin ba, quietly go to that kitchen kidafa sabon abinci wanda za’aci agidan nan this night tunda wanda aka dafa dake da kawayenki kun cinyeshi tatas” dan turobaki tayi dan wlh tagaji ahankali kaman zata rushe da kuka tace “Mama maisa Ladidi bata dafa wani ba wlh nagaji school fa naje” cikin fushi sosai Mama tace “are you stupid Umma? Inba so kike na makeki ba kiwuce yanzun nan kafin raina yabaci kije ki daura abincin daza’aci this night, I am talking to you kina gayamin Ladidi tadafa, kin zaci sabida ke nadauki Ladidi aiki kokin dauka jakace ita batasan ciwon kanta ba dazata zake tai girkin gida keda kawayenki kuzo kutasa abincin agaba ku cinye tas, yanzu ina gayamiki kije ki daura wani kina neman kawomin gabli da ba’adi, to the kitchen my friend!” Mama tadaka mata tsawa kaman zata kurma ihu tawuce hawaye sun cika idanunta tass tai kasa, harara Mama tabita dashi sanan takada kai kawai tawuce tashiga dakinta.

Kitchen din tashiga tamaida kofan da mugun karfi tarufe kaman zata Balla kofan sanan ta jingina da kofan tana maida numfashi takai kusan 5min sanan tawuce ta kwaso kayayyaki tashiga shirin hada girki.

Saida akai Isha’i sanan Baba da su Manaf suka shigo gida, afalo suka tarda Mama zaune gaidata duk sukayi, Mama ta gaida mijin nata zama duk sukayi, Maheer yace “Mama me aka dafa yunwa nakeji” ahankali Mama tace “Khairy na kitchen tana girki, itada kawayenta suka cinye duka abincin da aka dafa tass shine yanzu dannace taje tadafa wani abincin take kumbure kumbure” dan murmushi Baba yayi yana duba wayanshi ganin yanada miss call, cikeda kufulewa Maheer yace “wlh Mama Allah zan zane yarinyar nan, duk randa takawo kuchakun kawayenta tashiga kitchen tamusu girki da kanta ba abincin muba” cikin fushi shima Mu’az yace “ni I don’t even know wani kalan brain Khairy keda shi, ni tunda nake bantaba ganin wacce takai Khairy yawan kawaye ba, kawayenta sunfi dari biyu, tamaida mana da gida nanne majallisar kawayenta ai gobe Saturday Allah sa takawo mana wata gidan nan wlh daga ita har kawar saina kakkaryasu” Baba daduk ke jinsu yana taba wayanshi wayan ya ijiye yakalli Mama

yana murmushi sanan yakalli su Maheer yace “ku kyale yarinyar nan she’s just a small girl, idan making friends makes her happy so be it, abincin gidan banike siyaba taita kawo kawayenta sunaci is no big deal, and you wife” yajuyo yakalli Mama yace “idan abincin gida da kawayenta keciki ki kara yawan abinci since kinsan yarki mai mutane ce, ta yanda zasuzo suci su koshi sanan muma muzo muci okay” tabe baki Mama tayi tace “daman babu wanda ke bata yarinyar nan saikai kacigaba” Mama tai maganan da fushi dan murmushi Manaf da tuntuni baice komiba yayi ganin yanda ran Mama yabaci yace “Mama kudena making issue out of this small thing please bagashi yanzu tana kitchen tana dafa mana wani ba, is just friends ta tara bawai wani bad hali ko dabi’a takeyi wanda yaran yanzu sukeyi ba Mama, please ku kyaleta, she’s still a small girl, inda ace bata gama secondary school dawuri ba da har yanzu bamata shiga university ba ballema tazo hartana final year, ku barta please Mama ahankali zata gyara” murmushi sosai Baba yayi yanajin maganan da Manaf keyi, Manaf nada dabi’unshi sak, ga hakuri ga iya tafiyar da gida gashi da halin manyanta halin Baba, amman Mu’az da Maheer jin kansu suke kaman sa’onnin Ummul Khairy. Baki Mama tabude zatai magana aka bude kofan kitchen din aka fito Khairy ce tadauko wani hadaden warmer, ko kallonsu batayi ba sai uban turo baki take tawuce zatakai warmer dinning Baba yace “zo kawo kulan nan Umma anan falo zamuci” ahankali tajuyo tazo Mu’az da Maheer sai uban ballamata harara suke tana karasowa ta ijiye kulan Baba na kallonta yace “yauwa sannu da aiki Yanmata na” Maheer dake kallonta yace “yi sauri kije ki kawomin plate dina da fork” dasauri ta kalleshi da manya manyan idanunta harara ta watsamai wani irin mikewa tsaye yayi kaman zaiyo kanta dasauri tai baya tareda dan sakin ihu. “Wayyo Ya Manaf kaganshi ko” hararanshi Manaf yayi batare dayay magana ba hakan yasa Maheer yakoma yazauna yana kwafa, Manaf yakalleta yace “go and bring the plate and serve us” gyadamai kai tayi tajuya tana turo baki daga Baba har Mama suka bitada kallo, bata wani dade ba tafito dauke dawani babban tray da plates spoons, bottle water da drinks ke kai sanan takawo tsakiyan falon, sanan tabude kulan wani kamshi ne yadaki hancinsu tadafa wani lafiyayyen taliya da nama, zuzzubama kowa tayi sanan ta tashi, Baba yace “ina zaki zauna kici naki” ahankali tace “nakoshi naci shinkafa dazu, wanka zanje nayi Baba nagaji” “jikiyi yarinyar kirki” wucewa tayi sama sukuma sukahau ci, saida Maheer yajuya ganin hartama shiga dakinta yasa yajuyo yace “at least she’s good in one good aspect, wato girki” murmushi Baba yayi yakalli Mama yace “akwai wacce zata zauna da Wife bata iya girki ba ballema yarta” murmushi kawai Mama tayi batacemai komiba, saida suka gamacin abincin tsaf sanan Maheer ya kwashe komi yakai kitchen kafin su tashi suma iyayensu sallama suka wuce side dinsu.

Tashi Baba yayi yana kallon Mama datai shiru yace “please kidena sa zancen shirmen Khairy aranki, is just like what Manaf said at least friends kawai ta tara bawani mugun hali ba” dan ijiyan zuciya ta sauke sanan ahankali tace “Alhaji still yawan kawaye basu da amfani wlh” ahankali Baba yace “I promise duk randa nai sensing wani bad behavior kokuma wani abu nida kaina zan rabata dasu, please this matter of her friends shouldn’t be an issue again ok” Ahankali Mama tace “ai shikenan  dama kaine ke bata Umma ai” Mama tai maganan tai gaba abinta binta yay abaya yace “wifeyyy common” bata biyemishi ba tabude kofar dakinta ta shige, murmushi yayi kawai aranshi yace “I will handle u later” sanan yay hanyar dakin Khairy, knocking yayi ahankali tareda kiran sunanta. “Umma” jin shiru yasa ahankali yabude kofan

dakin, dakine nai kyau dakana gani kasan dakin Yar gata ne anyimai Fenti pink dakuma design na flowers everywhere, tana kwance kan lafiyayyen gadonta mai kyau tana sanye da dogon gown na bacci tana bacci hankali kwance ga dakin uban sanyin AC tachure alamun sanyi takeji, karasowa gaban gadon yayi yace “Umma Umma, mamar ki dake fada ita batasan rashin jin maganan ta kika daukoba” yay maganan yanajan bargon gadon yarufa mata sanan yadau remote don AC yarage AC sosai kafin ahankali yajuya ya kashe wuta sanan yarufe mata kofan yawuce dakin matarshi!!!!

💫 PROMISE OF THE HEART 💫

ALKAWARIN ZUCIYA 💔

✍🏻M SHAKUR

5️⃣

Da asuba kafin Baba yawuce masallaci yashigo yatadata wanda hakan yakeyi kullum.
Da farinciki ta tashi yau sosai kaman ba itane ta kwana da fushi jiyaba, murna take sosai sabida yau zataje bikin kawarta Zainab.

Saida tai salla tai karatu sanan ta gyara dakinta tsaf tafito kasa ta sauka a kitchen ta tarda Mama tsaye zata fara aiki dawani irin gudu taje ta rungume Mama. “Mama good morning” murmushi Mama tasakeyi this is another aspect na halin Umma datakeso ko kadan batada riko, tureta Mama tayi tace “waike karyani kikeso kiyi” dariya tayi tace “Mama dadi nakeji yau bikin Zainab Kawata, Beaty wacce nai ankon ta kin tuna”? Baki Mama ta tabe tace “ina zan tuna wata Besty Bestotin kin sunfi dari, keda kullum cikin bikin kawayenki ake, idan babanki ya shigo kije ki tambayeshi izini baruwana da zuwa bikinki, bani tukunya nidai kiga” dasauri tadaukoma Mama tukunyar nan suka shiga hada breakfast tanama Mama surutu wuraren 8 suka gama komi suka jera a falo daidai nan su Baba suka shigo gidan duka zama sukai a falo suka shiga kari sai bayan an gama ta kwashe komi takai kitchen sanan tadawo da saurinta tazauna kusa da Baba, fuskanta kadai yagayamai dawani abu hakan yasa yace “Ya akayi Khairiyya?” Murmushi tayi tace “Baba yau bikin Zainab kawata shine nakeso nagayamaka” idanu Baba yazuba mata yace “amman kinsan yau yakamata kije gidan Baffan kiko” gyadamai kai tayi dasauri ahankali tace “Baba gobe zanje gidan tunda yau inada biki please naje Baba”? shiru yayi sai chan yace “ok kije, but by 4 kidawo gidan nan ban yarda kije kai Amarya ba” murmushi tayi tace “Baba ai daman bazanje ba itada za’akai Kano, kumama ana daura aure wai zaa tafida ita kaga kenan kafin 4 nadawo ma” jinjina kai Baba yayi yace “duk kincikani da surutu, okay to adawo lpy, ki kama kanki banson kula maza okay” dasauri tace “to Baba, bari naje na shirya to”

tai maganan tana tashi tai sama, tashi Manaf yayi yace “bari naje na kwanta Mama” binshi Mama tai da kallo yawuce yafita shikuma Maheer da Mu’az Kwallo suka kunna a falon suna kallo abinsu, Baba kuma na duba wasu files dayasa Mama tadaukomai daga dakinshi.

Wanka tasakeyi sanan tashirya cikin wani hadaden ashobe, skyblue, dogon riga aka mata daya kamata daidai ita ya bala’in mata kyau, yabi jikinta sosai, zama tayi gaban madubi tana kallon kanta, dan tsaki tayi takai hannunta tana shafa siman rigan da akabi da net da kana iya hango tudun saman boobs dinta ahankali tace “I hate style like this dake nuna jikina, I will use gyalena narufe Mtsww” tasake jan tsaki sanan ta zauna tai wani lafiyayyen dauri dazaka dauka make up artist ce tayi, kwalli ta zizara sanan tadau wani lipgloss tasaka dayasa lips dinta shining pink din jiki yafito sosai dazaka dauka janbaki pink tasaka, wayanta dake gaban mirror kiran samsung note 22 ta dauka, ganin 10miss calls yasa tace “OMG guys gani nan zuwa kunata kirana” ganin battery ta yay ja yana nuna 10% left yasa takara jan tsaki tace “ohhh namanta bansa chaji ba” arayuwanta babu abinda take kiwuyan sawa irin chajin waya wani zubin sai wayan ya mutu russ ne shine zata dauka ma tasa a chaji, jefa wayan tayi a shinning handbag dinta dake ijiye kan mirror sanan  tajawo wani hill na dolce gabana tasaka sanan tamike tsaye, dan karamin gyalenta tadauka ta warware sanan ta yafashi ta gaba tsaf yarufe mata kirji sanan tadauki turarukanta ta feffesa kafin ta maida komi yanda yake tafito lokacin 12:48PM.

Saukowa tashiga yi daga Mama sai Maheer afalon yana kallon wrestling shima Mu’az yatafi ya kwanta, kamshin dayaji yasa yajuyo ganin Khairy yasa yasaki baki yace “ke kece amaryan Wanan kwalliya haka, Wanan ko ranan aurenki banjin zaki irin wanan kyan ba” hararanshi tayi takalli Mama dake binta da kallo tace “Mama kin ganshi ko” hararan Maheer Mama tayi hakan yasa yay shiru itakuma takaraso wajen Mama tace “Mama zan tafi ina Baba?” Ahankali Mama tace “Ya kwanta, ga kudi ya ijiye miki” tanuna mata bandir na yan 200 dasauri tadauka tana murmushi tace “Allah sarki Babana he’s the best, Mama natafi” tai maganan tana wucewa zatai kofa, Mama tace “ke” dasauri tajuyo takalli Mama dake kallonta, Mama tace “kindaiji abinda Baban ki yace ko, 4 tamiki agida Umma, kuma ki kama kanki, baruwanki da maza ko abokan ango, saura kuma naji kin wuce wani gantalin daban, wlh kika saba any of them bikin dazakije na karshe kenan ban kara barinki fita” dasauri tace “Mama I promise, nida keda bukukuwa I will not jeopardize that Mama, bye, Mama zan kawo miki alkaki” hararanta Mama tayi tace “banso, wuce Direba na jiranki” kofa tabude tafice, Already Adamu Direba harya shiga cikin motan ita kawai yake jira, wata lafiyayyen bakar Benz tabude baya tashiga sanan tace “gidansu Zainab zamu Adamu” “to Hajiya” yay maganan yana tada motan yaja, saida sukahau kan titi sanan taciro wayanta dake nuna 9% yanzu sabida uban kiran dasuke mata, kafin tama danna wayan wani kira yashigo da suna Zainab, daukan kiran tayi tana dariya tace “Amarya kinsha kamshi da turare, kuma wani gida ne gani ahanya” shiru tayi sai chan tace “Okk” sanan tace “Adamu suna gidansu Amal wai” ahankali tace “to” dan babu gidan wata kawarta dabaisani ba, tafiya kai nisa sukayi sanan suka shigo wani hadadden estate daya cika da mutane kana gani kAsan biki ake wani Layi daban ya shiga sanan yay parking agaban wani hadadden gida, murmushi tayi tace

“yauwa, Adamu bani key motan narike” dasauri yajuyo ya kalleta, ganin kaman yanaso yaganota yasa tace “zan taimaka musu dashine, ana kwaso one or two things dazamuyi amfani dashi, idan zan dawo zan kiraka saikazo mutafi” tai maganan tana mikamai hAnnu, ahankali yazari key motan yabata karba tayi tace “yauwa katafi to dan sai yamma zan kiraka” tai maganan tana fitowa daga motan shima fitowa yayi sanan tarufe motan ta danna lock tawuce cikin gidan abinta shikuma yawuce yatafi zuwa bakin titi ya tsaye abin hawa yahau.

Tun kafin tashiga gidan takejin tashin kida, murmushi tayi ta shiga gidan an gyara anyi decorating ga yammatan Amarya sai rawa suke suna hangota aka wani hau ihu. “Khairy, Khairy ta iso, ke join us” wani irin murmushi tayi kaman abinda take jira kenan dasauri tai dance floor din, DJ yasakan musu wani mad song rawa sukahau yi suna ihu suna hotuna idan kaga Khairy zaka dauka taje dancing school ne,  suna haka saiga Amarya tafito wani mahaukacin ihu sukasa aiko tashigo itama sukahau rawa kaman mahaukata, Amaryan ta rungume Khairy tana mata magana a kunne, hakan yasa taciro wayanta tana video ganin wayan na nuna mata 1% yasa tai tsaki ta maida bag sanan taciro kudi tana ihu yara sai kallonsu suke taba manna ma amaryan. It was fun she love her friends and she loves wedding har buri takeci irin na shagulgulan da zaayi idan bikinta yatashi.

💫 PROMISE OF THE HEART 💫

ALKAWARIN ZUCIYA 💔

✍🏻M SHAKUR

6️⃣

Wajajen 3 aka wuce da Amarya Kano, ita kanta Khairy saida tadanyi kuka cus Besty tabata tausayi, bayan an wuce da ita  tama Maman su sallama tawuce dan zuwa chan gidan dasukai party inda motanta yake a pake, ahankali take tafiya ta bala’in gaji sabida rawan dasuka sha, ita kadai kemagana tace “yanzu inda Baba yabarni da hardani za’akai Zainab Kano, gashi akwai more event a Kano” dan murmushi tayi ita kadai tace “Allah kaimu bikina wlh 2 weeks zaayi ana event hmm” dan murmushi tasakeyi tace “nidako saurayi banda shine nake planning biki na” ahankali ita kadai tace “saikace wata mara farin jini, inada samari dayawa but duk mazan Nile ne, basu hadu ba gasu yan rainin wayau saisa i don’t even talk to them” tai maganan tana murguda baki daidai lokacin ta iso wajen motan, ahankali tace “I want to marry hadadden namiji, classic , handsome, miji dat will make mata jealous of my catch” tsayawa chak tayi takalli motan gabanta yadan fadi, saikuma chan tace “don’t be scared Khairy you have to show Baba u can drive sabida yabarki kidinga jan motarki” tana maganan tabude gaban motan tashiga

tazauna tana sauke ajiyan zuciya sanan tamaida kofar motan tarufe kafin ahankali tace “Ohhkay let’s see” sitbelt tasaka still gabanta nafaduwa bata taba tuki bafa kawai tasha ganin yanda akeyi sanan Maheer idan tashiga mota dashi yana nuna mata yace “kihaka kihaka this and that” ahankali tace “Bismillahir Rahmanir Raheem” sanan ahankali takunna motar gently gabanta na dum dum tashiga yin reverse kadan kadan kana gani kasan wacce bata iya tuki bane acikin motan nan sanan ahankali taja motan tana tafiya ahankali wani irin murmushi tayi cikeda jin dadi tace “see ba gashi nan na iya ba ina tuki perfectly like a pro” Ahankali takejan motan feeling a bit too sad sabida su Mama basu Bari takai Zainab ba ahaka hartakai gate din estate din tasa kan motarta tafice tana kalle kallen main road din gabanta na faduwa, ganin motoci kowa na zuba gudu na wucewa yasa sabida irin karfin hali irin nata tasa motan ta shige cikin titin sanan tafara gudu Adan hankali, ganin tana gudu kan titi smooth babu wani tangarda yasa tai murmushi tace “wlh na iya” sanan tawani kara uban gudu tana murmushi, ko kadan bata lura dawani keke napep dake bullowa daga wani layi da mahaukacin gudu ba kawai danno kan keken shi yayi batare dayama kalli titin ba rawa jikinta ya dauka dudda da akwai tazara kadan tsakaninta dashi amman sabida yanda jikinta ke rawa tanason takara kara rage gudun datake kawai ta danna sauri before the blink of an eye jikake kwarap!! Motanta yadaki bayan keken da bala’in karfi tacigaba da tura keken gaba jikinta nawani irin rawa tama kasa taka burki. “Innalillahi wa innailaihi raji’un” tafadi arude kaman walkiya sanan ta ci wani mahaukacin burki dayasa dabata saka sit belt ba data buga kanta a siteri, ganin motan ya tsaya chak yasa dawani irin sauri ta murza key ta kashe motan gabaki daya tana wani irin sauke ijiyan zuciya da sauri dasauri tana kallon keken dake manne da gaban motanta zufa nawani irin keto mata daga goshi takasa ko motsi still in shock.

Dawani kalan sauri direban keke napep din yafito yaci Kwalli a idanunshi yana sanye da Yar singileta daya koma brown tsabagen datti da jeans passengers shi maza biyu suma dake baya duk suka fito yana kallon yanda bayan keken shi yay condemn, sauran motoci sukuma sunata wucewa abinsu tunda dai Allah yakawo sauki hatsari ne da babu wanda yaji ciwo to su karata chan anata wucewa ta gefensu.

Saida mai keken yagama duba kekenshi tass yakalli yanda duka kwan fitilan dake bayan keken suka faffashe sun fadi akasa sanan ahankali yadaga kanshi yakalli glass din gaban motan ranshi amugun bace yana kallon Umma dahar lokacin takasa motsi sai numfashi datake maidawa ita kadai tasan yanda cikin jikinta ke rawa, kafinma mai keken yay magana daya daga cikin passenger yace “durun uwanchan amman matar nan yar bala’in rainin wayau ce Auwal, muna tuki abinmu lami lafiya tazo ta dakan mana keke tamana Wanan uban asaran sanan ta zauna hankali kwance a motanta batama fitoba balle ta duba asaran datayi mana ba”……..

Wani hadadden hilux baka dakana ganinta zaka gane da security personnel ne ke gudu akan

titin, ganin titin is congested go slow yasa yashiga  rage gudu yana kalle kalle, wani kyakkyawan saurayi ne ke tukin motar yana sanye da kayan yan sanda, daya bala'in haska farin fatan jikinshi, ahankali yake tuki yanabin titin da kallon ganin yanda motoci suka cika hanya tam ga daga chan gefe gefen titi haka  ya hango accident akayi tsakanin keke da wata mota dayaba iya ganin cikin motan cus tinted glass ne, ga masu keken sun fito suna duba keken su uku kana ganin yaran kasan irin rascals dinan ne, dan tsaki yayi ahankali sanan ya gangara gefe yay parking motan shi, murya chan kasa tace "I hate this job Dad!" sanan ya kashe motan yafito yanadan yatsine fuska tareda maida kofan motan nashi yarufe..…..

Cikin wani kalan bakan zuciya mai keken da aka kira da Auwal da idanunshi sukai jajir danshi kadai yasan wuyan dayasha kafin yasami keken nan mezaicema mutanen dasuka bashi haya, cikin fushi ya nuna Umma dake kallonsu kuri ta glass din gaban motan da yatsa, irin warning dinan yama kasa magana tsabagen zuciya, hakan yasa ahankali Umma takai hannunta ta zare sitbelt sanan tabude kofan motan tafito ahankali jikinta na rawa tana kallon gaban motanta itama dayama bare yay kacha kacha saikuma bayan keken dashi ma ya baci wutan duk ya mutu sun faffashe sun fadi, sanan takaraso ta inda suke tsaye nesa dasu zata bude baki tai magana Auwal mai keken ya tare mata numfashi yace "ke dan ubanki dame kike takama agarin nan dazaki min condem din adaidaita sanan ki zauna cikin motarki batare dakinma fito kin duba barnan dakikayi ba balle kibani hakuri.." sosai kirjinta kewani kalan dukan uku uku hakuri tai niyyan tabashi amman yanda yazagi Babanta yasa taji ranta yabaci, cikin fushi tana kallonshi itama right in the eye tace "karka karayin kuskuren zagin ubana again inba hakaba wlh saina wanka maka mari, besides ma kai agidanku ba'a koyamaka kaduba hanya kafin kashigo ciki ba eh"? Cikeda wata kalan bakar zuciya Auwal yana kallonta da idanunshi da ita kanta taga bala'in dake cikinsu yace "ni kike gayama magana?" Dakewa tayi dudda kirjinta kaman zai tsage tace "ai kai kafara, dama ance idan Yaro bai koyi tarbiya agida ba zai koya a titi, dan haka from today karka kara ganin mutum kai kuskuren zaginshi ko iyayenshi" kafin ma Auwal dake dunkule hannu yay magana passenger sukace "ke wai kinada hankali kuwa kin bugemai keke kinmai asara bazaki bada hakuri ba" wani mugun kallo tamusu tace "kune marasa hankali bani ba, kuma hakurin bazan bayarba kuyi yanda zakuyi" tai maganan zata juya jitayi an wani irin fizgo bayan riganta fut tadawo baya hartana turgeda kafa sabida heel din data saka, wani irin bari jikinta yadauka tana kallon Auwal daya fizgota ganin yadaga hannu zai kaimata mari yasa tawani irin kwala ihu tareda kai hannayenta biyun tana kare fuskanta, shiru taji batare dataji saukan Marin ba akan fuskanta, hakan yasa ahankali kaman wacce tai sata ta shiga janye hannunta daga kan fuskanta tana nishi sama sama sanan tabude idanunta da kyau tana kallon gabanta inda su Auwal mai keken suke, wani mutum tagani dogo fari kal sanye da kayan yan sanda yasha gabanta yana rikeda hannun Auwal daya kawomata mari ya murde, dudda bataga fuskan mutumin ba dan yabata baya but she could see yanda bayan shi keda fadi, gawani kalan bakin suma dake kanshi sun kwanta suna kyalli sosai zuwa shi wajen yasa wajen yadauki kamshin dayakeyi. Daga Auwal har passengers din duka tsurewa sukayi suna mutumin, cikin wata kalan kakkausan murya yace "how dare you raised your hand zaka daki mace akan titi, are u mad!" Yadakamai tsawa yana murde
hannunshi da kyau ihu Auwal yayi jin azaba yace "officer dan Allah kayakuri bazan karaba, wlh bugemin mota tayi opisa" cikin muryan nan nashi nabawasa yace "and u dare to lift your hand

up zaka daketa, cause she is a woman, and she is helpless, alone! Inda kanwar kace fa? U deserve to sleep in jail dukan ku the three of you" sosai suka shiga bashi hakuri, tun tana kallonsu tanajin mesuke fadi har taji kanta nawani irin juyawa kaman tanajin jiri, bugawan da kirjinta keyi yay multiplying da kusan dari hakan yasa gently tajuya tana daura hannayenta akan kirjinta tana kokarin ta saita numfashinta dake mata wuyan kamawa tana kokarin tafiya kawai tafiyan taji ya gagareta wani irin zubewa tayi jikin motan, Karan faduwanta da bugewa da motan datayi yasa dawani irin sauri dagashi harsu suka kallo inda take, ganin yanda take nishi tana beating chest nata tana kokarin numfashi at the same time tana kokarin tashi tsaye yasa dawani irin sauri yasaki Auwal yay inda take.

💫 ALKAWARIN ZUCIYA 💫

✍🏻M SHAKUR

7️⃣

Ganin Officer yasaki Auwal yay wurin yarinya datake abu kaman mai aljanu yasa suka juya da gudu suka shiga cikin keken su suka ja suka bace atitin saurama kadan sukara wani hatsarin Allah ya kiyaye.
Ahankali ya tsugunna agabanta yana kallonta from head to toe, this is the first time yake kallon fuskanta ganin yanda take fitarda numfashi da kyar yasa yashiga bin jikinta da kallo kota bugene koko tai sustaining any internal injury ne,or something else but babu any sign ajikinta, ahankali yasake maida idanunshi kan fuskarta yana kallon yanda take breathing not knowing exactly what to do, da kyar ta iya bude idanunta tana nishi kaman zata mutu, dishi dishi take gani sosai but she could see mutum akanta yana kaman yana kokarin karantan wani abu, gently taga pink lips dinshi na motsi kaman magana yake mata amman batajin komi, tashi yayi da sauri ganin kaman something is stopping her from breathing maybe tanada blockage a airways dinta, bude gaban motan yayi ya cire jakanta dake wajen ya wurga kujeran mazaunin direba sanan yadawo inda take zaune akasa, ahankali yasa hannunshi yakamo kafadunta sanan gently yadagata yadauketa yakai ta gaban motan yasata aciki yamaida kofan yarufe sanan yazaga ta dayan bangaren direba da sauri daidai ana kiran sallan magrib yabude kofa yana kallon yanda take wani irin dambe da numfashinta da kyar ta iya bude idanunta ta kalli jakanta daya wurga mazaunin direba dayake kokarin daukewa zai zauna ganin haka yasa dasauri yadauki jakan yashigo motan tareda bude jakan cikin zafin nama yashiga ciro abubuwan ciki, kayan shafa, kudi turare wayanta sai daga dan lungun jakan yaga inhaler.

Yau dayake Monday sunada lectures 9:00 wuraren 8:00 tasauko ta sanya wata Dubai gown sky blue dayama skin nata bala'in, sai uban sheki fuskanta yake ka kalleta saika juyo kabata second look, yau flat shoe tasaka baki sanan tadauki black bag shima, tana tafiya tana duba jakanta taga ko tasaka komi dan lecturer su na safen nan shege ne ajinshi you must jot inba hakaba yakadaka waje yace "you are not ready for school" Tundaga stairs take kallon Mama dataga tana zaune dinning takife kanta a table which is not like normal Mama, dasauri takarasa wajen dinning din takai hannunta ta taba bayanta tace "Mama" dasauri Mama ta tashi zaune idanunta sunyi ja irin name mugun zazzabin nan kafinma tai magana Khairy tarigata tace "Mama bakida lafiya ne jikinki zafi" dan zaro idanu tayi takai hannunta tana taba jikinta tace "bawani zafi daga AC kika fito Niko dana gama da kitchen ba dole kiji jikina yay zafiba, zo zauna kiyi break kitafi school" kujeran kusada Mama tazauna ahankali tana kallon fuskanta dan bata yardaba, Mama ta tashi tareda daukan plate tace "kici masa sabida yarikeki" tai maganan tana zubamata sanan ta tura gabanta tace "Oya Oya eat" fara ci tayi tana kallon fuskan Mama data daure iya daurewa, ahankali ta hadiye masan bakinta tace "Mama nakawo miki paracetamol kisha kinga kar zazzabin ya kwantar dake" dan shiru Mama tayi tana kallonta ganin dukta damu yasa ahankali tace "to naji zansha amman dakaina zan dauka Nasha ke yanzu kici abinci kitafi school yi maza ina kallonki" murmushi tayi sosai har ranta tace "yauwa Mama, world best Mama, har hankalina yatashi, wlh Mama ko tari banso naji kinayi balle ciwo sai inji komi bayamin dadi" dan dariya Mama tayi tanaji kaman zatai kuka amman ta daure tace "Malama eat bance kitasani agaba da surutu ba, Ummulkhairy aku" dariya tayi bata kara cewa komibaharta cinye kafinma tai motsi Mama tamikamata ruwa a cup, kallon fuskan Mama tayi sanan tai wani kalan murmushin dadi tace "Mama ya akayi ki kasan ruwa zan dauka" bata kofin Mama tayi tace "sabida ni Maman kine, angayamiki just like that naci wanan sunan world best nabakin ki" wani kalan washe hakori Khairi tayi sanan ta shanye rawan ta tashi tazo kujeran Mama rungumeta tayi tabaya tace "Mama natafi, I love you kinji, Mama karki je ko'ina please, koma zaki fita ki jirani nadawo saina rakaki mutafi tare" murmushi Mama tayi tadaga hannunta tashafa kanta tace "naji, a dawo lpy, banda rashinji, banda kula maza Umma, banda rashin kunya" sakin Mama tayi batare data amsaba tafice daga falon da sauri ganin 8:30, Mama na zaune inda take tana kallonta ta window harta shiga mota mai gadi yabude gate driver yafice da ita.

Ajiyan zuciya tasauke ita kadai tasan metakeji ajikinta, jin tafiyan Baba datun bayan yay breakfast yatafi sama shiryawa dan yau ba aiki zashiba asibiti zaikaita yasa tadaga idanunta takalleshi, hada idanu sukayi dawani kalan sauri ya shiga saukowa daga stairs din yace "wife,

ur……Han…..hancinki" yay maganan yana karasowa gabanta ganin jini na gangarowa daga hancinta, dasauri tace "hanci na" takai hannunta ta taba jin abu na gangarowa kafin tadawo da hannun gabanta ganin jini yasa tace "laaa banma saniba" cikeda karfin hali tamike tsaye wani irin mahaukacin jiri yadibeta tai baya dawani irin sauri Baba yatarota tafado jikinshi a sume, daidai lokacin Manaf da Mu'az na shigowa falon cikin shirin zuwa office, ganin Mahaifiyarsu yasa dasauri sukai wajen kafin ma suyi magana Bana yace "Manaf daukomin mayafinta afalo mutafi asibiti, Mu'az get the car" dasauri Mu'az haryana bigewa da centre table yafice waje shikuma Manaf yay sama, har gaban flat din Mu'az yakawo motan sanan yadawo ciki atare dukansu suka dauki Mama sukai mota da ita bata Baba yashiga da ita, Mu'az da Manaf suka shiga gaba sanan suka fita gida.

Wani Babban private hospital sukaje, suna shiga aka karbe Mama sanan akasasu tsayawa awaje, zama Baba yayi da kusan yamafi yaran nashi damuwa, ahankali su Manaf suka zazzauna kusada shi babu iyacema wani kala idanunsu sunyi jajir, suna zaune awajen na kusan 2hrs sanan saiga Dr wanda yake abokin Baba yafito, Baba dagashi harsu Manaf na ganinshi duk suka tashi, kallonsu Dr yayi sanan yace "Alhaji follow me" binshi Baba yayi yay tafiya kusan biyu sanan yajuyo yakalli su Manaf dasukai zuru zuru yace "let's go" dasauri suka biyoshi abaya har zuwa office na Dr, zama Dr yayi sanan yanunama Baba sit ya zauna sukuma su Manaf duk suka taaitsaya kowa kallon Dr yake with hope koma yayane abasu goodnews, lumshe ido yayi ahankali sanan yabude yace "Alhaji ayanda kuke kallona dagaku har yaranka I wish zan iya gayamuku abinda nasan har cikin ranku shi kukeso kuji, I am sorry I don't have that sai akasin haka, condition din matarka has become worse da ayanzu riketa a asibiti yama kamata muyi muna bata yan taimakon dazamu i……" kasa jiranshi Baba yayi yakarasa sabida yasan menene zai fadi, cikin wata kalan tsinkakkiyar murya dake cikeda sanyi jiki dakuma lack of hope yace "how long does my wife have?" Kallonshi Dr yayi dan baiji Baba nason yaji Wanan amsan tambayan ba amman ganin kalan kallon dayakemai na ya shirya ji yasa ahankali yace "less than a month" hawaye Manaf yaji yazomai dasauri yajuya yafita daga office din, bayanshi Mu'az yabi da sauri yana goge hawayen dayazubomai, shiru Baba yayi kafin ahankali cikin wata kalan karyayyiyar murya yace "kasan dai kai ba Allah bane ba ko likita dazaka gayamin matata nada less than a month to leave" shi kanshi Dr ya bala'in tausayama Baba cus idanunshi sunyi jajir, cikeda lallashi yace "Alhaji listen to me, niba Allah bane, Allah shine masanin gaibu, kawai ina maka discribing lokutan datake dashine base on science, cells dinta sun soma shutting down daya bayan daya, I am just preparing you ne for the worst, you have to be strong ma yaranka, sabida ayanzu they're looking up to you, ka dake sanan ka koyamusu sudake, kanunama matarka so da kauna sama da da, karku dinga kuka agabanta koku dinga nunamata damuwa, hakan zai saukaka mata abubuwa da dama, ganinku cikin damuwa da rashin walwala shi zai karamata damuwa da zafin ciwo, dan haka Alhaji I am giving you Wanan chance din cry as much as u want now, after yanzu baka kara kuka ko nuna rashin kwazo sabida yaranka" kaman jira Baba yake ahankali hawaye suka shiga kwararowa daga idanunshi, tissue Dr yadauka yabashi karba yayi dasauri yakai kan idanunshi yana sharewa cikin wata kalan murya dake sosarai yace "I don't want Maryam to leave me, naso mu tsufa tare sanan mu mutu tare, why are you doing this to me now Eh Maryama diyar albarka" saukan da kanshi las Dr yayi yana sauraron Baba yakai kusan minti 15 ahaka sanan ya share fuskanshi tass da tissue Dr

yanunamai bathroom yashiga ya wanko fuskanshi yafito yama Dr sallama yafice zuwa dakin Mama ganin su Manaf tareda ita tana bacci ana mata Karin wani abu kaman yellow madara yasa yafito, zama yayi a kujeran gaban dakin sanan yaciro wayanshi number dayay saving da Amini yay dialing, ringing daya aka daga cikeda barkwanci irin na manya yace “badai kahanamin yarinya zuwa makaranta ba” dan murmushi kadan yayi sanan yace “jikin Maryam yatashi muna asibiti Baffa” anatse  daga dayan bangaren akace “Subhanallahi, turn d car Bala muje asibiti” kawai aka katse wayan.

Yana zaune  awajen ko cikakken 10min ba’a dauka ba, wani Babban mutum da akalla shida Baba zasuyi sa’onni ya shigo cikin asibitin yana gyara Babban riganshi, farine mutumin sol yanada kiba dan yamafi Baba, shida wani dan saurayi dabazai wuce sa’an su Manaf ba dayay kama dashi dukansu fuskokinsu yanuna damuwa sosai, yana karasowa dafa kafadan Baba yayi yace “be strong my friend, Allah yabama Maryama lafiya, Allah yatashi kafadunta, Allah yasa kaffarane” tashi Baba yayi yanadan murmushi sanan yakalli yaron dake gaidashi yace “su Baban Baby girl Hafiz, Allah ya raya” ahankali yace “Ameen Baffa” sanan suka shiga ciki, har lokacin bacci take, da idanu Baffa yama Baba alamu su fito, suna fitowa yace “bazamu fitada ita wajeba ko har yanzu tanakan bakanta”.

I will talk to her idan ta farka, ahankali Baba yace “Allah yasa ta yarda” kara komawa sukayi wajen Dr ko akwai wani solution amman babu, dudda haka Baffa saida yakira some of the best Doctors dayasani a Abuja but is still same thing hakanan suka hakura.

Wajajen 3:00 na rana tafarka, dakin tabi da kallo kafin ahankali tafara yunkurin tashi dasauri Manaf da Mu’az suka dagota, ahankali Mu’az yace “kinajin yunwa Mama mezakici” dakin asibitin tabi da kallo kafin ahankali tasauke ijiyan zuciya tadanyi murmushi ganin duk sun damu tace “ya akayi bakuje aiki ba yau, laaaa is that Hafiz” tai maganan tana kallon Hafiz dake zaune kan kujeran gaban gadon yana kallonta cikeda tausayi, cikeda murna tace “zonan zoka nunamin hoton jikata nagani” dan murmushi yayi yataso yazo, wayanshi yaciro yafito da picture cute baby girl dinshi yabata karba tayi tace “Masha Allah tubarkallah, Allah ya rayamana kaga yarinya kaman Babanta Yan biyu” tai maganan tana nunamusu hoton kafin idanunta ya sauka kan time din wayan ganin karfe uku har da minti goma yasa dasauri tamikamai wayan takalli Mu’az tace “kiramin Dr yasallameni inkoma gida, Khairi takusan dawowa daga school” tana maganan saiga Baba da Baffa da Dr sun shigo tare, Baffa na ganinta yace “ya jiki Maryam” murmushi tayi tace “Alhamdulillah Baffa, ya ji kalle inasu Hajiya Asiya” kafinma taji amsanshi tace “Dr zokai discharging dina natafi gida” ahankali Dr yakaraso wajen yace “Hajiya kibari mu dubaki na kwanaki tukunna saimu sallameki” kallon Baba tayi sanan takalli Dr rai Adan bace tace “sallameni yarana banaso su dawo Bana gida Dan Allah” kallon Baba tayi sanan ahankali tace “daman Wanan ne shirinka idan ka kawomi asibitin arikeni” dasauri Baffa yazo wajen anatse yace “Maryam kalleni nan” ahankali tajanye idanunta dagakan Baba dake kallonta kuri takalli Baffa, anatse Baffa yace “Maryam kiyakuri ki zauna likitocin nan su cigaba da baki

gudunmawa, zamanki agida zai karasa ciwon yazama worst ne, dan Allah maryam inhar kinajin magana ta" lumshe idanunta tayi sanan tabudesu ahankali tace "Baffa tun ina yarinya kasanni ban taba cemaka no ba, kome kacemin inayi dan haka yau Baffa dukanku anan zan rokeku alfarma, dagayau dan girman Allah kome zai sameni karku sake dawodani asibiti, Baffa nasan kalan chutan danake dashi, nasan metake nufi, da inzauna anan allurai da maganinsu yakarasa cinyeni gwara in koma dakina, I want to die adakina tareda yarana dakowa, I hate hospital and zaman asibiti shizaifi kasheni dawuri sama da komi, please Baffa dan Allah, idan baka yarda ba naji zan zauna, amman rokonka nake please Baffa" kowa na dakin saida jikinshi yay sanyi har Baffa, ahankali Manaf yakalli Baffa yace "Baffa please grant Mama wish, let's just take her back home ko Hafiz" gyadamai kai Hafiz yayi da idanunshi sukai jajir, hakama Mu'az, ganin Baffa da Baba sunyi shiru dan su sunfiso tazauna a asibiti tasami lafiya yasa ahankali Dr yace "Alhaji kubarta takoma gida, idan anything come up ku kirani ni zandinga zuwa nadauki Wanan nauyin" ahankali Baffa yakalli Baba dakokadan baisoba, kallon kayakuri takoma gidan, hakan yasa ahankali Baba yace "shikenan" murmushi Mama tayi sosai nan da nan aka zaremata drop din sanan Dr yarubuta mata magunguna suka saya sanan suka dawo gida gablaki dayansu.

💫 ALKAWARIN ZUCIYA 💫

✍🏻M SHAKUR

1️⃣4️⃣

Free page

Wuraren 8:50Am sukakai school. Adamu na parking wajen parking tafito da saurinta bama ta tsaya mai sai anjima ba tashiga sauri cus 9 dot mutumin nan ke shiga aji gashi baya wasa da attendance, tana cikin tafiya zuwa class saiga wasu yammata su hudu sun taho tunda suka ganta sukahau ihun murnan ganinta Khairy nada wani irin farin jini naban mamaki wajen mata, tareta sukayi. "Khairy how far"? Murmushi tayi dake karamata bala'in kyau tace "lpy lau wlh, yanaga zaku waje daban ba class garemu ba yanzu" yatsine fuska sukayi, daya daga cikinsu tace "wlh dabaki wani wahalar da kanki ba wajen class din Mr Okeme ba ba'a taba ganewa ba, ke saurayinki Ahmad celebrity yazo nemanki fa" hararanta Khairy tayi tace "Malama niba saurayina bane kidena hadani dashi, na wuce class nidai" tai gaba abinta ranta abace, daya daga cikinsu ne ta daga murya tace "idan yakadoki meet us a garden chan mukayi" daga murya itama tayi tace "that's not gonna happen Ladies" tana tafiya wasu another set na yammata na tareta bamata tsaya saurarànsu ba tace "I will see u later ladies inada class now" tahau tafiya gudu gudu sauri sauri, duk inda tabi ana kwalamata kira Khairy Khairy waving mutane kawai take tawuce benen dazai kaita ajinsu tana kaiwa yana shiga tana tsaye yana kallonta yaja kofanshi yarufe, ahankali ta yatsine fuska murya chan ciki tace "this wicked man cannot make

heaven" sanan tajuya tana kallon kasa daganan bene yanda student kowa na takanshi sanan ta fuzar da iska ita dai ko itace allazi boko bazata taba tsayuwa jikin window har agama 2hrs class ba, tashi tayi abinta tafara tafiya tawuce tana sauka daga staircase abinta tanadan turo baki ita kadai tana kunkunai.
Sabida yanda ranta yake abace taji bamatason tabi normal hanya friends nata suyita tareta da magana hakan yasa tabi ta parking space dan taje garden daga wajen, ahankali take tafiya ita kadai a parking space din tana cikin tafiya a parking space din taji an kwala mata kira. "Khairy" dan tsayawa tayi jim batare data juyoba jin muryan namiji ne ke kiranta, tunani tafara acikin kanta muryan waye wanan sai chan taja wani kalan annoying tsaki tacigaba da tafiya abinta gani kawai tayi ansha gabanta wasu maza guda biyu sunshamata gaba suna sanye da kananun kaya sun bubbude hannuwa irin suna tareta dinan, wani kalan daure fuska tayi babu ko alamun wasa akai tace "me haka" dan dariya sukayi daya daga cikinsu yace "listen to Ahmed mana Khairy yasan bazaki tsayaba saisa yace mutareki" yay maganan suna nuna mata bayanta, juyawa tayi cikeda masifa wani black skin guy ne da dududu bazai wuce mate nata ba in age maybe 20 ko 22yrs haka yake, yana sanye cikin rugget kayan yan iska dinan, crazy baggy jeans da wata babbar baggy riga yayi dying gemunshi zuwa blond color kana ganinshi kaga irin yan iskan yaran nan gashinan very popular aciki school nasu, wani kalan mugun kallo tamai da manya manyan idanunta tace "kai da boys dinka Ahmad should get out of my way" wani kalan murmushi yamata tareda daura hannunshi akan kirjinshi yana shafawa yace "auuch! I love it when you look at me like that Khairy with those ur big big lulu white eyes, Baby my heart only beat for you" spitting miyau tayi agefenta sanan tajuyo takalleshi tace "you disgust me Ahmad, nagayamaka time without numbers stop wasting ur time on me, you are not my type of guy, idan maza irinkane suka cika duniyan nan I rather die banyi aure ba dana aureka, I don't like you an taba soyayya dole ne" dan takowa sahu daya yayi zuwa gabanta, tsayawa chak tayi tareda kama waist dinta kirjinta na bugawa fat fat, wani mayen kallo yabita dashi barima kirjinta dayaga yacikamai idanu tunba yauba tunda ya lurada yanda Khairy keda boobs yaji yakara haukacewa akanta, dan hucin zafi Ahmad yayi yana kallonta still sanan yanuna kanshi yana bude kafafunshi da tsabagen effizy sun koma kaman boleg yace "look at me kinsan how many babes anan School namu ke kiyamun laili because of me eh? Look at me Khairy, I have money, I was born in wealth, banda haka I am a hip hop rapper number 1 a arewa, yaro mai zamani, har rap nayi da sunanki natura miki a watsapp u don't even open my chat balle kiji how much I love you, Khairy tell me mezan miki dazaki soni eh, kinga we are the only ones here, just tell me babu kowa don't be shy Khairy, baki sona don't u wish to be mine, don't u wanna make matan makarantan nan jealous ace Kece tawa, I want you to be my Choima while I become your Davido, lemme make you famous, lemme make u a star gurl, what will I do to make you mine baby na? Don't u want all of this" all maganganun dayake mata jitake kaman tai amai bala'in kyaman Ahmad take bawai he's dirty bane, kawai dai yanayinshi yanda yake dressing yana shiga kaman wani su wizkid yayi coloring gemunshi da halinshi na waka ita kawai he's not her spec, yana mata magana yana wani wawware fingers kaman yana rapping yana kama tsakiyan baggy wandonshi, ko kiranshi amatsayin boyfriend nata ma bataso ta tsani taji anyi, bakin ciki da haushin shi yamasa tama kasamai reply kawai tajuya ta gefenshi zata wuce dan sometimes idan abu is really annoying agareki rasama abinda zakace kake, kawai ji tayi yariko hannunta "don't go baby wait" wani irin juyowa tayi batai wata wata ba kawai ta daukeshi da mari jikake

tass! Wani irin ihu abokanenshi sukayi suna waige waige ko there's anyone there dayaga Marin datama Ahmad dan zai zama abin kunya ance wata tamari hiphop rapper. "Ke celebrity kika mara" fizge hannunta tayi tana kallon yanda yadaura hannunshi kan kuncinshi yana wani irin kallonta da idanunshi dasukai jajir dan marin ya shigeshi, rawa jikinta yafara da sauri tajuya Ahmad daya bala'in zuciya yace "ku bita" jin haka yasa ta kwasa da bala'in gudu acikin parking space din dababu kowa tana kalle kalle, kaman ance takalli right side dinta, hango wani dogon mutum tayi yabata baya Awani lane na motoci yana tsaye jikin wata suv waya a kunenshi da alamu waya yake, wani irin kwana tayi tana gudu tai lane din dayake batai wata wataba tana kaiwa daidai inda yake batai wata wataba tawani zaga ta gabanshi ta shige kirjinshi at once tana boye fuskanta akirjinshi jikinta ko'ina narawa sosai sabida tsoro yanda maza har biyu komatace uku suka biyota, cikin Yar siririyan muryanta that is trembling sosai tace "please save me…..plss…….I'm sca……." tana maganan tana nishi da sauri da sauri dayake jinshi harcikin fatan kirjinshi don fuskanta gabaki daya na wajen ne, daidai lokacin daga boys din Ahmad din har Ahmad din dukansu sunzo wajen sun tsaya agabansu suna maida ijiyan zuciya sabida gudun dasukayi, One by one mutumin ke binsu da kallo batare daya furta ko a word ba har lokacin wayan nakan kunneshi bai cireba, faduwa gaban Ahmad yayi ganin fuskan mutumin dake kallonsu, ahankali yajuya sadaf sadaf daso samune ko takalmin shi da kasan wajen karma suyi motsin nuna alamun yana moving sanan ya yafito abokananshi da hannu yace "let's go guys" dasauri sukace "marinka fa tayi Boss" da saurinshi kaman ana hankadashi yawuce yace "shikenan nidai natafi ku ku tsaya" ganin yanda yake tafiya da saurin bala'i tun bayan yaga fuskan mutumin yasa suma sukasha jinin jikinsu suka juyada sauri suka wuce.

"Eh Gwaggo ina jinki sorry ba shareki nayiba, Abban nake jira nariga nakawo shi…" ahankali tashiga dagoda kanta kaman wata mara gaskiya cikeda kunya jin mutum na wayanshi ta tsokano fada tazo tafada jikin shi, kanta akasa ahankali sadaf sadaf tashiga fitowa tana matsawa baya kafin gently kanta nakasa batare data kalleshi ba tace "thank you" sanan ahankali tajuya tashiga tafiya har lokacin gabanta nafaduwa sosai. "You!" Taji kaman daga sama mutumin yakirata chak ta tsaya batare data juyoba, "turn around" taji muryanshi anatse yet with authority batasan mesaba amman kasa ketare abinda yace tayi tayi hakan yasa gently tajuyo sanan ahankali tadaga fuskanta takalleshi, wani dogon saurayi ne fari sol dashi kaman balarabe yana sanye da jumper na farar shadda bugaggiya kanshi babu hula gashinshi akwance baki sidik sai kyalli yake hannunshi rikeda iPhone 13 yazubamata idanu dababu alamun wasa daidai da digi acikinsu, hakanan jitayi takasa jure kallon mutumin dataga kaman ta sanshi amman ta manta a ina ta sanshi ta sauke kanta kasa, anatse yace "the next time I will see you making trouble I will arrest you!" dasauri tadago kanta ta kalleshi saida yafidi kalman arrest sanan police din ranan yafado mata arai, dauke kai yayi daga kallonta sanan yabude kofar motan daya tsaya jikinta ya shiga ciki tareda rufe marfin motan da sauri dayadan firgitata sanan ahankali tajuya tacigaba da tafiya ahankali.

Samin kanshi yayi da binta da kallo ta madubin motan, yanda take tafiya ahankali har lokacin bata dawo daidai ba, sanan ahankali yadauke kanshi daga kallonta jin wayanshi na ringing

again screen din yakalla ganin Grandma yasa yabude motan yafito yace “this woman will not allow me leave in peace”.

Garden din takarasa tun daga nesa kawayenta dasuka hangota suka kwalamata kira hakan yasa takarasa zuwa inda suke zama tayi sanan tadauki bottle na ruwan dake gaban Farida tabude takai bakinta ta kwalkwale duk kallo suka bita dashi, saida ta shanye goran ruwan tass sanan ta ijiye tana sauke ijiyan zuciya, Farida tace “daga ina kike haka duk kinyi zufa kaman kin fito daga yaki” dan yatsine fuska tayi kaman bazatai magana ba ganin yanda suke kallonta yasa tace “Ahmad na mara shine yabiyoni and someone…..” tadanyi shiru kafin ahankali tace “wani mutumi yataimakeni” atare dukansu all the 5 friends sukace “wani mutumi” shiru tayi sai chan tace “oho nima ban sanshi ba” dukansu dariya sukahau yi dasauri takallesu tace “me” hada baki sukayi sukace bakomi, sharesu tayi kawai cus she doesn’t even feel okay batasan mesa ba, duk suna zaune wata kawarsu tashigo eatery dagudunta tana haki tace “kufito kugani yan sanda sun shigo school dinan anzo ana kwashe su Ahmad da Gang dinsu” dasauri Farida tace “ke haba let’s go video it musashi a internet” dukansu tashi sukayi itama ta tashi tabisu suka fice daga cikin garden din, van suka gani na police gaban wani eatry dake kusada garden din dasuke ciki, dasauri suka karasa gaban eatry din student sun cika wajen suna kallon Van din police, suna tsaye wajen dayay cha da mutane sukaga an fito da Ahmad da akasamai handcuff a hannu an sashi a van din sai abokanen shi na dazsu dasuka biyota guda biyu saikuma wasu guda biyu daban yan sandan sun fito dasu ana sakasu a van din saiga police man dinan shima yafito daga eatry har lokacin yana sanye da kayan dazu farin shadda waya a kunenshi still, hada idanu sukayi batasan mesaba jitayi gabanta yafadi dasauri ta sauke kanta kasa tareda juyawa ahankali tamabar wajen bata kara juyowa ba kawai tai hanyar class nasu, daidai lokacin ana shirin fara wani lecture kujera tasamu atsakiyan ajin ta zauna sanan tabude jakanta taciro note nata da pen aka fara lecture ko kadan takasa concentrating batasan mesa ba she just keep seeing police man face din da what happen today, gabaki daya all through da day har yamma ita kanta tasan yau ba school tazo ba takasa natsuwa tunanin shi da komi yacika mata kai, wuraren 5 na Yamma Adamu direba yazo daukan ta shiga motan tayi ahankali tace “Adamu please kafara kaini Coldstone nasayi ice cream nasha saimu wuce gida” cikeda girmamawa yace “to Miss Khairy” daura kanta tayi akan kujeran tajuyar da kanta tana kallon hanya tareda fuzar da ijiyan zuciya, she just hope tanashan ice cream dinan sanyin shi zaisa brain nata yay sanyi tadena all tunane tunanin datakeyi tun safe.

Agaban wani Babban joint na coldstone Adamu yay parking hakan yasa tabude motan tafito ta shiga ciki, daidai wani Babban Jeep na shigowa wajen parking yayi kusa da Benz da Adamu ke ciki, bude gaban motan yayi yafito ahankali wanan karan yana sanye da kayan yan sanda Rolex din dake daure a hannunshi yakalla shidda saura, sanan yazaga zuwa boot din jeep din yabude keken guragu yaciro ya ijiye ya maida boot din yarufe sanan yadawo bangaren baya yabude motan wata kyakkyawan tsohuwa ce fara sol kaman balarabiya zaune abayan tasaka Riga da zani irin na tsofaffi anmai dinkin Bubu kafafunta da hannayenta sunsha lalli, hannunshi yamikamata batare dayace mata uppan ba hararanshi tayi tana kama hannun nashi tamike tsaye da kyar tana masifa tace “idan kaga dama kai gaba dani dagayau har jibi Ice cream dai

saika kaini nasaiwa jikoki na ja'irin yaro kawai" ko kala baice mata ba da taimakonshi ya daurata akan keken sanan yamaida kofan bayan yarufe da karfi tace "kama balla motan baban karfi, ubanka zai sayamin wata Alhamdulilah Allah yamai arziki rufin asiri danasha takaici" cikeda masifa yace "wlh Goggo in baki shiru ba anan zan barki na shiga ciki nasayo" wani kalan murmushi tayi tamaka bakinta tace "yo ai nadauka gaba kake dani to muje nadena" dan murmushi kadan kawai yayi sanan yashiga turata zuwa gaban entrace din dakenan divided into 3, staircase ne gefe da gefe sai tsakiya a bit sloppy floor dazaka haura ka shiga cikin shagon, daidai lokacin security na budewa Khairy kofa tana fitowa rikeda paper bag na ice cream din dakuma handbag dinta rataye a shoulder dinta, saiga wasu yara su biyu maza dabazasu wuce 8yrs ba suna guje guje kowanne rikeda ice cream dinshi dayan kawai ya mamayi brother shi ya fizge ice cream din hakan yasa brother yay ihu yabi dan uwanshi da gudu Khairy dabude mata kofa kenan tasa kafa tafito zata fara sauka daga staircase din kawai yaran suka fito suka mugun bangajeta dayasa ita kanta tasaki wani irin ihu kafanta ya gicce abunku da tiles kawai ta kifo zata fadi da mugun sauri Gwaggo tace "Subhanallahi" dawani irin sauri yasaki wheelchair Gwaggo daidai kanta zai daki dakaIUlin stairs din…

💫 ALKAWARIN ZUCIYA 💫

✍🏻 M SHAKUR

Dan magana da M shakur
wa.me/+2347012181461

1️⃣5️⃣

Yasa hannunshi daya awajen kanta ya daki tafin hannunshi bayan hannunshi yadaki stairs din sanan yakai dayan hannunshi yakama waist dinta yajuyo da ita hakan yasa ta mirgino side tafado jikinshi.

Daga yaran, security, iyayensu dasuka biyosu da sauri, Gwoggo dakekan wheelchair duk sandarewa sukai danba karamin faduwa zatayi ba inda Allah bai kiyaye ba, yanda yakeji yanda take nishi a hannunshi yasa ahankali yazare hannunshi daga waist dinta gently yakai hannun kan fuskanta yadago fuskanta yana kallon face dinta yanda ta kankame idanunta gam gam cikeda tsoro pink lips dinta nawani irin shaking dayasa dimples dinta na lotsawa tana nishi sama sama dayake jinshi akan hannunshi, murya chan kasan makoshi while looking into her face yace "are you okay"? Muryan dataji yadaki dodon kunnenta yasa kadan kadan tashiga bude idanunta danta gasgata abinda taji kafin tabude su tass tadaura white fararen idanun nan nata manya manya dasukenan kaman an wanke da madara tadaura su akan fuskanshi, jitayi

numfashinta ya makale somewhere in her throat ganin fuskanta dab da nashi yana kallonta as if he's trying to check something, yatsanshi yakai saitin nose nata jin bata numfashi kawai takafeshi da manyan white eyes nata yasa dasauri yakalli security man din yanunamai jakanta dake kasa chan yace "give me her bag" dasauri yakawo jakanta yamikamai juye jakan yayi kasa inhaler ta yafado dasauri ya dauka yacire marfin yakai bakinta ahankali yace "breathe in Ummulkhair!" Wani irin bugawa zuciyanta yayi jin yanda yakira sunanta kaman sunanta dayakira ne yay reviving nata batasan lokacin datawani saki numfashinta data rikeshi amakogoronta ba yafito mai kara sanan taja inhaler, zagayesu mutane sukayi barinma parent din yaran da jikinsu yay sanyi ganin Yarinyar da yaranta suka ture is even asmatic, ganin yanda mutane suka cika kansu duk ana kallonta yasa ahankali takai hannunta batare data kalle fuskanshi ba tana kokarin karban inhaler daya rikemata abaki, ganin haka yasa gently yasakin mata ahankali yaran dasuke tsaye sukace "Anty sorry" dan murmushi tayi tana cire inhaler daga bakinta duk dasauri tana kokarin tashi tsaye, tsugunnawa Maman yaran tayi tace "rest a bit please" tai maganan tana maida mata kayan jakanta back aciki tareda daukan mata jakan ice cream dinta da sauri ta mike tsaye tana karban abubuwan ta daga hannun matan tace "I am okay thank u" Gwaggo dake kallonta tace "sannu kinji inane gidanku mukaiki nida jikana" dasauri tace "direbana na nan nagode Ma" sanan tawuce da sauri hartana tuntube tai wajen motansu da Adamu ya kwantar da kujera yanata hira awaya abinshi batare dayamasan meke faruwaba, saida yaga tabude motan ta shiga sanan yakoma wajen Gwaggo yatura keken sukai ciki tace "ohh yara da rashin wayau Hydar, inda badadan kaiba da sunja Yar yarinyar nan tafasa goshi wlh, itama yarinyar uwa batacin abinci yoo nakema wanan maganan haka rainon indomie ce daga ganinta, ace daga yan yara sun bangaje budurwan yarinya haka kawai sai faduwa uwa lagwani, ace yara suci tuwo suki duk irinku ne ai gashinan kaga yara sun taso basu da karfi ko kadan, kai Allah dai ya wadaran naka subaci, Allah dai yasa kai aure ka haihu, wlh tun yaranka na wata biyu zan fara basu lafiyayyen tuwo da miyan kuka dataji daddawa" hararanta yayi baima cemata komiba ya sassayi ice cream din sanan suka fito tace "minene Wanan abin danaga kanata matsamata abaki" kin kulata yayi yasa ta amota ya maidata gida sanan yafito yatafi aiki.

Har suka shigo anguwan su badaidai takeba yau sau uku kenan tana ganin mutumin nan, saida suka shigo gida tukunna sanan taji wani kalan dadi, parking sukayi sanan tafito dasauri tana kwaso kayayyakin ta tana kwalama Mama kira. "Mamaaaa! Mama nadawo" daga Mama, Baba, Baffa da yayyinta da Hafiz duk suna zaune a falo dan basu dade da dawowa daga asibiti ba babu wanda yama iya wani kwakkwaran motsi, ita tsabagen murna batama lura da Karin mota kan tagidansu ba tai hanyar flat dinsu tana shouting Mama. "Mama nayomiki tsaraba yau nasayo miki ice cream kuma best flavor naki mint ban miki adding any thing ba ayanda kike sonshi plane" tai maganan tana bude kofan falo tana shiga tana kiran Mama. "Maaaam……" kasa karasa kiran Mama tayi ganin mutane a falon ga Mama zaune kusada Baba tana kallonta tana murmushi, hararanta Hafiz yayi yayi yace "inda ace ke kadai keda Mama aduniyan nan Khairy da munsha takaici" cikeda wasa Baffa yace "kagamin d'a kai kanama namiji ka more taka Maman balle ita mace kuma auta, ina tsaraban dakika kawoma Maman bazaki zo kibata

ba kin wani tsaya awajen" akunyace takaraso cikin dakin wani irin rungume Mama tayi tana murmushi akunyace ganin duk ana kallonta yasa tadaurama Mama paper bag na ice cream din akan jikinta akunyace ta sauko dagakan jikinta tace "Baffa ina wuni" murmushi yayi yace "diyar Mamanta ya makaranta" ahankali tace "fine" sanan takalli Hafiz tace "Ya Hafiz ina yini ya baby kuma, dan Allah ya Hafiz kasa mata sunana" dasauri yazaro idanu yace "waaaa niii rufamin asiri Khairy sokike y'ata tazama fitinanna irinki" dariya aka hauyi adakin ahankali Khairy tace "Baffa kaga Ya Hafiz ko" kafin Baffa yay magana Baba yace "karya yayi to Khairiya" turo baki tayi kaman zatai kuka Baffa yace "sharesu Yar albarka, sun lashe basusan baiwan dake tattare da sunan ki bane saisa suke magana ahaka" wani kalan murmushi tayi tace "yauwa Baffa" sanan tajuyo takalli Mama tace "Mama kin sha maganin kan yadena miki ciwo muji" takai hannunta tana taba goshin Mama with so much care, gyadamata kai Mama tayi tace "yadena, cikani maza tashi kai ice cream din kisa a fridge kije kiyi wanka kiyi salla idan bakiyi a school ba saiki sauko kici abinshi" gyadama Mama kai tayi sanan ta tashi tana kallon yayyinta dataga sunyi wani iri harzata wuce tace "Ya Manaf kungaji ne haka naga kunyi wani iri, Ya Maheer idanunka sunyi ja kaman kayi kuka" hararanta yayi hakan yasa ta murgudamai baki tawuce abinta sama itama, dayake yana takanshi dayaji ciwon Mama yatashi yau baima biyemata ba.

16

Free page
😉 enjoy

Kofan dakinta tabude ahankali ta shiga tanabin dakin da kallo yanda ko'ina tsaf tsaf an gyaramata sai kamshi dakin yake, shiga ciki tayi sanan tamaida kofan tarufe kafin awani irin gajiye cikeda sanyin jiki tasaki handbag dinta akasan dakin tafada kan gadon batare data cire takalmin kafanta ba tawani kalan kankame jikinta tanajin wani irin sanyi na shiga jikinta, she don't even know why amman hakanan fuskan police man dinan take gani a idanunta muryan shi namata yawo a kunne  da kanta gabaki daya yana kiran sunanta Ummulkhair breathe in, runtse idanunta tayi gam gam tana feeling yanda bones nata ke cringing to each other tana ganin fuskanshi namata yawo a idanu kafin idanunta suna hasko lips dinshi wani kalan ihu tayi. "Ahhhh stop!"  dasauri ta tashi zaune tana wurwurga kafafunta cikeda damuwa tace "Stopppp noooo what's wrong with me"? Wani irin zabura tayi ta tashi tsaye kawai tawuce dasauri tafada bathroom, wanka tayo sanan tafito daure da towel tana tunanin yaushe Mama zatasa amata Kitso dan gashin ya isheta daga tsifemata jiya, wani simple dogon Riga tasaka sanan tasaka hijabi tai salla tana idarwa tafito falo tawuce ganin duk basu tasan sun tafi masallaci sallan magrib, dinning tawuce zama tayi tana bubbude kula rice tazuba kadan sanan tasa nama tafaraci saida tacinye sanan takai plate din kitchen kafin tafito ahankali tai stairs, knocking dakin Mama tayi sanan tabude kofan ganin Mama akan gado ta lullube da bargo yasa tashigo da sauri tace "Mama menene" wani kalan kallo Mama tamata tace "bacci zanyi nagaji" hawa gadon tayi tana kallon fuskan Mama tace "Mama kibari ayi isha'i tukunna nima bacci nakeji"

gyadamata kai Mama tayi tana kallon gashinta tace “weekend zakiyi kitso tunda ke kin dawo yarinya daga tsife miki kai kanki yadawo kaman na mahaukaciya” gyadama Mama kai tayi tana hamma, ganin haka yasa Mama tace “Oya tashi kije kiyi sallan to gashinan ana kira saiki kwanta tunda kin gaji, kinmasha ice cream din” girgizakai tayi agajiye tace “gobe zan sha Mama nagaji, gud night world best” night my baby girl, Mama tai maganan tana binta da kallo wucewa tayi tafice daga dakin tana salla ta kallabi tahau gado sai bacci.

Da asuba tana tashi salla tafarayi sanan takoma bacci dan yau batada lectures sai 10 and she wants to sleep sosai cus kanta yay clearing tadena all this banzayen tunanin nan datakeyi. Karan wayanta yatadata by 9, da kyar ta iya bude idanunta ta kalli wayan rabon data danna wayanta hartama manta one thing dabai dameta aduniya kenan ba waya, she’s not just a phone person, itadai barta da physical surutu, yawo rawa haaba anan ake samin Khairy, hannunta tamika da kyar tadauko wayan ganin Besty yasa taji duk wani kalan bacci datakeji yafice daga idanunta dasauri tai picking call din tace “Iyye su Besty Amarya ai nadauka kin manta dani yar rainin hankali saisa na shareki banma nemekiba” kuka Besty tasaki awaya dayasa dasauri ta tashi zaune adan tsorace tace “ke menene Besty, what happen? Kinasa inajin tsoro why are u crying?” Cikin wani kalan muryan ban tausayi Besty tace “Khairy wlh nafasa auren mutumin nan kasheni zaiyi tun ranan da aka kawoni abu daya ake har yau nagaji” dan ware idanu Khairy tayi tanajin maganan wani banbaram itadai barta da rashin ji but duk wani harka na maganan banza da Iskanci bata aciki, adan kunyace cikedajin nauyin magannan tace “to ba ance ana sabawa ba” tai dan shiru saikuma ta turo baki tace “idan yaki kihadashi da Maman ku” wani gajeren tsaki Besty taja cikeda masifa kaman tabugama Khairy dundu tace “I don’t even know why I called u you are crazy Khairy, da zancen party ake da yanzu kingama tsara komi, lemme call Amal” tana maganan ta katse wayan, hararan wayan Khairy tayi ta ijiye saikuma chan kaman ta tuna wani abu wayan ta dauka dailing number Besty tayi back ringing daya tadaga, ahankali tace “sorry Besty kinji I seriously don’t know what to tell u or how to advice u” cikin muryan damuwa Besty tace “wai Khairy when will you learn all this stuff eh, u are just hella wired Umma, u are just leaving life kaman bamace ba gashi duk munata aure Khairy keko saurayi bakida shi sai wanan Wizzy dake binki” hararanta Khairy tayi tace “nacemiki kidena hadani da wanan yaron” dan dariya Besty tayi kaman ba itane mai kuka yanzun nan ba tace “naji nadena, yanzu dai kinyi wani saurayin”? Dan shiru tayi kaman mai tunani harta bude baki zatai magana saikuma tai shiru hakan yasa Besty tace “ohhh wowww, Khairy this is something new, tell me who is he? Dan tunda nake dake duk aka miki tambayan saurayi direct kike cema mutum baki dashi wanan dakika kasa magana tell me wayeshi” dan murmushi tayi tayi dan juyi akan gado tana dan lumshe ido saikuma ahankali tace “wlh Besty banda kowa kawaidai wani Police man ne naketa haduwa dashi this days amman ko magana bamayi kawai dai he always saves me from trouble ne I don’t know if that means anything amma dai ba soyayya muke ba ko magana ma bamayi” ahankali akuma natse Besty tace “ohh my Goddd! Khairy kinji yanda harwani natsuwa kikayi kina bani labarin police man dinnan kuwa, My world Khairy you love me! Wlh….” Dan yatsine fuska Khairy tayi dasauri tace “stop it! Mutumin dabanma sanshi ba, yaushe zaki dawo school nidai” dariya Besty tayi sosai tace “tunda u are avoiding maganan ai ba matsala, this weekend zai dawo dani but every weekend zai dinga zuwa” gyadamata kai Khairy tayi tace

“sai kinzo bye” tai maganan tana katse wayan da sauri dan tasan Besty bazata taba hakura da topic dinan ba, ijiye wayan tayi ahankali sanan ta mirgina zuwa dayan gefen gadon tana tunani.

Ajiyan zuciya tasauke sanan ta tashi tasauka daga kan gadon zatai bathroom wayanta yashiga kuka cikeda masifa tadawo tace “mekuma kike sake kirana eh” wayan tadauka ganin Glory yasa tai picking wayan takai kunne kafinma tai magana Glory tace “hello fine girl, melanin goddest, pop skin with those sexy milky eyes” dan dariya tayi, Glory is her friend masters ita take a school nasu ta girmeta far far amman tana bala’in son kawance da Khairy, dan murmushi Khairy tayi tace “Hey! Where have u been i haven’t seen u in school this days” dan dariya tayi tace “I travel naje PH chan gida, Khairy u don’t know I am angry with u ba” dasauri Khairy tace “what happen? Why” kaman zatai kuka tace “today is my birthday Khairy” Adan kunyace Khairy tace “ohhh Glory, sorryy happy birthday darling” dasauri Glory tace “come to my party and wish me there, zamuyi a jabi lake mall a cikin jirgin ruwa, dress code is red 4pm sharp” wani kalan juya idanu Khairy tayi tace “ohh okay then bye see u later” ta katse wayan sanan tawuce bayi da gudu wanka tayi agurguje sanan tafito cikin wata doguwan rigan atampa ta shirya tafito tana tunanin yanda zatai planning zuwa party zata dawo gida by 2 wuraren 5 saita tafi tadawo 6.

Tea kawai tasha sanan tawuce school dan tayCi latti sosai.

17

Free page
Ahankali yake tuki ganin ya shigo cikin estate dinsu, saida yakarasa gaban wani dankareren gate sanan ya danna horn, budemai gate da akayi yasa yaja motan zuwa cikin gidan dakeda bala’in kyau kuma babban gaske ga flowers dasuka karama gidan kyau sosai, parking yayi abangaren parking sanan yakashe motan yana kallon cikin gidan dababu kowa sai gardener dinsu daketa yayyanke flowers yana gyara su, yakai kusan 1min cikakke zaune a motan yay shiru sanan ahankali yabude kofar motan yafito yamaida kofan  yarufe sanan yafara tafiya dai dai yawuce zuwa babban flat dakenan shine first flat a gidan, bude kofa yayi ahankali tareda sallama chan ciki sanan yashiga babban falon da babu kowa ciki, falon ya bala’in hadu yaji furnitures, saikuma dan kara dayakeji a kitchen da alamu mai aikice ke wanke wanke, juyawa yayi zai fice kaman daga sama yaji ankirashi. “Aliyu” dan juyoda kanshi yayi ya waigo, wata matace doguwa mai jiki fara kal da ita taci gayu da sarkan gwal a wuyanta wacce bazata wuce 40 ba tana sanye da lace ja da baki ke saukowa daga benen, kallo daya yamata yadauke kai yace “barka da rana Mami” dan murmushi matan tayi sanan takalli agogo bangon falon ganin is just 11 yasa tace “Lafiya kadawo gida ware haka Aliyu”? Batare daya kalletaba ahankali yace “lpy lau Mami” gyadamai kai tayi tana kallonshi still tace “tom shikenan, mezakaci a aiko maka dashi”? Batare daya kalleta ba har lokacin yajuya yace “zanci abinci wajen Gwaggo” yana maganan yajuya yafice tareda rufo kofan binshi da kallo tayi ta jikin window falon har saida yay

side din Kaka yabace mata daga gani sanan tasami kujera ta zauna tanadan karkada kafa tunda take bata taba ganin wanda uniform na police kemai kyau kaman Aliyu ba, haryau tarasa maisa Aliyu yawani zama police ba yaron dayay lafiyayyen karatu yakuma gama da good result, kwanciya ahankali tayi tana kwalama Yar aikinta kira dan tazo ta danne mata kafa.

Bangaren Gwaggo shima yanada girma sosai, da sallaman nan nashi chan kasan makoshi yadaga labule ya shiga dakin ko kadan Gwaggo dake zaune tana kada lagwani bataji alamun shigowan mutum ba kawai karan kwas kwas na takalmin dake kafanshi taji akan tile din dakinta afirgice takalleshi tana “Innailaihi wa innailaihi raji’un, waikai Aliyu wani irin murdadden yaro ne eh, bama wanan ba dan ubanka koma ka cire shegen takalmin nan naka dazaka shigomin dashi falo ina salla a ko’ina afalona dan tsarki ne dashi wlh” ko kallonta baiyiba saima hawa kan dogon kujeran ta dayayi yay kwanciya abinshi yanadan lumshe idanu, ijiye komi Gwaggo tayi tamike tana gyara zani tazo kanshi zatahau mai bala’in idanunshi daya lumshe tabi da kallo ganin sundanyi ja yasa tace “kai yaron nan zazzabi kake yine”? Dan bude idanunshi kadan yayi yakalleta dauke kanshi yayi yaki kulata, dasauri ta kalli agogo ganin ko shabiyu batayiba yaron da dazun nan dasafe yafita aiki yasa tace “wlh bakada lafiya Hydar zo meke damunka”? takai hannunta da duk audugan lagwani yake kai zata tabamai fuska dasauri yatashi zaune yace “karki tabani da hannun dattin nan Gwaggo” dan sassauta murya tayi kaman ba ita kemai ihu ba cikeda damuwa tace “meke damunka eh Hydar? Duk wanda yasanka yana ganin Wanan idanun naka yasan bakada lafiya, meke maka ciwo” tashi daga kan kujeran yayi yace “tunda bazaki barni nai bacci ba bari na barmiki dakinki” yay maganan yay hanyar fita tana kwalamai kira kaman badashi takeba, cikeda damuwa tace “ai idan bakaji nawa ba zakaji na ubanka, yaro sai bakin zurfin ciki da shegen share mutane sabida yaga nadamu dashi” duk yanajin ta tana surutunta bai amsata ba flat dinshi yawuce bude kofa yayi yashiga cikin dakin da babu abinda yakeyi sai kamshi ko’ina a gyare kaman babu wanda ke zama adakin, bedroom nashi yawuce yana shiga adaddafe yacire rigan yan sandan ya Yar anan kasan dakin sanan yazauna takalmin kafanshi yacire yazaro wayanshi yadaura saman side drawer sanan ahankali ya kwanta yanadan yatsine fuska bala’in ciwon kai yakeyi daya rasa na menene amman sai uban dauriya, har bacci yasoma daukanshi yaji wayanshi na ringing da kyar yadaga hannunshi yakai wajen wayan dauka yayi batare dayama kalli screen dinba yakai wayan kunne ahankali yace “Hello” daga tachan bangaren muryan wani magidanci ne yace “Aliyu meke damunka?” Dan yatsine fuska yayi yanaji kaman ya rufe Gwaggo da duka akan me zata fadiwa Abba dan gyara muryanshi yayi yace “Abba I am fine” cikin rashin gamsuwa Abba yace “Aliyuuu” dagashi sai Abba sukasan meaning din anytime yakirashi da Aliyuuu hakan yasa gently ya fuzar da dan iska ahankali yace “Abba kaina hurts so bad” anatse Abba yace “is that all”? Ahankali yace “yes Abba” “okay I am coming yanzun nan nadubaka” dasauri yace “no Abba I am fine kazauna please zansha magani” dan jim Abba yayi yace “Aliyu haryau banga wanda yakaika tsanan magani ba” sanin tsaf Abba zaibar hospital yazo yasa yace “Allah Abba zansha I promise” cikeda gamsuwa dan yasan Aliyu baya promise yaki cikawa yace “okay kasha I will call Ogan ka zance mai yabaka the rest of today da gobe kahuta, this work is draining you Aliyu banason shi, anyway that will be another day talk, kasha maganin ka kwanta” ahankali yace “to Abba” Allah kara sauki kaji gyadama Abba kai yayi tareda katse wayan, hannunshi yasa yajawo drawer

gefen gadon shi sanan yadauki paracetamol ya ballo guda biyu yana kallon maganin a hannunshi kaman yay amai, yadade yana kallon maganin sanan yasa hannu yadauki goran ruwan dake kan side drawer yabude kurba yayi sanan yajefa maganin da kyar ta hadiye sanan yasa goran abaki saida yasha kusan duka ruwan sanan yaji maganin yatafi ahankali ya ijiye goran kafin yakoma ya kwanta ya lumshe idanunshi bai wani dade ahakaba bacci ya kwasChe shi.



Free page

Wuraren 3 na rana yafarka, ahankali yake bude idanunshi yanabin dakin da kallo jin anrike hannunshi yasa yajuyo da kanshi ahankali wata yar budurwa ce da zatakai 22yrs zaune gefen gadon dake bala'in kama dashi kana ganinta kasan kanwanshi ce takama hannunshi gam tarike tanadan gyangyadi, tana sanye da doguwan rigan atampa, Meena kenan he's sure Gwaggo ce tagayamata baida lafiya saisa tataho daga dawowanta daga school, dan murmushi yayi sanan ya fizge hannunshi da karfi afirgice tabude idanunta takalleshi tana kara ware idanu tace "Ya Hydar katashi sannu yajiki" hararanta yayi yace "meya kawoki dakina" cikeda damuwa tace "yanzun nan muka dawo daga school muka tarar Gwaggo na kuka wai batada lafiya shine nazo naga kana bacci, cha tayima na sata a keke nakawota wurinka nasan damunka kawai zatayi saisa naki" dan jim yayi yace "jeki cemata tadena kuka I am fine" murmushi tayi sosai tana kallonshi tana kokarin tashi  dagakan gadon tace "Ya Hydar kanason Gwaggo amman kullum fada kukeyi baka nuna mata kana sonta maisa" hanyar bathroom dinshi yawuce yace "kafin nafito kibarmin daki inba hakaba jikinki zai gayamiki" tashi tayi ranta namata dadi ganinshi lafiyanshi kalau tace "Ya Hydar zaka kaimu Jabi lake mall din? Kagama sai Gwaggo takara yarda lafiyanka kalau ko" "go and get ready" yafadi murya chan kasa duk ya gaji yakosa tabar dakin dansai sashi surutu take, shigewa bathroom din yayi abinshi yamaida kofan yarufe, tashi tayi cikedajin dadi tai hanyar fita, sai yanzu tama lurada riganshi akasa dakin tsugunnawa tayi tadauka sanan tamakalamai a hanger tabude wardrobe dinshi tasaka tawuce tafice danta gayamusu su shirya.

Yadade abayin sanan yafito wani simple jallabiya yasaka yay salla sanan yatashi ahankali har yanzu kanshi namai ciwo sosai daurewa kawai yake, shiryawa yayi cikin wani milk yadi mai bala'in taushi danshi baya iyasaka kaya masu karfi, feffesa turare yayi sanan yadauki wayanshi yana dubawa ganin baida miss calls yasa yafito yana tafiya one one, tundaga gaban kofan dakin Gwaggo Meena ke kallonshi ganin yay wani kalan kyau tana murmushi ohh God duk duniyan nan batada wanda takeso kaman Yayanta Hydar, hararanta yayi alamun kallon fa wuce

kigayamusu su shirya hakan yasa tawuce tashiga dakin Gwaggo tana kallon Gwaggo dataci gayu itama tana zaune kan tabarman data shimfida akan lafiyayyen carpet din dake falon, girgizakai kawai yayi baitaba ganin rigimammiyan tsohuwa irin Gwaggo ba, gatada carpet amman tsabagen kauyanci saita shimfida tabarma akai, idanko yawone ko jikokin nata wani zubin da gangan sukekin gayamata zasu fita dan tsohuwarnan Allah ya zubamata son zuwa yawo kaman taci kafan kare.
Wasu yammata guda biyu ne zaune agefenta suma kyawawa dasu Amal dakuma Khadija duk sunci gayu kansu daya, zama yayi abinshi Gwaggo tabishi dakallo bata kulashi ba shima bai kalleta ba yakalli su Amal dake kallonshi suna gaidashi yace “kawomin abinci” tashi Amal tayi dasauri zata fita yace “ina zaki”? Ahankali tace “falon Mami zani nadebo maka” girgiza mata kai yayi yakalli fuskan Gwaggo yace “bani na Gwaggo” daure fuska Gwaggo tayi takalli Amal tace “jeki uwardaka na abincinshi na cikin kula sabida ku na boye kafin ku cinye mai yara saikace mayu barinma wanchan mai idanun kutaren” tanuna Meena tabe baki Meena tayi daga ita har Khadija, Amal tawuce tadauko mai takawo, kafinma Gwaggo tai magana Khadija ta tashi tadauko mai ruwa da drink daga fridge na Gwaggo ta kawomai bude abincin yayi dambu ne lafiyayye yanasan dambu hakan yasa yaci ba laifi Gwaggo tana zaune tana kallonshi ganin yadanji sauki yasa hankalinta ya kwanta sosai saida yagama ci sanan suka kwashe kayan sukai kitchen dashi shikuma yafice suka biyoshi abaya suka fito Gwaggo natafiya ahankali dan kafafun sun dawo a lallaba bata iya tafiya sosai saisa ko’ina za’aje da ita da keken guragun ta tareda ita.

Mami suka gani a tsakar gida kan wani hadadden chair da table agabanta tadaura kafanta kan table din Yar aikinta na gyaramata nails na kafa tana danna wayanta tana tauna cingum tana murmushi, jin sahun tafiya yasa tadago kanta binsu tayida kallo tace “Hydar daga kannenka sai Kakar ku kakeso nibaka sona saisa ba’a taba fita dani ba” tai maganan tana kallon Aliyu dayamayi gaba abinshi kaman badashi akeba, kaman jira Gwaggo take taballamata harara tace “akanme zai soki ke kika haifeshi jimini ikon Allah” dan dariya Mami tayi tai kara da cingum dinta tace “Hajiya Gwaggo maida wukan a dawo lpy” “Mami mun tafi” yaran suka mata sallama, “saikun dawo” Mami ta amsa yaranta tana murmushi tabisu da kallo  tana hararan bayan Gwaggo, saida sukai nisa sanan ahankali tace “Allah yakasheki mayyar tsohuwa kawai na huta, mata takai kusan shekaru dari amman taki mutuwa” tana zaune tana kallonsu yaja mota suka wuce sukabar gidan.

On a normal speed yake tuki yau danji yayi kanshi yasoma ciwo sosai amman yadaure dan baiso Gwaggo tagane ballema tadamu, ahaka harsukakai jabi lake mall din wuraren 5:30. Parking yayi wurin parking sanan suka fiffito, ganin yazauna aciki yasa Gwaggo tace “muje mana” yatsine fuska yayi yafito yabude boot yaciro kekenta yana sata akai yace “zan jiraku anan akwai wayoyin office dazanyi” yay maganan yana bama Meena ATM card dinshi yace “idan kuka kararmin dakudi Abba zansa yabiyani da monthly allowance dinku” dariya sukayi sanan Meena ta tura Gwaggo suka wuce tace “bye Ya Hydar” shiga mota yayi yazauna tareda

kwantar da kujeran yana kara karfin Ac sanan ya kwanta kanshi najuyawa ya tsani rashin lafiya saisa baimaso ya kwanta ma wanan, ajiyan zuciya ya sauke ahankali yanaji zuciyanshi natashi cikinshi najuyawa kaman zaiyi amai, jin amai yazomai dawani irin sauri ya yunkuro yabude kofa yafito sai amai, kwaro amai yashigayi anan wajen motanshi sosai idanunshi sukai ja…..

Ahankali ita kadai take tafiya a parking lot din wayanta na kunnenta tana sauraron kwatancen da Glory kemata na inda venue su yake acikin wajen, bakaramin kyau tayiba tana sanye dawani english gown daya kaimata har kasa red yabi jikinta sosai ya bala'in fito da shape nata dudda bawani kamata yayi ba amman sabida kalan yadin yasa yanayin jikinta yafito, fuskanta yay wani kalan kyau yana glowing dudda bata shafa hoda ba dan ita hoda nasata kuraje a fuska saisa tama daina sawa but ta gyara eyebrows dinta sanan tasa kwalli dayawani irin haska fararen idanunta suka fito wallll, sai pink lipstick data kara kan pink lips dinta dayasa lips dinta yay wani kalan crazy baby pink daya kara fito da fuskanta sosai, ta gyara gashinta daya gama hargitsewa tai styling frontal hair din da gel dudda dama gashinta a kwance yake but karawa da gel datayi yasa tai kyau fuskanta yafito sosai takawo wasu simple pearls earring silver tasaka, tayana light peach karamin veil akanta dayadan zame kadan kasa sabida iskan da akeyi uwa za'ai ruwan sama gashi bahadari just that garin is looking damn cozy, tasaka heel dayama kafanta kyau silver dayafito da fine fine sexy toe nails dinta, tana tafiya ahankali taratataya wani karamin handbag na LV a shoulder ta sai goran bottle water na Eva data rike tasha kadan aciki dan she was thirty ahanya ma tasaya yanzun nan dazasuso.

Kaman daga sama taji kakarin amai na mutum chak ta tsaya at the same time taji kirjinta yawani buga dum! Tsayawa tayi chak sanan ahankali tace “ok I am coming now nagane wurin” katse wayan tayi sanan tajuyo tana kalle kallen inda take ganin bataga kowaba sai shiru dataji yasa tacigaba da tafiya abinta, karajin kakarin amai datayi yasa tasake tsayawa chak ita kanta she don’t even know why take tsayawa amman kaman something is pulling her, komawa baya tashigayi ahankali tana waige waige kafin chan tahango wani Babban mutum dan that doesn’t look like a small boy tsugunne in between wasu manyan jeeps guda biyu yabata baya yana amai, tsigan jikinta taji yawani tashi, tun tana Yar karaman Yarinya ta tsani taga mutum naciwo, part of the reason why kowa is her friend a school kenan inhar Khairy tasan u are sick to far she die there Khairy is damn caring idan mutum naciwo saitamafi mai ciwon damuwa.

Takai almost 20second tsaye tana kallonshi yanda yake amai tsigan jikintai natashi tun yana amai abu na fitowa har kawai amman yake babu abinda kefitowa, ahankali tadaga kafanta zata wuce ta tafi samin kanta tayi dasake juyowa takalli bayanshi sanan takalli bottle water hannunshi kafin ahankali tana tafiya gently tawuce lungun motoci adaidai bayanshi dab dashi ta tsaya tana kallonshi bakinta nadan rawa dan tsoroma takeji mutum na amai tazo meruwanta amman still tadaure ahankali tace “Sir do you want some help nakira maka security”? Batare daya kalleta ba koyajuyo ba ya girgiza mata kai alamun no, jitayi zuciyanta yamata wani nauyi kaman tai kuka tasake dukowa kanshi sosai anatse tace “but u are very very sick, do you want some water, I have water, here gashi” tai maganan da sauri tana budemai goran ruwan tana

mikamai ta gaban fuskanshi, goran ruwan yabida kallo, murya chan ciki dabaya fitowa sosai yace “thanks” goran tabida kallo ganin bai karba ba yasa ahankali tace “ka karba ka wanke fuskan ka u will feel better, haka Mama kemin idan banda lafiya nai amai” jiyayi kanshi nawani irin ciwo, azuciye yawani juyo da jajayen idanunshi dake cikeda zazzabi yawani taso kaman zaki zai cinyeta baya tayi atsorace ruwan hannunta yafadi heel din kafanta ya turgude dawani dutse hakan yasa kafanta ya turgude tai baya zata fadi atsorace hannu daya yasa ya chapko hannunta dasauri yana kallon fuskanta da jajayen idanunshi kaman yanda itama a bala’in firgice take kallon fuskanshi kirjinta nabugawa fast fast lips dintal narawa sosai ganin police man dinaCn ne.

19

Cikinsu duka babu wanda ya iya wani motsi yana rikeda hannunta yana kallon fuskanta kaman yanda take kallon nashi, ganin iska nawani irin kadawa sosai gyalen ta gabaki daya yay baya iska na neman fizgeshi yay sama dashi yasa yay wani irin pulling dinta ta taso saura kiris tafada kirjinshi da kyar ta iya maintaining posture dinta gabanta nafaduwa sosai tasauke idanunta kasa, tundaga yatsunta datake wasa dasu tana yakushin riganta dasu yake kallo har zuwa fuskanta da lips dinta dake rawa sosai zuwa gashinta dakeda bala’in kyau datai parking tai donut da jelan gashin dayay yawa kana gani kasan tanada suma sosai gyalen na wuyanta, ganin yanda ake iska sosai ta sandare awurin not her self yasa murya chan ciki yace “cover ur hair” gyadamai kai tayi ahankali batare data kalleshi ba takai hannunta takamo gyalen daga wuyanta zata yana akanta kwace gyalen iska yayi da karfi saikan fuskan Hydar dasauri tadago kanta, ahankali ya lumshe idanunshi jin wani sassanyar kamshin da gyalenta ke fitarwa da atake yaji ya kwantarmai da tashi da zuciyanshi keyi duk wani amai dayakeji yakoma, gently yakai hannunshi yadaura akan fuskan nashi yadauki gyalen sanan ahankali yamika mata, kallon fuskanshi tayi kafin ahankali takalli hannunshi dake dauke da gyalenta dayake mikamata sanan tasa hannunta ahankali ta karba daidai wani kalan mugun ruwa sama ya sauko da karfinshi dayama firgitata dasauri takalli sama sanan takalleshi kafin tajuya da sauri zata wuce.
“Ummulkhair!” Taji yakirata amugun natse dayasa taji gabanta yawani kalan fadi, tsayawa tayi chak ruwan nadukanta sanan gently tajuyo takalleshi gani tayi yabude mata bayan jeep dinsu shima yana tsaye ruwan na dukanshi, batasan mesa ba but kasa mai musu tayi ahankali ta tako tazo har gabanshi sanan tashiga ciki ta zauna, bayan shima taga yashigo dasauri ta matsa chan gefe yamaida kofan motan  yarufe, daganan inda yake yadan mika hannu ya kunna motan sanan ya kunna AC motan yadauki wani bottle water yadawo yazauna yadan bude kofan motan kadan ya kuskure bakinshi kafin ahankali yamaido kofan yarufe sanan ya ijiye goran ruwan akasa ya kwantar da kanshi yana sauke ijiyan zuciya ahankali dukansu suna sauraron yanda ake ruwa da mugun karfi harda kankara ma.

Sunkai almost good 6min a motan babu wanda yacema wani wani abu kanta nakasa tana fidgeting yatsunta, shikuma yana zaune gefenta kanshi naciwo amman kallonta yake kaman an ijiyemai TV, ganin yanda ta takure tanajin sanyi sosai sabida ruwan dayadan daketa kadan sanan ga sanyin AC motan daya kunna yasa ahankali yadan yunkuro hannunshi yamika ya kashe AC sanan yadauki jacket dinshi na kayan yan sanda that is always acikin motan sanan ahankali yawarware shi matsowa yayi kusada ita yana kallon fuskanta bala'in firgitata tayi jin mutum kusada ita sosai dayasa takalleshi dasauri kallonta shima yake ko kyafta idanu bayayi ahankali yadaura mata jacket din kan kafadanta yarufamata shi da kyau yana kallonta kaman yanda take kallonshi tana nishi da sauri da sauri dayakejin hucinshi akan fuskanshi sanan yadan matsa baya zai koma wurin dayake da zama kaman daga sama ahankali murya chan kasa fa inda ace akwai mutum na uku amotan nan bazai tabajin metace ba tace "u are sick" kallon kwayan idanunta yayi kaman baigane metace ba, gyadamai kai tayi idanunta sun cika da kwalla sosai ahankali tace "wlh bakada lafiya, ur body is hot, let's go to the hospital please" tana karasa maganan hawaye ya gangaro mata daga idanu sharrrr, hawayen yabi da kallo kaman wanda baitaba ganin mace tai kuka ba, murya chan kasa batare daya koma ba he's still very much close to her ahankali yace "you don't want me to be sick" gyadamai kai tayi ahankali wasu sababbin hawayen nakara taruwa a idanunta, murya chan chan ciki yana kallon kwayan idanun nata dasukenan farare fat kaman farin gajimare yace "why"? Girgizamai kai tayi saikuma ahankali tace "I don't know, seeing u sick is making my heart to hurt" dan lunshe idanu kadan yayi sanan yabude su yadaura akan nata, lips dinshi sukai motsi kaman whistling yana kallon yanda take kuka mara sauti yace "stop crying" gyadamai kai tayi ahankali tana kokarin tsayar da hawayen, hannunshi yasa yaciro handky daga aljihunshi yamikama mata yace "here" karba tayi takai kan fuskanta tana goge hawayen saida yaga tagoge tass sanan yakoma gefenta yazauna da kyau yace "mekikazo yi anan?" ahankali tace "today is Glory's birthday my friend she's celebrating it anan" dan juyowa yayi yakalleta kaman mai nazarin wani abu yace "how old are you" kallonshi itama tayi kafin tasauke kanta ahankali tace "20" kaman daga sama taji yace "small Gurl" dawani irin sauri takalleshi tabe baki taga yayi batasan mesa ba abin saiya bala'in bata dariya she don't even know why, dan murmushi kadan tayi sanan tahadiye shi kallonta yayi ganin yanda dimples dinta keta lotsewa alamun murmushi take amman tana hadiyeshi, kaman daga sama taji yasake jefo mata tambayata anatse. "Are you in any relationship"? Dasauri takalleshi, kallonta shima yayi fuskanshi looking he's serious da tambayan, murya chan kasa yace "kinada any man dakikeso…..or yake sonki"? Yay maganan  muryanshi na breaking cus shi kanshi baisan mesa yakema tambayanta this kind of wired question ba, dauke kanta tayi, sanan ahankali ta girgiza mai kai alamun no, dan murmushi kadan yayi yanajin duk wani ciwon kan dayakeji yana tafiya, jakanta dake in between them yasa hannu yadauka yabude wayanta yaciro Dasauri takalleshi numbershi yasaka sanan yakira kanshi, danne danne taga yanayi awayanta kafin yamaida ya ijiye cikin jakan, ganin ruwa na tsagaitawa yasa tadan kalleshi ahankali tace "zantafi" yana kallonta right in the eye yace "where is ur driver? U should head home" gyadamai kai tayi sanan ahankali tace "yanata chan bangaren" inda take nunamai da hannu yakalla, ahankali yace "ok" bude kofa yayi yafita cikin yayyafin da akeyi yakoma gaba kunna motan yayi yaja motan har gaban motansu yakaita sanan yay parking jacket dinshi tacire ta linkemai ta ijiye ahankali tace "thank you" sanan tabude kofan zata fita kaman daga sama taji

yakirata. “Ummulkhair!” Faduwa gabanta yayi batasan mesaba duk idan yakirata sai gabanta yafadi, juyoda kanta tayi takalleshi shima ita yake kallo, ahankali yace “I am a very very jealous Man! Be mine only Khairy! I am in luv with you! Good night!” Dawani irin sauri har hannunta narawa tamaida kofar tarufe sanan tajuya tabude bayan motarsu ta shige kafin yaja motar nashi yawuce.

20
Free page

Wucewa yayi daidai lokacin wayanshi na ringing ganin Meena ce ke kiranshi yasa yamaida kanshi kan tukin inda yasan zai gansu chan yawuce, atsaye ya gansu da alamu shi suke jira, kashe motan yayi yafito yana kallon Gwaggo dake binshi da kallo ganin ya wartsake sosai yace “Ipy” hararanshi tayi tace “munafuki nidai sani a mota” sata yayi a mota yana murmushi kasa kasa sanan yamaida kujeran boot su Meena suka saka ledojin abubuwan dasuka siya a boot sanan yarufe kowa yakoma yashiga motan yaja motan zuwa gida yana parking yafito baima tsaya bi takansu ba masallaci yawuce dan yasan zasu tafi da Gwaggo ciki.

Tareda Abba suka shigo gidan daga masallaci magidancin mutum ne yana sanye da suit baki dan daga wajen aiki yake, falo suka wuce, duk su Mami da yaran na falo gaida Abba duk sukayi, ganinshi yasa Mami tace “akawo abincin yanzu Alhaji” girgiza matakai yayi yay hanyar stairs yace “I am coming tukunna muje Aliyu” binshi Hydar yayi har zuwa sama wani babban falo suka shiga wanda kana gani kasan na Baban shine, zama yayi akan kujera Abba yazauna kusada shi yakai hannunshi yabude idanunshi yana haskawa dawani dan tocula dankarami yana dubashi, dan jim yayi sanan yace “you have typhoid Aliyu, I think zan saka on injections tunda bakason magani” yatsine fuska yayi ahankali yace “Abba wlh naji sauki, kainafa kadai ke ciwo kuma yadena” “yimin shiru my friend” Abba yay maganan yana tashi wani babban first aid box yadauko yabude sanan yahada wani allura Aliyu naji yana gani Abba yamai allura, sanan Abba yace “Aliyu this work is draining you, akan me u are a Barrister kawani kama kashiga aikin police with just mukamin ASP eh, why will you choose a police man job Son common talk to me” yay maganan yana kallon Aliyun cikeda damuwa, Aliyu ne kadai danshi namiji, yaranshi duka takwas aduniya, Aliyu ne nafarko he’s 32yrs sai kannenshi mata guda bakwai hudu sunyi aure dukansu baa Nigeria suke aure ba Saura 3 agida suna school, ganin yay shiru yakasa cewa komi yasa ahankali Abba yace “tashi katafi, but make sure kaci abinci kafin ka kwanta kaji” gyadamai kai yayi sanan yatashi yawuce yabude kofa shikuma Abba yashiga cire kaya dan yay wanka duk bayajin dadi.

Yana fitowa da Mami yaci karo anan falon sama tana zagaye, kallo daya yamata yadauke kai yashiga sauka kasa itakuma tawuce tashiga falon Abban da sauri tanabin ko’ina da kallo dan Abba yariga yashiga bayi, ganin allura da first aid box abude yasa tasauke ijiyan zuciya taje

gaban wardrobe tana budewa dan samoma Abba kayan dazai sa….
**

Tana komawa gida kayan jikinta tacire tayo wanka sanan tai salla tasauko kasa gabaki dayansu duk suna zaune a falo suna dinner gaida kowa tayi sanan tazo kusada Mama tazauna tana kallon Mama dataga tasaka sweater turtleneck black daya rufe har wuyanta tasaka hulan sanyi shima baki kafanta da bakin safa, kallonta Mama tayi jin ajikinta ana kallonta hannu tasa taja hancin tace "ke abinci zakici ko kallona kikazo yi" dan dariya kadan tayi tace "Mama sanyi kikeji ne AC akashe" gyadamata kai Mama tayi batare data bata amsan tambayan ba tace "mezan zubamiki" kallon abincin tayi sanan takalli madaran da Baba kesha tace "Mama madara zansha banson naci abinci" Madaran da Baba Kesha a cup da zafinshi ma yamika mata da sauri ta karba tana murmushi tace "thank you Baba" hararanta Mama tayi tace "kwadayi Khairy, aikin ki kenan tun kina Yar kankanuwan ki sabida babban ki kullum yanashan dafaffen milk kema kikesha" mikewa tsaye Baba yayi yace "bagashi nan saisa she's so bright ba ga kwanya, milk is good for children barin ma Wanan na Shanu damuke sha dababu mix, bari naje nai salla" yakalli su Manaf da duk suka tashi suma sukawuce suka tafi masallaci, madaran ta shanye tass sanan ta tashi ta tattara kayayyakin dasukaci abinci takai kitchen sanan tadawo tana kallon Mama dahar lokacin take zaune inda tabarta tace "Mama tashi mutafi sama" ahankali Mama tace "wuce kitafi akwai wani program na wa'azi dazan kalla yanzu za'a fara" sanin Mama da kallon tashoshin wa'azi yasa tawuce stairs abinta tace "Mama gobe zani saloon kitso good night" ahankali Mama tace "Allah yakaimu Khairy" saida taji bude kofanta tashiga daki sanan gently tasa hannunta tadaura kan kujeran dake gefenta tana kokarin tashi tsaye amman takasa idanunta sunyi jazur kana ganinta kasan tana wahala ita kadai tasan metakeji, komawa tayi tazauna ahankali sanan tasauke ijiyan zuciya, hawayen daya zubomata takai hannunta tashare tanajan hancinta jin majina ya tsinke mata kafin tasauko da hannun ta share majinan, sanan ahankali tasauke hannunta kasa tana kallon tafin hannayen nata dasukai jajir kaman wanda yaji ciwo, ajiyan zuciya tasauke majina na gangarowa daga hancinta sanan tadaura hannunta kan hannun rigan tajashi sama tana kallon fatan jikin hannunta dasukai jaaa wasu kalan kuraje dasuka fitomata sunyi dabbare dabbare sunyi chaaaaa wanda is not just hannu ko'ina ajiki suka fesomata har wuya saisa tasaka Riga turtle neck dankar Khairy tagani, hannu takai tashare majinan dataji yana gangaromata yakai mata baki sanan tadaura hannunta kan baki tana kuka mai bala'in tabarai, she don't even know why she's crying, tana zaune a inda take aka turo kofan falon aka shigo dago kanta tayi takalli kofan Baba ne yashigo, kallo daya yamata yagane kuka take maida kofan yayi yarufe sanan yakaraso ciki ahankali yazo gabanta tsugunnawa yayi sanan yakai hannunshi yakama nata yakai kan kafadarshi kafin ahankali yadagata tashi tsaye tayi da taimakonshi dan ayanzu sai an dagata an kuma kwantar she can't really do anything da kanta sabida, har yakaita daki bai iya cemata uppan ba, zaunar da ita yayi akan gado sanan yashiga bayi yadauko baho da buta da kanshi yamata alwala sanan yasamata hijabi kwantar da ita kan gado yayi sanan yace "pray" gyadamai kai tayi da idanunta dasukai jajir sanan tashiga yin sallan isha'i yana zaune gefenta harta idar sanan yacire mata hijabin.
Kashe wutan dakin yayi sanan ya kwanta gefenta yarufa mata bargo kafin yadaura kanta kan kirjinshi yanajin yanda jikinta yay zafi sosai, murya chan kasa tana kara kankameshi tace "nagode Baban su Manaf" gyadamata kai yayi yakasa magana har lokacin, hannunshi takama

takai kan kirjinta ta manna sabida yaji yanda zuciyanta ke bugawa ahankali tace “kaji yanda zuciyana ke bugawa ko, tunanin yarana yasa haka, dan Allah ka kara aure banso daidai da sakan daya yarana suyi maraici kaji Baban Manaf” wata kalan huci kai zafi Baba yasaki ahankali yace “Maryam at this junction danake in my life banma da natsuwan dazan iya neman aure, yarana bazasu taba maraici ba, I am here, Baffan su nada mata har biyu they are sounded with mata they can call mom, please tunane tunanin nan will keep on eating u harsai kin daina, please concentrate on your health kinji, gobe zan kira Dr” girgizamai kai tayi tace “please no kabarshi yaje yay saving those that still have chance not me nariga naji ajikina my end is nea…..” Kankameta sosai yayi ajikinshi yana huci mai zafi wasu thick tears na neman fitomai daga idanu ya hadiye su ahankali yana jijjigata ahaka bacci yay awon gaba da ita saida ya tabbatar tai baccin sanan yatashi ahankali gyaramata bargo yayi sanan yawuce yashiga bayi alwala yadauro yazo yahau kan dadduma shafai da wuturi yayi yamata addu’a sanan yakoma gado kusada ita ya kwDanta.

21

Free page
Saida tai sallan isha’i sanan tacire hijabi kayan bacci taciro tasaka tana tunanin abinda yafaru dazu itada Aliyu, dan murmushi tayi sanan ta kashe wutan dakin ta kwanta.
Batasan mesaba tadade kwance rikeda wayanta tana kallon wayan every minute deep down she wish to hear his voice amman kuma bamataso tana tunanin what she wish for din akanshi abin is so so new for her she’s not just use to it, ahaka bacci yay awon gaba da ita wayan nakan kirjinta this is the first ever time in her life da waya ke bacci akan kirjinta.

Wuraren 12 nadare wayan nata yahau ringing afirgice tafarka tana daukan wayan daga kan kirjinta tana danna gefe dan yadena ringing yay silent, sanan takalli screen din da kyau ganin Aliyu Hydar batasan mesaba faduwa gabanta yayi, ahankali takai yatsanta dake dan rawa ta danna wayan na gab da katsewa takai kunnenta, murya chan kasa dake nuna alamun bacci tace “Hello” shiru yayi yana sauraron muryanta da bazaiyi karyaba tunda yake baitabajin macen da muryanta yamai dadi kaman nata ba, dan gyaran murya kadan yayi cikin wata kalan murya dashi kanshi baisan yanada itaba yace “Khairy” ahankali kaman wata Yar karaman baby tace “Uhm yajiki? Kasha magani?” dan murmushi yayi jikinshi namai wani iri jin muryanta like that so naked sabida baccin data fara, sanan har ranshi yaji dadin yanda ta tambayeshi yajiki koyasha magani, ahankali yace “yeah, Abba yamin allura” kaman zatai kuka dan ita harga Allah tanada tausayin mara lafiya tace “auuch that must have hurts, I hate niddles, sorry ko!” murmushi yayi ya gyadamata kai yace “thanks, you are sleepy”? Gyadamai kai tayi tace “Uhm” ahankali yace “alright good night, make sure you plug in your phone sabida yasami chaji, and say your prayer before sleeping okay” gyadamai kai tayi ahankali tanajin wani iri azuciyanta kaman tacemai sucigaba da magana karya tafi tadenajin baccin tace “okay night” tai maganan batare data cire wayan daga kunnenta ba shima bai katse wayanba sunkai kusan 10min ahaka sanan murya

chan kasan kasan makoshi yace “I love you Ummulkhair okay” gyadamai kai tayi ahankali tanaji hawaye nazuwan mata dabama tasan na meyeba but ko Allah yasani she just feel damn connected to him and vulnerable around him kaman ba itaba, katse wayan yayi hakan yasa taciro wayan daga kunnenta tarungume wayan hawayen na gangaro mata daga idanu, karan message dataji yasa taciro wayan daga kirjinta dasauri tabude wayan ganin message from Aliyu Hydar, bude messege din tayi da sauri. “Maisa nake sonki Ummulkhair? Well who am I to question faith? All I feel right now is I wanna spend my eternity with you, gud night Khairy” Takaranta message din kusan sau biyar sanan ta danna reply tai shiru tana kallon blank space din bamatasan mezata rubuta maiba, saikuma chan tashiga typing .
“I feel vulnerable and free around you, my heart beat whenever I hear your voice, duk sanda na rufe idanuna kai kadai nake gani, is that love?“
Yana ganin message din yay mata reply.
“time will tell Khairy na❤️”
Wani kalan murmushi tayi ganin yakirata da Khairy na sanan ta tashi zaune USB takamo dake jone da wall socket ta saka wayan nata kaman yanda yace tayi sanan takoma ta kwanta tadade kafin bacci yay awon gaba da ita.

Da asuba Baba yashigo yatadata saida yaga tashinta dan Khairy nada nauyin bacci sanan yawuce yatafi, bayi tashiga tadauro alawala tazo tai salla, koda tagama karatun Al Qur’ani tayi yau sosai wuraren 6 ta tashi, hijabi tacire yau ita keson yimusu breakfast tunda bazata school ba hakan yasa ta tashi tafice daga dakin tasauka kasa kitchen tashiga tana murmushi tace “idan matarchan tazo yau zataga na hutashe ta” lafiyayyen breakfsat tahada musu dan sinasir tayi da farfesu sai kunun Gyada dasu fried chips, saida tagama tsaf sanan tashiga fito da komi falo ganin Mama zaune afalo kusada Baba yauma sanye da kayan sanyi yasa ta ijiye kulan a tsakiyan falo ta tashi tana kallon Mama dataga tamata haske sosai Mama datake nan baka but tai wani irin haske, kafinma Mama tai magana Baba yace “ke wuce ki kawo mana abinci ga yayyinki nan zuwa” dasauri tajuya tana murmushi tace “Baba naga Mama tai haske ne takara kyau” kitchen tashiga takarasa fito dakomi takawo lokacin su Manaf sun shigo suma zama duk sukayi Baba da kanshi yadebo ma Mama Sinasir yana bata abaki, murmushi tayi tana kallonsu tana taba Ya Manaf, hararanta yayi yace “dalla kauyus” cigaba dacin abinci duk sukayi kowa yay shiru Baba da Mama ne suka fara gamawa sanan yakalli Khairy yace “Maman ki tace zaki saloon ko” gyadama Baba kai tayi tace “eh Baba, gyadamata kai shima yayi yace “yau rabonki da gidan Baffan ki kwana nawa” dan ajiyan zuciya tayi ganin yanda Baba ke kallonta sanan ahankali tace “an dade Baba” jinjina kai yayi yace “kije ki shirya kitafi saloon yanzu ana gamawa kije gidan Baffan ki ki gaidasu sanan kije gaida Matar Hafiz” ahankali tace “to Baba” “tashi kije” tashi tayi tai sama Baba yacigaba dayima Mama hira yau yanaso yakaita asibiti kotaki kotaso dan kwata kwata this days bata iya baccin dare ga kurajen nan kara fesowa suke ajikinta bana wasaba.

Tana shiga dakinta zama tayi kan gado sanan tadauki wayanta dahar lokacin bata cire daga chaji ba tabude message din Aliyu tagani around 5 na asuba.
“it’s time for subhi, wake up”. Murmushi tayi sosai sanan ta ijiye wayan tawuce bayi wanka tayo tafito direct gaban wardrope dinta taje wani riga da skirt na wani paper lace dinta tafito dashi da akamata dinkin jumper rigan yakai mata har gwuiwa sai skirt shikuma straight skirt daidai jikinta, mustard color ne lace din sai aka ni kayan dawasu bakaken stone, murmushi tayi taje tadaurasu kan gado sanan tazauna gaban mirror tadauki manta tana shafawa tana kallon fuskanta amadubi tana tunanin Aliyu, saida tagama shafawa sanan ta saka kayan dasuka mata bala’in kyau sosai, murmushi tayi black veil tadauka ta feffesa turare sanan tadauki handbag dinta ta jefe wayanta aciki tasa flat slippers yau tafito, afalo taga Baba kan doguwan kujera yana duba jarida Mama kwance tayi filo da kafanshi tana bacci yarufamata bargo, ganin Khairy yasa yadaura hannunshi akan lips dinshi yace “karki tadamin da matata tana bacci” turo baki Khairy tayi ashagwabe tace “Baba yanzu kafisun Mama dani Yar Autan ka” dan dariya tayi yamika mata wasu kudade yace “gashi Adamu na jiranki kije saloon kina gamawa ki wuce gidan Baffa” gyadamai kai tayi ta karbi kudin sanan takalli fuskan Mama dake bacci tace “Baba natafi” adawo lpy.

Saloon suka wuce direct baa wani bata lokaci ba wanke mata kan akayi sanan aka mata kalaba yan manya manya within one hour tagama tafito tashiga mota Adamu yatada motan zuwa gidan Baffa, dan tsaki tayi ahankali kawai dan babu yanda zatayi ne dabataje ba bata wani don zuwa gidan Baffa dudda tana bala’in don Baffa da duka yaran gidan, da Mum amman Ammi kwata kwata jininsu bai hadu ba batasan mesaba, tana cikin yan tunane tunanen ta ta iso gidan, Babban gida ne katoto, gidansu Babba ne but Gidan Baffan su is X2 nasu, mai gadi na ganinsu yahau murmushi yace “oyoyooo Khairy” murmushi itama tayi Adamu na parking tabude tafito dasauri mai gadon yazo wanda yake bayaro ba yace “munyi fushi wlh” dariya tayi tace “Baba Bala wlh school yaboyeni” tai maganan tana ciro kudi a jaka tamikamai 5k cikin kudin da Baba yabata karba yayi yace “nagode Yar albarka, Khairy mutuniyan kirki” murmushi tayi tajuya tana kallon cikin gidan, dankara dankaran flat ne guda uku agidan haka ajere, na farko wanda shizaka fara isa kafin kaje sauran yafi sauran biyun girma saina biyun dana ukun girmansu daya, da sauri saurin ta gudu gudu take tafiya wuce flat na farkon tayi tayi na biyun bude kofa tayi tana ihu. “Mummmmmm Mum” bin falon tayi da kallo daya hadu sai kamshin turaren wuta yakeyi stairs tayi da gudu tai sama daidai wata mata dazata kai 45 kefitowa daga wani daki cikin shiga na alfarma ta harari Khairy tace “ai nayi fushi wlh Khairy” wani murmushi Khairy tayi batayi wata wata ba taje dagudu tafada jikin Mum tana juyida ita cikeda murna tace “Mum I am sorry kinji, wlh school yahanani zuwa, Mum kinyi kyau iyyeee, ina Batool” turata Mum tayi tana nishi tana dafa kujera dan jiri taji tanaji tace “jama’a na shiga uku yarinyar nan zata kassarani” dariya Khairy tayi tajuya tai hanyar wani daki tace “nasan yarinyar nan tana bacci to baki isaba nazo” binta da kallo Mom tayi ganin kullum kara girma Khairy keyi, tana bude dakin taga wata yarinya da atleast zasu iya zuwa mate kokuma yarinyar tabama Khairy 1 zuwa 2yrs haka ta tashi zaune sanye da kayan bacci tana hamma tana hararan Khairy, yarinyar kamansu daya da Mom, wani tsalle Khairy tayi tafada kanta akan gadon yarinyar ta kwasa ihu tace “Mum kinga Khairy ko ni dagani ai wlh fushi nake dake konai chatting naki up baki dubawa kuma baki daukan calls” sakinta Khairy tayi tace “wlh Batool ni taba waya ma wahala yakemin balle

responding to calls or chat har gwarama kamin text message ina gani zan reply, but rabona ma dana shiga watsapp harna manta wlh" baki Batool tabude zatai magana Mom ta turo kofan dakin tashigo hakan yasa duk suka kalleta, Khairy takalla tace "kinje kin gaida Ammi Khairy"? Dan zaro idanu Khairy tayi sanan ta girgiza mata kai ahankali, daure fuska Mum tayi babu alamu kan fuskanta tace "Oya tashi kije ki gaidata, fast" tashi tayi kaman ruwan jikinta ya shanye, jakanta ta ijiye kan gadon Batool sanan tawuce tafito Mum tace "duk idan kin shigo gidan nan always ki shiga flat nata ki gaidata kafin kizo nan" gyadamata kai Khairy tayi sanan tawuce ta sauka kasa kafin tabude kofa tafice.

Ajiyan zuciya tasauke tana kallon kofan sanan gently tasa hannu tabude kofan wani lafiyayyen kamshin turare namata sallama ahanci, Babban falo ne sosai dayamafi na Mom girma, zaka dauka dakin wani president ne ko gwamna sunji kujeru da kayan gayu, wata Babbar mace ce mai kiba sosai a falon, kana ganinta you don't even need to ask twice kaga Hajiya irin cash HajiyUoyin nan.

22

Free page
Fara ce tass kana ganinta kaga bafulatana dan tanada mark na fulani a gefen fuskanta taci gayu na alfarma tana sanye dawani stone gown na exclusive mai pattern, kunenta zinare wuyanta ma haka yatsun hannunwanta guda biyu ne kawai babu zoben zinare ajiki manyan yatsun hannunta sune babu but sauran 4 4 fingers nata duka da zinare tana zaune akan kujera ta hakimce gawani iPad na Apple agabanta tadaura kan wani very very fine stool tana video call dabata iya ganin kowaye a screen din tunda ita daga waje take, hannunta matan rikeda wani white transparent bowl da ita kanta Khairy basuda irinshi agidansu an yanyanka strawberries da kiwi fruits kanana tanaci da fork, kokai waye kaga matan saika shiga taitayinka like duk rawan kanka irin matan nan ne da they don't even needs to show u su waye kana ganinsu kasan they're no nonsense powerful woman saisa haryau itadai Khairy bazata iya cewa ta tsani matan bane but kawai bata sonta, hasalima ita tsoronta ma takeji ko haukanta take agidan dazaran Ammi tazo wajen natsuwa take kaman ba itaba kodako da Baffa take magana, kuma agaban kowa ko agaban Baffa ne Ammi zata iya rufe kowa da fada baruwanta saidai in bakayi ba daidai ba.

Kallo daya tama Khairy ta dauke kai, ahankali Khairy tajawo kofan falon ta maida tarufe sanan takaraso cikin falon ta nemi waje ahankali akasa tazauna kanta akasa tana sauraron maganan datakeji na namiji daga iPad din ashagwabe data rasa na waye dan tasan muryan duka yaran gidan nan banda Babban yayansu da akace yana UK.

Ashagwabe yace “Ammi please niki kyaleni I will get the food nafita jibi fa yanda kitchen dina yadawo” hararanshi Ammi tayi tana kallon screen din tace “My friend dauki egg din break it ingani” cikeda gajiya kaman zai fashe da kuka yace “I don’t even know why I called u ki koyamin yanda ake soya egg ma” dan dariya Ammi tayi da saida Khairy dake zaune tadan saci kallonta dan bata taba ganin Ammi ko taji Ammi tai dariya haka ba lallai waye wanan itakuwa.
“Good boy Zayn, tom add a pinch of salt” Zayn! Zayn Zayn! Itako a inama ta tabajin sunan nan Ohhkay kaman shine sunan yayan nasu dake kasan waje ko yayan su Hafiz, tatabaji Baba da Baffa suna maganan.
Maganan Ammi ne yadawo da ita daga tunanin datake tace “bagashi nan ba kagama soya egg din amman da u are being lazy” dariya yayi sosai yace “Ammi nataba gayamiki u are the world best Mommy? No not just best you are the bestest Mom in this world Ammi na” dan murmushi Khairy tayi dan maganan yasa ta tuna da Mama haka take cema Mama world best, kiss taji yasakin ma Ammi ta wayan yace “love you Ammi bye” murmushi sosai Ammi tayi tace “I love you too Son, speak later, make sure u put on jacket kafin kafita dan u are having cold” “who am I to say no to this fine woman, Ammi this egg taste delicious bye” dasauri Ammi tace “kaci ahankali karka kwar…..” kafin takarasa maganan ya katse wayan murmushi tayi sosai kafin takalli bowl don fruits din hannunta ganin tacinye yasa ta kwalama mai aikinta kira. “Karima” da gudu mai aikin tafito daga kitchen jikinta har yana bari dan inhar Ammi takiraka sau biyu to kora ne, cikeda girmamawa tace “Hajiya gani” bowl din Ammi tamika mata tsugunnawa tayi sanan ta karba tace “akawo miki wani abune Hajiya”? Girgiza mata kai tayi tamata alamu da hannu ta tafi, wucewa tayi tawuce kitchen falon yarage daga Khairy dake zaune akasa ta takure waje daya saikuma Ammi data dauki wayanta Z-flip tana daddannawa kaman batasan da mutum awajen ba.

Ahankali kaman ba Khairy ba tsabagen yanda ta natsu tace “Ammi ina yini” batare da Ammi takalleta ba kota daina abinda takeyi da wayaba tace “yanzu kikaga daman shigowa gaida ni Ummulkhairy” girgiza mata kai dasauri Khairy tayi gabanta nafaduwa da kyar tace “Ammi kiyakuri bansan kin…..” “stand up and get out of this room!” Ammi tadaka mata tsawa dan she finds it insultive ace itace Babba agidan nan ko kare yashigo gidan nan yasan itane Babba an dole ne abata wanan girman balle Wanan Yar karaman yarinyan nan da aka haifa agabanta tashigo gidan nan saita fara zuwa ta gaida kishiyanta sanan zatazo nan, itafa Ammi is like that bata daukan raini kona waye gatada fada, komin girmanka zata iya daga hannu ta kwasama mari.

Tashi tayi jikinta har rawa yake itafa adai rayuwanta yanzu this woman is the only woman datake shakka aduniyan nan, duk iskancin ka baka iya kallon fuskan Ammi kace zaka mata rashin kunya kozaka maida mata da magana wlh bazaka iyaba Allah yariga yabata Wanan haiba da kwarjinin nanne, gabanta nafaduwa sosai idanunta sunyi ja tace “Ammi I am so……” “out!” Ammi tai maganan tana nuna mata kofa dasauri tai kofa zata bude aka turo kofan hakan yasa kofan yabuge mata hannu, baya tayi tana yarfe hannun dasauri idanunta sunyi ja Hafiz ne yana sanye da jeans da riga ganin Khairy yasa yace “Khairy kene agidan” hannunta yabi da kallo yace “ohh no sorry nabuge miki hannu ne” murmushi takakalo tana maida hannun baya

tace “Ya Hafiz welcome ina yini” sanan tabi tagefenshi tafice dasauri yabita da kallo kafin ya kalli Ammi dake danna wayanta abinta, maida kofan yayi yarufe yazo kusa da Ammi ya zaune yace “Ammi yaushe Khairy tazo” batare data kalleshi ba tace “maiya hanaka tambayanta kake tambayana” shiru yayi baice komi ba, saida tagama abinda zatayi sanan ta ijiye wayan takalleshi tace “how’s my granddaughter”? Murmushi yayi yace “she’s fine” “tafara shan nonon”? Gyadamata kai yayi yace “tafara Ammi, bata barin mu bacci, koda yaushe shan Nono take bata barin Moon tahuta”  dan dariya Ammi tayi tahararreshi tace “idan naga granddaughter na tarame dagakai har matarka will have to answer me I am very very serious Hafiz, anyway anjima idan yan suna sun watse akwai kayan dazaka tafi musu dashi” Gyadamata kai yayi yace “Ammi kinsan irin uban kudi da Ya Zayn yaturomin wai nabama Moon da Little niko sule biyar bai baniba bayan ni namafi mai jegon wahala” dariya Ammi tadanyi saikuma tai shiru kaman mai tunani ahankali tace “I can’t wait to see yaran Zayn shima” dasauri Hafiz yace “Ammi ai nagayamiki Zayn nadawowa kurikeshi kumai aure dan wlh  Ammi Ya Zayn bai shirya yayi aure ba” shiru Ammi tayi batace komi ba, kallon fuskanta Hafiz yayi ganin tai nisa a tunani yace “Ammi kema u believe what I am saying ko” “stop talking about ur brother Hafiz” shiru yayi saikuma chan yatashi yace “ina zuwa Ammi” baijira amsanta ba yawuce yatafi, awaje yaga Khairy gaban tap na wajen flower tana wanke fuskan ta da ruwa, bamata lurada shi ba yana zuwa ya tsaya agefenta yace “after all this years haryau baki gane halin Ammi ba kullum kikazo sai kinyi kuka common my friend, je daki ki dauko gyalenki keda Batool na kaiku gidan suna kowa nachan banda ku” murmushi tayi tajuya da dan gudunta tashiga dakin Mum, basu wani jimaba itada Batool suka fito datai wanka taci gayu motanshi suka shiga sai gidaUnshi.

23

Free page
Gidan Ya Hafiz yacika makil da mutane sabida suna, duka yaran Baffa na wajen, Yaran Baffa takwas, Ammi ta haifi hudu duka maza, Zayn ne babba, sai Hafiz, sai yan biyun da Ammi ta haifa maza da Hassan da Hussain, dukansu manya duk sun gama makaranta suma aure yau ko gobe, dan Ammi da Baffa sunyi aure tun suna yara, haihuwan yan biyun yazo mata da complication da dole aka cire mahaifanta gabaki daya data haifi sama da haka, itakuma Mom yara hudu ta haifan ma Baffa, mata biyu Batool da Zara’u wacce itace auta dan maza biyu kebin Batool kafin Zara’u, Abdulhamid da Abdullahi sai Zara’u, Zara’u ce kadai ke primary school su Abdulhamid yanzu suke SS1 boarding school, Batool itace ke university, dayake ana hutu dukansu suna gidan ga mamakinta harda su Ya Manaf da Maheer, dukansu sun hadu dasu Ya Hassan suna gaggasa raguna, mantawa ma tayi tayi kuka suka shiga shagalin suna ga Matan Ya Hafiz badai kirki ba sunan Moon yabita hakan yasa kowa Anty Moon yake cemata.

Sai Bayan sallan isha’i sanan suka baro gidan itadasu Ya Manaf, tagaji iya gajiya bacci ma tasoma abayan motan tadaura kanta kan kafadan Ya Maheer, bai tadata ba ganin tagaji yacigaba da danna wayanshi abinshi.

Bude musu gate akayi ganin motocin su Baffa yasa daga Ya Manaf har Mu'az din kowa yasha jinin jikinshi, parking sukayi hakan yasa tabude idanunta jin tsayuwan mota ta tashi zaune tana kallon compound dinsu sanan tabude kofa suka fito zata wuce Ya Manaf yace "ke ina zaki"? Dasauri tajuyo takalleshi kafin ma tabashi amsa yace "kibi Maheer kuje flat dinmu su Baffa sunzo magana akeyi" batai musu ba danta gaji tabi Maheer sukai flat dinsu shikuma da Mu'az sukai flat dinsu Mama da saurin su, bude kofa sukayi suka shiga sunabin kowa na falon da kallo, Baffa ne da Baba zaune kan kujera daya, sai Ammi da Mom zaune tareda Ammi akasa da fuskanta ya kukkkumbura kaman ba ita suka Bari this morning fuskanta looking normal ba, Mom na rikeda handky tana share idanunta dan takasa rike kuka itakuma Ammi idanunta sunyi ja dan ciwo is something dako enemy naka don't wish it on him, duk wanda yaga Mama saiya koka mata, kallonsu Mama tayi lurada kaman magana takeso tayi yasa Manaf yakaraso inda take hannunta yakama yarike yace "na tura Maheer da Khairy chan side dinmu Mama" ahankali yace "Mama meke miki ciwo"? Kafin ma wani afalon ya iya magana aka bude kofa aka shigo Dr ne, rikeda wata karaman Leda a hannu yana zuwa allura yahada yazo wajen hannun Mama yakama yamata alluran a jijiya sanan yakalli Baba da Baffa dake kallonshi yace "can I talk to you sir in private"? Girgiza mai kai Baba yayi yace "likita duk duniya banda family daya wuce Wanan circle din dakake gani anan u can say anything, I think we are ready to hear kome zakace right wife" gyadamai kai Mama tayi kaman ba ita ke wahala ba, huci Dr yayi yakalli Mama yace "alluran nan zai saukar da kumburin fuskan nan da wuyanta, but at this point all I can say is make ur wife as comfortable as possible dan koda ankawota asibiti babu abinda zamu iyayi kuma, daga yanzu kome zaku gani kawai hakuri zakuyi har Allah yayi ikon shi dan komi na hannunshi, just make her comfortable and happy, please kudena kuka agabanta kowani abu dan Allah, that's all bari nakoma hospital" tashi yayi yafita babu wanda ya iya cemai kala, Manaf yayi yayi yarike kukan nashi but yakalli Mama yaga yanda tadawo but dudda haka she's still faking smile musu kawai yaji zuciyanshi yay breaking, fuskanshi yakifa akan kujera kusada Mama sai kuka yake da Mu'az dahar lokacin shi yama kasa shigowa cikin falon yana wajajen kofa, ahankali Mama tasa hannu takamoshi wani irin rungumeta yayi sanan tamikama Mu'az hannu alamun yazo zuwa yayi shima kuka wiwi ajikinta babu wanda ke iya magana cikinsu har Maman dan kumburin da fuskanta da wuyanta yayi yasa bata iya magana.

Ranan dukansu suna zaune a falon nan babu wanda ya iya motsi har asuba sanan tai bacci, daki suka Kaita suka keantar da ita sanan Baffa ya kwashi iyalinshi suka tafi gida, suna shiga alwala yadauro kawai yawuce masallaci.

Wuraren karfe 8 nasafe yafito daga masallacin, gida yawuce dayake yana dakin Ammi ne nan yayi bata falo yasan ta kwana hakan yasa yay sama zuwa dakinshi, zama yayi kan wata kujera ta musamman dayake da ita adakin nashi datake nan kaman gado shiru yayi yana tunani, ahankali yamika hannunshi yadauki wayanshi yay dailing number dayay saving da Zayn dayake nan international number, wayan na gab da katsewa yadauka anatse yace "Abba" dan ajiyan zuciya ABBA yasauke anatse shima yace "Zayn nasan is late ko wajenku" gyadamai kai Zayn

yayi yana ture shishan dake gabanshi yatashi daga wajen yay bedroom dinshi zama yayi kan study chair nashi jin muryan ABBA somehow couple with the fact Abba baima Saba kiranshi da night ba most time da safe ABBA ke kiranshi ko darana, ahankali yace “Abba what is it are u okay”? Ajiyan zuciya Abba yasauke yace “Zayn Maryam matan Baffan ku batada lafiya, she’s seriously ill, inaso kome kakeyi yanzu kabarshi find any available flight dazaka samu dazai taho naija gobe be it PJ ko normal flight ne kadawo gida” tunda yafara school that’s tun lokacin dayake degree Abba baitaba demanding yadawo gida ba sai this time hakan yasa ahankali yace “okay Abba, but meke damun Mama”? Zayn yay tambayan ahankali dan yanason Mama she’s one humble woman da he admires alot dudda he’s not that close to her shi aduniyan nan ma only Ammin shi ne he’s close too. Ahankali Abba yace “she has blood cancer! Just few days takeda shi left inji Doctors, anyway just come home kayi few days Saika koma tunda baka fara finals dinka ba, good night son” “night Abba” yay maganan ahankali feeling down, yadade ahaka sanan yatashi.

Wuraren 8:00 na safe tabude idanunta ganinta adakin yayyinta saida abin yabata mamaki, murmushi tayi ta tashi zaune sanan ahankali ta sauko daga gadon lallai tagaji ko lace din jikinta bata chanza ba tai bacci, jakanta tadauka tawuce tafita daga dakin tana tafiya ahankali, flat dinsu tashiga babu kowa a falo sama tayi dakinta tashiga alwala tayi tai salla tukunna sanan tacire kayan wata doguwan rigan bacci ta tasaka sanan tafito direct hanyar dakin Mama tayi bude kofan tayi tace “Mama tun jiya nan ganki ba adakin su Ya Manaf na kwana” akan gado taga Mama ta jingina da hango ta sanya sweater tai fayau da ita da hulan sanyi akanta batasan mesa ba but gani tayi Mama tamata wani iri a idanu, karasowa tayi gaban gadon saikuma ta tsugunna takai hannunta tai tagumi tana kallon Mama, hararanta Mama tayi da kyar ta iya dagewa tabude bakinta tace “me haka”? Ahankali tana kallonta still tace “Mama wlh kin chanza, lips dinki are so dry, Mama wai bakida lafiyane kike boyemin kinyi wani iri eh sabida kinsan zan damu, bazan damu bafa Mama ai yanzu na girma saima na kula dake” dan shiru tayi tana kallon Maman dake kallonta tanaso tai magana amman azaban datakeji awuyanta yasa takasa, dasauri Khairy tace “zan damu kadan but zan kulada ke bakid lafiyane Mama” tai maganan idanunta na rau rau dan she’s really believing Mama bata da lafiya, ganin haka yasa Mama tamikamata hannu sanan tahadiye duk wani azaban datakeji tace “lafiyana kalau kawai gani nayi my little Khairy has grown so sooo big, yarinya na tai girma she can even take care of her Mama come here” dasauri ta tashi hannun Mama takama sai kawai tasaki hannun tafada jikin Mama ta kankameta sosai ahankali tace “Mama wlh ina bala’in sonki, without you bansan ya zan kasance ba, Mama ko idan na kalli wasu yaran ko sai inga they are not lucky sabida bakene Maman su ba, Mama u are the best Mama I the world, u are the coolest Mom, the softest, the sweetest, bakida fada, gashi kina sonmu, we are ur everything Mama, Mama kinsan menene” girgiza mata kai Mamantayi, Khairy tace “all mothers are mothers, but not all mothers are like Mamana, cus Mamana tafi takowa dadi, Mama kinga duk girman dazanyi I will always be ur baby, Yar autan ki, kinga na gama school nafara aiki zan dinga miki komi, Mama nasan kinje makka but zan kaiki makka da kudina da aka biyani albashi wajen aiki” dariya Mama tahauyi sosai dayasa Khairy wani kalan murna, sanan tace “Mama yauma ni zan miki breakfast mezaki ci na dafa miki” ahankali tace “fate nakeso” wani tashi tayi tasauka daga gadon sanan

tai juyi tace “then fate it is bari naje” tajuya dasauri tai hanyar kofa hartasa hannu zata bude kofan ahankali Mama tace “Ummulkhair” faduwa taji gabanta yayi hakan yasa ahankali tajuyo takalli Mama tace “naam” dakai Mama tamata alamu tazo dasauri taje gaban gadon, hannu biyu Mama tasa tai cupping face nata tana kallonta kafin ahankali takai goshinta saitin bakinta sanan ahankali ta manna mata kiss a goshin, murya chan kasa tace “I love you Ummulkhairy, Allah yamiki Albarka, Allah ya haskaka rayuwanki, Allah ya tsaremin ke” ahankali tana kallon fuskan Mama tace “Ameen Mama” takasa tashi, ganin kaman she’s trying to read something from Mamas face yasa Mama tace “Oya tashi kije kimin fate na yunwa nikeji Madam kokin fasane tunda kin tasani gaba kaman kin sami talavijin” da sauri ta tashi tana dariya tafice daga dakin.

Bana tagani agaban dakin murmushi tayi tace “good morning Bana natafi yima MaUma fate”.

24

Free page
This book is 1k to join my group pay 1k into 3107021073 aisha Muhammad first bank saiki turo evidence of payment ta watsapp number na 07012181461

Chat me up directly by clicking on this link
wa.me/+2347012181461

Wuraren 11 tagama faten daya cika gidan da kamshi, fito da kulan falo tayi Mama tagani da Baba zaune afalo saisu Ya Manaf sunama Mama hira, tashi Maheer yayi yatayata suka fito da komi tsakar falo sanan suka zazzauna karban na Mama Baba yayi da kanshi yadinga bama Mama faten bashi kadai ba harsu Manaf sunyi mamakin yanda tasha faten dan tadena cin abinci, tass ta shanye sai dadi Khairy keji saida kowa yagama sanan ta kwashe komi itada Maheer sukakai kitchen tarema sukai wanke wanken tace “lallai yau mutanen mutuncin ka na nan kusa Maheer” hararanta yayi yawuce yafita daga kitchen din itama tabiyoshi tafito, Baba dake kallonsu yace “go and get ready Khairy malamin ki zaizo by 12” sama tawuce agurguje ta shirya tafito falo lokacin ba kowa Baba yakai Mama dakinshi, by 4 malamin yatafi su Manaf suka fita da ita basu dawo gidan ba sai around 10 tana zuwa lafiyan gado tabi.

Gabaki dayan gidan yau basuyi bacci ba sabida yanda jikin Mama yay tsanani, amai tadingayi na jini both tabaki da hanci, jikinta yay zafi sai maganganu take dabama sa ganewa, saida safen nan bacci ya dauketa.

6 ta tashi tana kallon agogo mamaki ma take ya akayi take lattin tashi late this days, wayanta dataga yay haske yamika hannu tadauka 2miss calls tagani na Aliyu saikuma message dayamata bude message din tayi. “I miss you” murmushi tayi ta ijiye wayan sanan ta tashi tawuce bayi wanka tayo tareda alwala Dan yau tanada morning lectures, tana fitowa tasa kaya

tai salla sanan tabude kofa tafito su Ya Manaf tagani a falon sama kwakkwance kan kujera suna bacci, mamaki tayi amman ta tabe baki tai hanyar dakin Mama bude kofan tayi zaune taga Baba kan kujeran dakin yabude Al Qur'ani yana karantawa itakuma Mama na kwance kan gado tana bacci yarufa mata bargo, saida yakai ayar sanan ya kalleta tace "Good morning Baba" murmushi yamata yace "morning daughter, Mama is sleeping jiya dukanmu bamuyi bacci dawuri ba munata hira yayyinki na nan falo suna bacci suma" gyadamai kai tayi tace "eh nagansu" Gyadamata kai yayi yace "jeki breakfast yau Monday 8 kikeda lectures i want you to be serious kigama da good grade" gyadama Baba kai tayi sanan tajuya tafita tana kallon fuskan Mama dake bacci peacefully sanan tasauka falo ahankali, kitchen taje tea tadafa musu duka sanan ta soya chips zama tayi dinning zataci amman hakanan taji takasaci jikinta yamata wani irin sanyi kodan ita kadai ke yin breakfast dinne oho, tashi tayi tawuce sama tana kallon su Manaf da still ke bacci ta shiga dakinta dan shiryawa.

Shiryawa tayi tsaf cikin wani black abaya mai bala'in kyau tai rolling gyalen akanta ko kadan batai kwalliya ba but she looks kaman wata Somalian queen, jakanta tadauka sanan tafito, dakin Mama tabude takalli Baba dake karatu har lokacin tace "Baba natafi" saida ya idasa Ayan sanan yadago kudi yaciro yamika mata karba tayi tana murmushi tace "thank u Baba, kacema Mama natafi idan ta tashi bye" murmushi Baba yayi yace "to yarinyar Mama" maida kofan tayi tarufe yasauke ijiyan zuciya Noo yagaji Khairy deserve to know Maman ta is sick, he's tired of hiding it from her, bari Maryam ta tashi zai gayamata is time sufadi ma Khairy, Khairy is grown up she can handle it.

Fitowa tsakar gida tayi tana tafiya ahankali hakanan jikinta kawai yamata sanyi yasaki tarasa mesa kawai she's feeling sad and week ma yanzun nan, karasawa wajen motanta tayi Adamu na shiga itama tana shiga baya daidai sunajin horn mai gadinsu na budewa, motar Baffan ne ke shigowa gidan Hafiz ke tuki, sai motar Ammi biyeda su da driver ke parking sai kuma motan Mom, bude kofan motar tayi tafito tana murmushi da saurin ta tai wajen motan Baffa, daidai lokacin Baffa na bude baya yana fitowa yana mata murmushi yace "yan makarantan bokoko" dariya tadanyi tace "Baffa ina kwana, Ya Hafiz Baban Baby ina kwana, Laaaa Ya Hassan da Ya Hussain harda ku akazo yau" kafinma suyi magana Baba yace "wuce tafi school karki latti" yanuna mata motarta da Adamu yatada yana jiranta shiga motan tayi tana waving Mom dake saukowa daga motanta dan har yanzu motan Ammi bama abude ba kuma bamata iya ganin cikin banda driver shima ta glass din gaba taganshi dan motan tinted ne, jan motan Adamu yayi suka tafi nai gadi yamaida gate din gidan yarufe daidai lokacin Baba da Manaf suka fito.

Ahankali aka bude kofar motar Ammi, wani clean white kafane ya sauko dake sanye cikin wani hadadden sandals na Prada black, nails na kumban kafan are so fresh and white, gently yakarasa saukowa daga cikin motan yana yatsine fuska yana gyara bakin sun glasses na idanunshi na kampanin rayban, yana sanye cikin milk color yadi dayay dinkin jumper dashi daya bala'in amsan jikinshi, yanada tsayi dan wajen gabaki dayansu yafisu tsawo babu wanda baya

ganin kanshi, yanada cika dakuma fadin kirji, kana ganinshi kaga Ammi kaman tai kaki ta tofar saisa yafi kannenshi kyau dansu Hafiz da Baffa suke kaman, yanada wani irin black very very dark saje dake kyalli kaman na bature, lips dinshi is so pinkish, gashin kanshi a kwance suna shinning, hannunshi ya daura agogo Rolex akai, ita kanta Ammi anytime ta kalleshi she feels proud da Allah yabata Zayn as her son, Zayn is definition na handsome guy, kyakkyawan namiji da babu macen data isa tamai yanga, ganin Baba yataho wajensu yasa ahankali yakai hannunshi yazare eye glasses na idanunshi yadan sunnar da kanshi kasa Baba nazuwa cikeda mamaki yakama hannun Baffa yace “d’ana Zayn nake gani haka” murmushi daga Baffa har Ammi da Mom sukayi, Baffa yace “da asuban nan yashigo gida” anatse Zayn yace “ina kwana Abba”? Hannu Baba yabashi ahankali yasa nashi hannun cikin na Baba, daidai sukaji muryan Maheer yana ihu. “Babaaa” Dawani irin sauri Baba yasaki hannun Zayn yay ciki Baffa da kowama suka bishi sama sukayi, dakin Mama Baba yashiga yatarar da Mu’az yarike Mama dake aman jini sosai tai lakur babu karfi kodaya ajikinta, wajenta Baba yayi yakamata daga hannun Mu’az yadau tissue yana share mata bakin ganin tadena aman, shigowa dakin Mom tayi takalli Baba tace “Alhaji bari mu chanza mata kaya” girgiza kai Mama tayi ahankali tana rike Baba gam batare datai magana ba, kallonta yayi sanan yakalli Mom yace “abarshi tukunna” karasowa gaban gadon Baffa yayi yaja kujera yazauna yana kallon Mama dabata iya bude idanunta da kyau yace “Maryam mutafi asibiti”? Girgizamai kai tayi ahankali, ajiyan zuciya yasauke yay shiru, shigowa ciki Ammi itama tayi tasami gefen gadon tazauna ahankali tana kallon Mama murya chan kasa tace “kina bukatan wani abu Maryam mezaki ci?” Girgizama Ammi kai tayi hakan yasa itama tai shiru, ahankali Baffa yajuya yakalli Zayn daya tsaya chak abakin kofa shima yana kallon Mama sanan Baffa yajuyo da kanshi ya kalli Mama yace “Maryam ga Zayn dakika ce nakira miki yazo” dan yunkurowa kadan tayi da duka karfinta, dasauri Baffa ganin haka yasa yace “Zayn come” karasowa gaban gadon Zayn yayi ahankali sanan gently ya tsugunnawa gaban gadon yana kallon Mama dake kallonshi kallon dakasan baa hayyacinta takeba yace “Mama I am here” hannunta daya tacire daga jikin Baba data rikeshi gam gam jin haka yasa Baba yatayata , kama hannun Zayn tayi hawaye yazubomata daga idanunta sanan kadan tabude bakinta dasauri Zayn da zuciyanshi ta katse yace “Mama I am here mekike so tell me” yakai kunenshi saitin bakinta, magana tashigamai a kunne wanda harta Baba dayake rikeda ita baiji abinda ta Fadima Zayn ba sanan takoma jikin Baba ta kankame shi, Maheer dataga yana kuka sosai mara sauti abakin kofan ta kalla hannu tamikamai ahankali yataso yazo kawai kankameta yayi yahau kuka sosai ahankali yace “Mama dan Allah kiwarke, Mama please karki mutu kibarmu” motsi sosai bakin Mama yafara hakan yasa Baba ya janye Maheer daga jikinta kankame Baba tasake yi takama hannunshi tarike gam gam kaman dats the only thing dake mata dadi sanan cikin wata kalan murya dabata fita da kyau dan hakoranta sun datse tace “Baffa, Ammi, Mom, dukanku yarana ina rokonku gafara ku yafeni idan nataba bata muku, idan Ummulkhair…..” wani kalan nishi tayi tana kuka sosai dabayama fitowa sosai tace “kuce mata nace tayakuri tayafema Maman ta, i hide everything sabida nasan idanda tasan banda Ipy bazata dauki abin da kyau ba, Baban Manaf” tai maganan tana kankame Baba tace “ka kulamin da Khairy dan Allah, Baffa nabaku amanan Khairy da duka yarana, Khairy is fragile, and innocent please ku rikemin yarinyata amana ita nafiji araina, zanbar duniyan nan amman Khairy ce araina sabida ita kadaice diyata mace yayyinta maza ne” ajiyan zuciya Mama tasake saukewa sanan ahankali tace “idan narasu Khairy taki kwantar da

hankalinta kabata Littafin nan danabaka ka ijiye mata Baban Manaf"  gyadamata kai Baba yayi ahankali hawaye na taruwa a idanunshi Baffa ya bubbugamai kafa alamun karyay kuka, ahankali Mama tace "Baffa kamishi aure dazaran na rasu banson yarana su rasa uwa, Manaf kurike Matar da mahaifinku zai aura kaman ni kada kubata ciwon kai" gyadamata kai Manaf yayi, Ammi kallon Mu'az yayi dake bakin kofa tayi ya tsugunna idanunshi sunyi jajir tace "zo wajen mahaifiyar ka Mu'az" mikewa yayi tsaye da kyar shigowa yayi zuwa wajen gadon kawai yadaura kanshi kan gado yadaura hannunshi kan nata dan that's what Maheer da Manaf duk sukayi, yanda tazo tana nishi yasa Baffa ya gyadama Baba kai ahankali Baba yasoma karanto mata kalman shahada, saukar da kanshi kasa Zayn yayi, ahankali Mama ta amshi kalman shahadan karfe 12:03 daidai tacika da imani daidai lokacin Khairy ta tashi daga kan kujera sun gama lectures zasu fita jitayi kafafunta sunyi sanyi kawai tai baya zata fadi kaman tai paralyze Rabi dake bayanta ta tareta tace "ke Khairy are u okay" ? rike Rabi tayi tana taba kirjinta tace "gabana fadi yakeyi sosai kafana ba karfi" zaunar da ita Rabi tayi tace "kinyi breakfast kuwa"? Girgiza kai tayi hakan yasa Rabi da sauran kawayenta sukai dariya tace "yunwa ce muje kici abUinci".

25

Almost good 10min na silent ne yacika dakin, at this point Baba jiyayi kaman shima yamutum ne dan he could feel yanda hannayenta suka sassandare ajikinshi kasa koda motsi yayi hakan yasa Baffa yay taking over, daga Baba tsaye yayi, ahankali Baba yasauke kanshi kasa yana kallonta in disbelief, yadade ahaka sanan yakai hannunshi ya kulle mata idanu kafin yaja bargon yarufeta saikawai yazauna akasa dabas baimasan mema zaiyi ba dan he's still in shock idan ya kalli su Manaf daduk suke kuka saiyaji zuciyanshi yakara tsinkewa, kafadanshi Baffa yakama ya matsa hakan yasa ya fuzar da iska kafin ahankali yasa hannunshi yakamo su Manaf daya bayan daya duka yarikesu ajikinshi kam kam, juyawa Baffa yayi yakalli Hafiz dashima yay mutuwan zaune hakama su Hassan ahankali yace "Hafiz jeka dauko Khairy daga makaranta" Tashi Hafiz yayi ahankali yafice daga dakin tafiya yake but jiyake kaman iska ke kadashi yana tuna all memories dinshi da Mama shikenan daba danta data haifa ba balle kuma yaranta yaya zasuji.

A famfon gaban flower ya tsaya saida ya wanke fuskanshi tass sanan yakarasa wajen mota shiga yayi yatada motan yana kallon yanda mai gadi ke budemai gate he just wish yanada karfin sanar da su, amman ina motarshi yaja yafita daga gidan zuwa school  din su Khairy, har gaban department dinsu yaje accounting yay parking yakai kusan good 20min zaune acikin motan baida courage na facing Khairy, da kyar ya iya gyara mood dinshi sanan yakashe motan yafito yamaida yarufe yana kallon ko'ina kafin ya shiga ciki, Khairy nabashi labarin how popular she is a school so yasan ganinta bazai tabamai wahala ba, wasu yammata guda uku dasuka sauko daga bene yatare yace "hello ladies dan Allah kunga Khairy" daya daga cikinsu ce tace

“yanzun nan muka rabu da ita ga ajinsu chan wanchan floor din suna lectures” thanks yace musu sanan yawuce sama zuwa gaban class din excuse yay taking hakan yasa lecturer yafito dan yana ganinshi yasan Wanan baimai kala da dalibin makarantan nan ba, dawowa cikin ajin lecturer yayi yace “Ummulkhair” dasauri Khairy dake zaune ta kwantarda kanta kan table takalli lecturer tace “yes sir” waje yanuna mata yace “ana nemanki” tashi tayi ahankali tana daukan jakanta tafito tana tafiya kadan kadan dan sosai kafafunta basuda karfi ganin Ya Hafiz yasa tabude baki cikeda mamaki takarasa gabanshi da sauri tace “Ya Hafiz mekazo yi a school dinmu”? Hararan ko’ina yayi yay gaba abinshi tana binshi da sauri yace “me zanyi a school dinan naku Baffa yace nakawo ki” dasauri tace “Allah sarki Baffa yana ina tare kukazo kenan” “yana gida” yafadi kai tsaye batare daya juyo ya kalleta ba daidai suna karasa sauka kasa tana binshi abaya tace “Ya Hafiz wani laifin nayi ne wanan da dazu dasafen nan nabar Baffa agida mekuma nayi” juyowa yayi yakalleta daidai yabude mota yay murmushi yace “yarinya laifi dayawa” zare idanu tayi cikeda tsoro tace “hala saisa gabana keta faduwa wlh” tada motan yayi tashigo ganin duktai wani irin yasa yace “common babu abinda kikayi so relax” murmushi tayi dasauri tana sauke ijiyan zuciya but dudda haka she’s not just feeling ok hakan yasa tai shiru kaman ba itaba danda tacikashi da surutu shima shiru yamata baice mata komi ba ahaka har suka shigo layinsu, tundaga nesa take hango tulin mutane ata kofar gidansu maza na alwala hakan yasa ta gyara zama tace “Ya Hafiz maiya faru a anguwan mu”? Hango gate din gidansu abude awangale gakuma mutane yasa taji kawai gabanta nafaduwa ba kakkautawa, shiga cikin gidan sukayi daga baki baki Hafiz yay parking dan compund din yacika da mutane wasu tsaitsaye wasu zazzaune hango mai gadinsu da Adamu direbanta na kuka yasa kawai taji wani karfi yazo mata tawani bude kofan taduro juye juye tafara tana juwa juwa tanabin all mazan da idanunta kan sauka akansu tana kallo, kaman daga nesa taji dodon kunenta yaji wani magana. “Itace diyar Hajiyar data rasu” kafafunta da tun dazu sukai sanyi jitayi karfi yazo mata acikinsu kawai tahau gudu tai flat dinsu dataga kofar abude tashiga uwa an jefota tanabi kowa na falon da kallo matan anguwansu ne makotansu sunci mayafai some da charbi a hannu, stairs tayi dawani kalan mahaukacin gudu kawai neman mutum daya take dan gidansu she wants to know what’s happening idanunta ma sun rufe zuciyanta na bugawa batama ganin gabanta bum! Taji sunci karo da mutum da sauri takoma baya sanan tazaro idanunta tadaga kanta takalli wanda ke gabanta kaman yanda shima yake kallonta, batasan wayeshi ba but she could see kamannin shi da Ammi wani kayatyaccen kamshi nafitowa daga jikinshi, ahankali bakinta ke motsi numfashinta na neman gagaranta yi sabida yanda kirjinta ke bugawa ba kakkautawa ahankali tace “I……ina…….ina….”? Idanunta ne suka sauka kan gawar dataga an shimfide anan falon sama da aka suturta, sai yanzu ma talura da mutanen dake falon saman, Baffa, Baba, Ammi, Mom, Ya Manaf, Ya Mu’az, Maheer, Ya Hassan da Hussain Mama ce kadai batagani, still numfashinta na bala’in katsewa tabi idanun kowada kallo barinma Maheer dake kallonta yana wani irin kuka harda majina da she just think that answers her question, gently tadaga kafanta tana wani kalan kyafkyafta idanuwanta tana dambe da numfashinta dake kokarin daukewa tana kokarin tai taking just a step forward kawai tajita blank tai baya straight, wani irin tareta yayi dawani irin sauri Baffa yataso yana kallon Zayn daya tareta yace “Zayn kwantar da ita akasa she’s asmatic, Manaf get me her inhaler” dakinta Manaf yashiga yafito da sabon inhaler dago kanta Baffa yayi yadaura akan kafanshi yakai inhaler bakinta yana bubbuga kumatunta da kyar ta shaka tai wani irin nishi tadawo Baffa takalla tashi tayi zaune kaman bata hayyacinta tace

“Baffa ina Mama na”? Ganin Baffa yay shiru yakasa bata amsa yasa takalli Ya Manaf tace “Ya Manaf ina mama ya akayi banganta ba” saukar da kanshi kasa yayi, ahankali Baffa yace “Ummulkhair” wani irin gyadamaikai tayi jikinta ko’ina na ta rirrike Baffa, all this while Baffa has been mai taurin zuciyan but for the first time yaji Khairy kaman itace zata karyashi, dakewa yayi yace “listen to me Khairy, kinaji” gyadamai kai tayi jikinta har kafafunta bari suke ta rirrike Baffa wani irin zufa na keto mata agoshi, anatse yace “dukanmu anan da mazajen dakika gani a waje ke kawai ake jira domin inaso kima mahaifiyarki addu’a, Ummulkhair inaso kizama yarinya mai Imani da kaddara mai kyau ko mara kyau sanan kisani cewa kullu nafsin za’ikatul maut, i want you to calm down don’t shout and don’t cry kinga kinada Asma karkije kima kanki illa, Ummulkhairy Allah yayiwa…..” Baffa yadanyi shiru ganin yanda tazaro ta kwalalo manyan idanunta waje kaman zasu fado kasa yanda jikinta ke rawa zaka dauka ajikin injin markade take, daurewa Baffa yayi ahankali yace “Allah yayiwa mahaifiyar ki, Maman ki rasuwa Ummulkhairy”.

26

Wani kalan shuuuuu taji kunenta nayi, itadai tasan taji koke koke, taji maganan Baba, su Ya Mu’az har maganan Ammi tasan taji sama sama kafin chan kuma taga tabude idanunta tana kallon kowa dake kanta, kala batace musu ba rarrafe ta shigayi har zuwa gaban gawan zama tayi dirshan tana kallon farin likafanin hannu tamika zatakai tabude saikuma tai shiru kafin ahankali tasa hannunta taja likafanin kasa fuskan Mama ya bayyana tai wani haske ga alamun murmushi tanayi wani kuri tayi da idanu kaman tahaukace sai kawai idanunta aukahau mata yana kaman Mama murmushi take mata dariya tayi sanan tajuyo ta kalli Maheer dake kuka tace “Ya Maheer dena kuka kaji zoka gani ga Mama nan namin murmushi, Mama bata mutu ba bacci take wlh gashinan zoka gani” babu zuciyan wanda bai tsinkeba adakin ahankali takai bakinta saitin fuskan murya chan kasa tace “Mama Mama, world best tashi kiji, Mama ai bacci kikeyi ko” tasake shiru, ganin ko motsi Mama batayi yasa tai tagumi tana kallonMama tace “zan jira harsai kin tashi kinmin magana” ahankali Baba yataho yazauna kusada ita dasauri tajuyo takalleshi kaman mai karantan wani abu akan fuskanshi, kafadan Khairy yakamo sanan ahankali yace “Ummulkhairy mamanki has been bathling with cancer for so long, blood cancer bataso kisani cus tasan abinda zakiyi kenan idan kikaji she has few days left, u will not take it likely, saisa taboyemiki all this while mamanki has been sick, seriously sick amman taki yarda kisani duk ciwon da mamanki keyi taganki she will pretend she is fine” hawaye masu bala’in dumi ne suka zubo mata dasauri tasa hannu tashare, ahankali Baba yace “karki sakawa Maman ki hakan nan Khairy inhar she’s your world best, kimata addu’a tasan tabar ya tagari aduniyan nan muje mukaita makwancinta, your mum is tired she need rest, go and pray for your mum” ahankali Khairy tasake matsawa kusada Mama she can’t believe Mama ne nan kasa addu’an tayi sai kuka ahankali tace “Mama dan Allah dagaske wai kin rasu?”, zuwa yayyinta sukayi kawai rungumeta ahankali Manaf yace “Mama tarasu Khairy pray for her” Ahankali tace “Mama Allah

yajikanki Allah ya gafarta miki, Mama why did u leave me, shikenan bazan kara ganin ki ba, Mama maisa baki bari na rokeki kiyafemin ba, kullum ina cikin batamiki rai inta rashin ji, Mama Tayaya zan cigaba da rayuwa baki aciki Mama Innalillahi wa Innailaihi raji'un" tashi Baba yayi ahankali hakama Baffa dasu Ya Hassan da Hafiz dakuma Zayn zasu dauki Mama dan kaita waje salla, wani Zabura tayi zata tashi dasauri Manaf yariketa, Mom yabama ita tana wani kalan nishi hannu Mom tasa takarbi inhaler ta tace "Khairy Khairy" kaman zata haukace haka takeji da kyar ta iya kallon Mom tace "Mom na shiga uku, Mom Mama tarasu Innalillahi wa innailaihi raji'un, Mom wlh wlh ko…." kawai maganan yakakare takara suma, ruwa Mom tashafa mata a fuska tanamata addu'a, tafarfado ta sume tai having Asma attack haka tadingayi ahaka har akama Mama salla aka tafi da ita, Khairy bamatasan inda kanta yakeba tana jikin Mom, jikinta yay wani mahaukacin zafi dayasa Mom takalli Ammi dake zaune tanajan charbi tace "Hajiya kira Alhaji Dr yazo jikinta yay zafi dayawa, kuma suman nan datakeyi yay yawa" dan jim Ammi tayi sanan tadauki wayanta takira Baffa ta sanar dashi.

Bayan magrib Baba yashigo gidan tareda Baffa gaisawa yayi da matan dake falo dakemai gaisuwa sanan suka taho sama tundaga stairs yake kallon Khairy dake kwance akasa gatanan gatanan ne kawai baa cewa komi, tsugunnawa Baba yayi agabanta ahankali yadagota sharaf ta taso Mom yakalla yace "tayi salla kuwa"? Girgizamai kai Mom tayi, Baba zaiyi magana kawai tasaki wani sabon kuka mai bala'in tabarai dayasa kowa na dakin yazuba mata idanu tana taba zuciyanta kaman ta mutu takeji, kaman tai hauka takeji, kaman tadawo da hannun agogo baya takeji tama Mama duk abinda takeso batare datasa Mama fushi ba, duk su Baba magana suke mata amman harga Allah bata gane komi kunenta ma yadode, duk suna zaune ahaka tai kuka ta sume tadawo Dr yashigo gidan, allura kawai yamata aka samu tai bacci, Baba zai dagata Dr yace "ku kawo bargo kurufa mata, let her sleep anan" Baffa da kanshi yashiga dakinta pink bargonta da filonta yadauko yakawo Baba yakarba yasamata akarkashin kai sanan yarufa mata bargon yana kallonta yana kafin yasa hannunshi yacire rolling gyalen dake kanta ya ijiye gyalen agefe long kalaban ta suka bayyana duk akai shiru.

Hayowa saman sukayi duka yaran Hafiz na rike da jakanta daya dauko daga motanshi Dan dazu amotar tabari dakinta yabude ya shiga ya ijiye sanan yafito yasamu gefe daya yazauna afalon, suma su Hassan da Manaf suka zazzauna, ahankali Zayn ke hayowa stairs din da duk yay wani irin tsayawama waje yayi yin wata waya saisa bai shigo tareda kannen nashi ba,hayowa yayi kallo daya yama Khairy dake bacci akasa da aka lullube da pink bargo yadauke kai sanan yawuce gefen Ammin shi yazauna akasa tareda daura kanshi kan cinyanta hakan yasa tadaura hannunta ahankali tana shafa kanshi, kallon yaran Baffa yayi yace "kutashi kutafi gida mu muna nan" cikinsu duka babu wanda yay motsi, ahankali Ammi dake shafa kan Zayn tace "Son tashi katafi gida kahuta yau ka dawo daga tafiya" girgiza mata kai yayi ahankali yace "I don't wanna go Ammi" kallon Hafiz Baba yayi yace "wuce katafi gidan ka Hafiz" girgiza kai yayi shima yace "Baba ai basu kadai bane kanwarta damai mata wanka duk suna nan" addu'a Baffa yayi dukansu sanan aka shafa, aka zauna turus duk wanda yaga su Baba da yaranshi saiya tausaya musu abinda kuma yahana yaran Baffa tafiya kenan Dan idan suka tafi gidan zai

musu wani iri kai mutuwa batada dadi! Baba da Baffa sauka falon kasa sukayi sukuma yaran duk suna wajen kusan ahaka bacci ya kwashe kowa daga Ammi da Mom da duk suke kan kujera zuwa su Manaf dake bacci rabi rabi falon yarage only Zayn ne baiyi bacci ba dayake tattaba wayanshi maganan da Baffa da Baba keyi akasa yanaji.

Motsin da Khairy tayi cikin bacci yasa yajanye kanshi daga waya yazuba mata idanunshi kusan sai yanzu nema yake mata a very good kallo tunda yazo, hawaye yaga suna gangarowa daga gefen idanunta pink lips dinta na motsi sosai cikin bacci ta kankame pink bargon da aka lullubeta dashi tana maganganu da kana gani kasan mafarki take. “Mama Mama wai kin mutu? Ai baki mutu ba ko, bansan menama su Baffa dasukemin karya ba, Mama zansha madara, in dauka, Mama Mama Maaaaa….” Wani dogon ijiyan zuciya tasauke na kuka kalabanta daya na saukowa kan fuskanta, dauke kai yayi daga kallonta shi dabama danta ba mutuwan yajishi balle yaran data haifa, he can’t even imagine loosing Ammi God no please, Allah ya sassauta musu koma mesukeji a zukatan su.

Wuraren 4 daidai tabude idanunta daga kwance datake tana kallon saman dakin da kallo, the first thing daya fado brain nata is mutuwan Mama, ajiyan zuciya tasauke tana assuring kanta cewa mafarki ne tayi, juyoda kanta tayi tabi kowa na dakin da kallo, Hafiz nakan kujera yatakure yana bacci, Ya Manaf na zaune shima kan kujera yana bacci, Ya Mu’az ma haka Maheer ne kadai akasa yana bacci, sai Zayn da kanshi kekan kafan Ammi yana bacci shima kaman wani auta, Mom dake saitin inda take akan kujera tana bacci itama ta kalla ajiyan zuciya ta sauke zuciyanta na tsinkewa but she’s still in disbelief, bargon jikinta ya yaye ahankali sanan tamike tsaye da kyar cikinta namata wani irin ciwo na yunwa dan jiya all through babu abinda tasa abaka, tadade tsaye tana rikeda cikinta kafin ahankali tafara tafiya jelan kalaban kanta na lilo abayanta tai hanyar dakin Mama, ahankali tasa hannunta tabude kofan kaman a kunnen Zayn danshi baida nauyin bacci hakanan any movement kodan kara daza’ayi yana tashinshi da sauri yajuyo da kanshi yakalli kofan tana tsaye bakin kofa tarike handle na kofan da hannu tana kallon cikin dakin gashinta na lilo.

Ko’ina na dakin takebi da kallo idanunta namata gizo daga taga Mama tafito daga bayi tana mata murmushi saita ganta kan dadduma tana mata murmushi, saita ganta kan kujera tana zaune rikeda littafin zikirin ta saikuma chan taganta kan gado kwance tana mata murmushi, hannayenta duka biyun tadaga takai kan idanunta ta murza idanun da kyau sanan taciresu tasake kallon dakin amman babu kowa ciki dawani irin sauri ta shiga dakin tai bayi budewa tayi dasauri tace “Mama kina ina” ganin babu kowa abayin yasa tadawo dakin tana juye juye kalle kalle bakinta na rawa tace “Mama kina ina”? Gadon tayi ta yaye bargon kan gadon, jini jini datagani a zanin gadon wanda na aman jinin da Mama tadingayi ne yasa taji kafafunta sun kara sanyi kawai tayi kneeling awajen takifa kanta akan gado sai kuka kaman ta kwakulo zuciyanta tayar takeji kukanta sa duk wani wanda zaiji tanayi kuka yake, kowa na falon tunda tafara kiran Mama suka farka amman babu wanda ya iya shigowa yacemata wani abu abar Khairy tai kuka

dan ita akama Wanan mutuwan.

Da kyar Manaf ya iya tashi yashigo dakin gaban gadon yazo kusada ita yadaura hannunshi akan bayanta murya chan kasa yace “Khairy stop crying and pray for Mama, kinga tun jiya baki magrib ba balle isha’i, muje dakinki kicire rigan nan shower kiyi salla and pray for Mama, Mama tariga tarasu……” wani kalan ihu tayi da saida gidan gabadaya ya amsa. “Mama bata rasu ba, Mama batada lafiya babu wanda yafadamin, mena muku? Ni yarinya ce dazaa boyemin uwata batada lafiya, nama Mama laifi dayawa bansami dama na roketa gafara ba, nabar Mama agida natafi school nadawo kucemin Mama tarasu, babu wanda yagayamin Mama batada lpy saidai kugayamin tarasu, Mama b…….a…” maganan yasoma gagaranta sabida mugun attack na Asma daya taso daukanta chak Manaf yayi yafito da ita daga dakin yana karban inhaler da Maheer kebashi, Mom tace “please ku kulle dakin nan tadena zuwa ciki” kwantar da ita kan gadonta yayi yasa mata inhaler cus nishi take kaman zata mutu da kyar ta shaka, Mom tashigo dakin takalli Manaf dake kanta tace “tafi Manaf” fita yawuce yayi daga dakin.

27

Free page

Da taimakon Mom tai wanka ta chanza mata kaya zuwa wani simple atampa doguwan Riga sanan tasata tai salla itadai tasan tai salla amman bamatasan metakeyi cikin sallan ba kotana karatu dakyau kobatayi jikinta yay munannan zafi, kwanciya tayi kan dadduman Mom tazo dagata tayi tacire mata hijabi tace “kwanciya akasan ya isa haka nan kar sanyi ya shigeki zoki kwanta akan gado” Mom ta kwantar da ita kan gado ta kwanta lamo kan gado hawaye nabin idanunta suna sauka kan katifan, hannu Mom takai tana sharemata hawayen ahankali tace “Khairy nasan mekikeji aranki yanzu haka amman kisani kome yan uwanki sukayi da mahaifinki sabida mamanki sukai hakan, shi mara lafiya ana so ana cikamai wishes nashi, barinma mara lafiya kaman na mamanki, Mamanki ita ta haifeku duka idan she choose ke kadai zata boyemawa rashin lafiyanta believe me tanada reason nata maybe taga Kece mai weak zuciya u can not take it, and believe me yanzu idan nagayamiki Wanan abin dakike yi yanzu is not what she wants Khairy, be strong dan yanzu Kece maman su yayyinki, kinyi tunani what Baban ki is going through yanzu haka, matarshi dasuka tsufa tare bata kuma dawanne zaiji dake koko da rasuwan da akamai? Khairy ki kwantar da hankalinki kinji, bari na sauka kasa na hadomiki ko shayi ne kisha” Mom tashafa kanta kafin ta tashi daga kan gadon tawuce tafita daga dakin su Manaf zasu shiga tahanasu.

Ranan haka aka wuni Khairy gatanan gatanan ne, takasa cin komi kotaci amai straight, rasuwan Maman ta yabi gari bama asan ya kawayenta sukaji ba before you know it kawayenta suka cika gidan harda Besty duka dakinta aka kawosu kallonsu kawai take kaman ta haukace,

babu wanda take amsa gaisuwan shi, duk wanda yazo gaisuwan bazaiyi kuka ba amman dazaran kaga Khairy saikai kuka kawayenta sunyi kuka sunyi kuka harsun gaji, Besty tunda tazo take rungume da Khairy da jikinta kaman wuta tana kuka da kyar ta iya tauna kosai guda da Besty tabata abaki ahaka dare nayi suka tafi.

Hakanan yaji ya bala'in damu cus yakira Khairy yanaganin miss calls din daya sunkai 20 maybe but all ba amsa same with text messages nashi ba reply, he don't know why but kasa jurewa yayi tashi yayi daga office din nashi yadauki car keys dinshi yafito wajen police station din, motarshi yashiga yajata yafice daga police station din, he don't even know why he's driving to layinsu Khairy but yasan zuciyanshi keeps pulling him to go there dudda bawai shiga gidansu zaiyiba, ahaka har yazo layin, kofar gidansu yagani tsaitsaye da maza sanan gashi an bude gate an saka canopy a compound din ga tabarmai maza sun zazzauna, hakanan yaji kirjinshi yabuga dum! Waje yasamo yay parking motarshi yadade zaune sanan ahankali yafito ya tsaya jikin motanshi yana kallon jama'a dake shiga da fita gidan yakasa zuwa, yana tsaye awajen Ya Mu'az yafito tareda wasu friends nashi dasuka zomai gaisuwa, shiga motansu sukayi suka wuce daidai zai juya yakoma ciki idanunshi suka sauka kan Aliyu dake tsaye jikin motanshi yay folding hannunshi yana kallonshi tunani yafara inda yasanshi kafin daga baya kanshi yagayamai police man din ranan nan takowa yayi zuwa inda Aliyu yake tsaye yamikamai hannu dasauri Aliyu yabashi hannu yace "meke faruwane wucewa zanyi naga mutane gate abude shine nai parking, what happen?" Aliyu yasake tambayan Ya Mu'az heart nashi nabugawa, ahankali Ya Mu'az yace "Maman mu ce ta rasu, muje nakaika ciki kaman Baba gaisuwa" Ya Mu'az yay maganan yana gaba binshi abaya Aliyu yayi har zuwa cikin gidan har inda Baba yake kan tabarma tareda Baffa dawasu abokanen arziki Mu'az yakai Hydar, Baba nada gane mutane kallo daya yana Hydar yace "Aliyu" hannu yamikama Baba anatse yace "Baba yahakuri, Allah yajikanta Allah yamata rahama" ahankali Baba yace "Ameen Ameen Allah yayimaka Albarka" sanan yakalli Baffa yace "Wanan ne officer dana gayamaka ranan da Khairy tai shirmen nan yadawo da ita gida" dasauri Baffa yace "Allah sarki, yaro mai hankali angode Malam Aliyu, gashi Ummulkhair ba lafiya da an kirata kamata gaisuwa nasan zataji dadin hakan" gyadama Baffa kai yayi yakasa magana kirjinshi na bugawa dum dum, kafin da kyar ya iya tashi yamika musu hannu yace "bari nakoma wajen aiki" addu'a su Baffa sukamai sosai sanan yajuyo Ya Mu'az biyeda shi har waje zuwa wajen motanshi sanan Ya Mu'az yace "mungode Allah bada lada" murmushi yamai tareda gyadakai har Ya Mu'az yajuya zai wuce yaji yakasa hakura ahankali yace "Ya Ummulkhair take"? Juyowa Ya Mu'az yayi yakalleshi cikeda damuwa yace "not good at all" yay shiru yana kallon Hydar din dayaga ya tsaya yaki tafiya yana kallonshi kaman yana jiran yace wani abu ahankali Ya Mu'az yace "Mama had cancer all this while Khairy bata sani ba cus Mama tahana afadi mata, as it is now kaga yau uku this is the third day da abinci bai shiga bakin Khairy ba, she's not handling the whole thing very well, she's not doing okay, kuka suma asma attack duka yahadu mata kaman zatai hauka takeji, kasan she's very very close to Mama, naji Baffan mu yana cewa yau zasu wuce da ita gidansu Dan gidan nan is not helping her at". Gyadamai kai Aliyu yayi idanunshi sunyi ja yakasa magana juyawa Ya Mu'az yayi yCawuce ciki.

28

Free page
Shiga motan Aliyu yayi dasauri sanan yatada motan wani irin jan motan yayi da bala'in gudu yayi tafiya mai bala'in tsayi sanan ya gangara gefen hanya ya kashe motan kafin yawani irin daki siterin motan yace "noooooo" he just wish zai iya shiga cikin gidan yaganta, wayanshi yaciro dasauri idanunshi sunyi ja baimasan mezaiyi ba text yashiga turamata.
"Rashin uwa is not something I wish for even my enemy, but muna plan dinmu ne Allah is the master of all planners. Ummulkhair nasan mekikeji, I know abinda zuciyanki kije because I was once there, just know this wherever Mama is she's resting, tana cikin jannatul Firdaus, I want you to calm down, pray for Mama, cry but just little sabida nasan it hurts alot, babu wanda zai gane how it hurts sai ke, so cry little and pray lot, be strong for me Khairy, and kisani cewa I am here for you koda bana wajen presently but my love and my heart is there with you, I love you to the moon and back Ummulkhair, Allah ya yassaremiki wanan nauyin dakikeji aranki"
Turamata text din yayi yadade ahaka sanan yafuzar da iskan yatada motanshi yawuce.

Bayan sallan magrib Mom da kanta tashigo dakin, Khairy na kwance kan gado tadagota tana kallonta tawani irin rame tace "muje gidan mu, bayan kwana biyu saiki dawo nan bari nakawo miki hijabin ki" bin Mom kawai take da idanu tadauko mata hijabin tazo har gaban gadon tasake dagota danta kara kwanciya tasaka mata hijabin dagota tayi tasauko kasa baya tayi kaman zata fadi dasauri Mom tariketa tana kallon fuskanta idanun idanunta sukai suntum har lokacin jikinta da zafi ahankali tace "kiyakuri Khairy, kiyakuri" fita da ita Mom tayi tana binta luuu kaman wacce tasoma zarewa duk su Baba da kowa na tsakar gida wajajen mota Mom tafito da ita binta da kallo sukayi, dafa Baba Baffa yayi dayaga yana kallonta cikeda tausayi yace "don't worry she will be fine" karasowa wajen Mom tayi tasata acikin mota bata musu duk yanda akai da ita, kowa shishiga mota yayi Baffa yana su Baba sallama sanan suka tafi da ita.

Suna kaiwa gidan parking suka yi, Zayn yafara saukowa daga motan Ammi side dinshi yawuce dan yagaji he needs rest, Mom kuma tafito da Khairy dahar lokacin take yanda take, Ahankali Baffa dake kallonsu yace "kitafi da ita side dinki tunda akwai Batool" gyadamai kai Mom tayi tawuce da ita itakuma Ammi tadaure fuska tawuce abinta Baffa yabi bayanta yana amsa wayan daya shigo phone nashi.

Kafin suma iso Batool tabude musu kofa tana kallon Khairy dan ita all this while bataje gidan rasuwan ba tana gida tana kulada kannensu, zata fashe da kuka ganin Khairy Mom ta

ballamata harara hakan yasa tahadiye kukan taya Mom riketa sukayi sukai sama da ita zuwa dakinsu zaunar da ita kan gado sukayi kwanciya tayi sharaf Batool zatai magana Mom tace “ki barta jekimin tea yanzu zanzo nabata tasha yauma bataci komiba” Gyadamata kai Batool tayi tafito daga dakin tsayawa tayi nan bakin kofa tana kuka ahankali, bude kofa Mom tayi tafito ganinta yasa Mom taidan jim sanan tace “kinsan wahalan da akasha kafin Khairy tadaina kuka? Tana ganinki kina kuka yanzu zata fara” Mom tai maganan tana janta daga wajen kofa sukai stairs, cikeda da bala’in tausayi Batool tace “Mom kaman na Khairy mai surutu ba Mom kaman tazare Innalillahi, duniyan nan babu komi cikinta Mom, look at Khairy damuka sunan Ya Hafiz da ita muna wasa muna rawa, Mom I can’t stand seeing her this way” ahankali Mom tace “then u should support her as ur sister, show her love abinda take bukata kenan yanzu, sanan mudena nuna mata muna tausayinta, kijata ajiki u will help her tadawo daidai” gyadama Mom kai tayi, Mom tace “good yanzu jekiyo mata tea kizo kibata tasha, lemme go and shower” wucewa tayi zuwa kitchen da sauri.

Tea Batool tahado mata tadaura cup din a tray tadawo dakin nasu tana kwance sharaf agadon yanda suka barta, ijiye tea tayi tahayo gadon tadagota ta tashi zaune ahankalli murya chan kasa tace “Khairy zoki sha tea bakici komi ba” tsare Batool tayi da idanu da dazaran kaga yanda take kallon Batool kasan bata hayyacinta don ahankali tace “ina Mama”? Danne kukan datakeji tayi zatai mata magana taji kukan yatokare mata wuya hawaye yazubamata dasauri tashare daidai Mom tashigo harararanta Mom tayi tadauki tea tace “tashi kibani waje” da kyar Mom tasamu ta kurbi tea sau biyu sanan takara kwanciya dagata Mom tayi takaita bayi alwala tamata tasata a dadduma salla tajirata tayi Allah dai ya karba sanan tadagata, wani sabon kayan bacci na Batool Mom ta dauka tasamata bayan tacire mata atampan jikinta spaghetti hand ne dan kaman shimi yake iya guwiwanta ya tsaya mata pink color dan itama Batool nasan komi pink, dawowa tayi kaman wata Yar baby roba akayan looking damn cute, kaita Gado Mom tayi ta kwantar da ita tarufa mata bargo itama kaman abinda takeso kenan rufe idanu tayi dasauri, Mom tazauna abakin gadon tana tofamata addu’a bude kofa akayi Baffa ne yashigo yana sanye da jallabiya ganin Mom namata addu’a yasa ya tsaya yana kallonsu saida tagama sanan yace “tai salla”? “Eh tayi” “what about abinci” Baffa yatambaya anatse, ahankali Mom tace “tasha tea kadan ba laifi, shine na chanza mata kaya nakwantar da ita, karka damu she will be fine nan bada jimawa ba” murmushi Baffa yayi yana kallon Mom ahankali yace “thank you mace tagari” yakalli Batool dake bayanshi tai zuru zuru yace “dama kuka zaki dingayi kika dameni nadawo da ita nan kisami Yar uwa” dasauri ta girgiza kai tace “Bazan karaba Abba” murmushi yayi yashafa kanta yace “jeki kwanta” sanan yakalli Mom yace “jeki kwanta kihuta wife muje narakaki” murmushi tayi ta tashi, itakuma Batool taje gefen Khairy ta kwanta itama tashiga bargon Baffa yakashe musu wuta tareda jawo musu kofa sanan yaraka Mom zuwa dakinta kafin yafito yasauka kasa yakashe wutan falo sanan yaja kofan yawuce side din Ammi.

Wuraren karfe biyun dare tabude idanunta tass jin muryan Mama nakiran sunanta. “Ummulkhairy!” Hakan yasa tabi dakin da kallo ganin Mama tsaye jikin kofa tana sanye da

Atampa mai kyau tai lullubi yasa ta yaye bargon data rufa dashi tawani tashi tsaye tai wajen kofan bakinta na motsi, gani tayi Mama tabi ta kofan tafice bude kofan tayi dasauri tafita ko'ina duhu but she could see Mama natafiya akan stairs dan fararen kayane ajikinta, hanyar stairs din tayi itama dasauri ganin Mama tai kofa tafice yasa itama tai kofan, hannu tasa tabude kofan tafice batare data rufe kofan ba, tsakar gidansu kaman rana sabida ko'ina hasken lantarki tashiga sauka daga stairs din gaban kofan tana mika hannu ganin Mama tamata nisa tai hanyar gate murya chan dake cikeda nuna alamun bacci tace "Mama jirani!"

Zaune yake kan daya daga cikin wasu hadadun kujerun dayake nan barandan flat dinshi, irin hadadun kujerun basket dinan da ake sawa a garden, dagashi sai wani gajeren wando dayakaimai guiwa da farin singlet tass yadaura kafafunshi kan class table din wajen yana shan shishi, tunda yadawo naija saiyau yasamu yakeshan shisha, yama fito waje ne yanasha sabida kar dakinshi yakama kamshin gashi Abba nashigowa dakin dakannenshi duka, jin karan kofa an bude flat din Mom dan daga flat din Mom sainashi at this hour of night yasa yasaki pipe din shishan kasa dasauri yana mika hannu yana sauke shisha pot din daga kan table din at the same time yana kallon kofan yaga wanda zai fito daga dakin.



Free page

Ganin yarinyar nan da Mamanta tarasu dayaga antaho da ita gidansu dazu dazasu dawo dan he can't even remember her name yasa yadan ware idanu yana binta da kallo yanda take sauka daga kan staircase din gaban flat din Mom, babu takalmi akafanta babu dan kwali akanta kalaban kanta na lilo atsakiyan bayanta, daga ita saidan rigan bacci pink mai hannun taliya daya tsaya a guiwanta, ganin yanda take tafiya one one as if she's trying to hold something yasa yadanja karamin tsaki yace "God am I a baby sitter now" jin tace Mama kijirani tai hanyar gate yasa yadanja tsaki yatashi dasauri ganin tai hanyar gate, dawani irin sauri yasha gabanta batare dayace kalaba yay folding hannunshi a chest dan ihu yaso yamata but to his biggest suprise gani yayi gabaki daya idanunta are close is she sleeping walking or what? Yatambayi kanshi daidai ta iso gabanshi babu any tazara tsakanin shi da ita tsayawa yayi yana kallonta just to feed his curiosity yaga mezatayi, wani kalan heart melting murmushi tasaki daya bala'in lobar da dimples dinta all the 2 yabayyana set na white teeth dinta, pink lips dinta nawani kalan shinning kafin ahankali takai duka hannayenta biyun tadaura kan hannunshi daya rungume a kirji takama cikin muryanta kaman na baby tace "Mama kinjirani, Mama I miss u, karki kara tafiya ki barni kinji Mama" tai maganan tana warware hannunshi daya rungume a kirji tasaukar da hannun kasa sanan gently takara tako one more step ta shige cikin jikinshi tai wrapping two hands nata around his back tawani kalan kankameshi tana sauke ijiyan zuciya dahar cikin brain

dinshi saida yaji ahankali tace “Mama bacci” tunda yake in his life what he just felt now baitaba jinshi ba, sandarewa yayi hannunshi sauke akasan batare daya iya komiba yanajin saukan ijiyan zuciyanta akirjinshi yana kallon tsakiyan kanta da yanda gashinta ke lilo sabida iskan dake kadawa da yanda heart dinta ke biting each beat yana jinshi anashi heart din, yakai kusan 2min ahaka she’s still holding him tight batare data kara magana ba, ahankali yadaga hannayenshi dayaji sunyi sanyi kaman basa functioning kuma yakai saitin hannunta abayanshi zai kwance yanda tadaure hannun abayanshi, kankame hannun tasakeyi saikuma yaji tasaki kuka dabaida kara ko kadan. “Baran sakeki ba Mama, ina sakinki cemin zasuyi kin mutu, Mama nakusan haukacewa da suka fadamin haka ni nasan baki mutu ba, ni ajikinki zanyi bacci anan dakinki zanyi bacci, I will not allow u to leave me ever again and go” yanda hawayenta kebin kirjinshi yasa yaji zuciyanshi ta tsinke shifa baicika tausayin mutane ba but for the first time jiyayi yarinyar nan tabashi tausayi sosai ahankali yakomar da hannunshi batare daya rabata dashi ba, yadan dade ahaka sanan gently yadan duka tareda ita yasa hannayenshi the two yadauketa ajikinshi kankameshi tasake yi gamgan tana kara gyara zaman kanta akirjinshi yana kallon fuskanta saida tagama sanan ahankali kaman yadauki Kwai yafara tafiya har zuwa flat din Mom, shiga ciki yayi daman kofan abude yake yay stairs da ita yana mamakin yanda batada nauyi kaman yadauki paper, dakin Batool dayagani a bude ya tabbatar mai daganan tafito, shiga cikin dakin yayi dudda ko’ina da duhu but he could see sabida hasken window dake nuno compound nasu gently ya tsugunnawa kaman yanda ake kwantar da baby haka ya kwantar da ita kan gadon zai zame hannunshi yaji ta chapke hannunshi da sauri tana sheshekan kuka kaman yanda jarirai kema mamansu takai hannunshi kirjinta ta kankame sosai kaman idan tasaki hannunshi something will happen to her, wani dauuuu yaji a brain dinshi kaman an watsa acid a alkaline environment, dan gabaki daya a boobs nata ta kankame hannun nashi, he could basically feel sign na her sleeping nippy, karya fizge hannun tahau kuka ne this is middle of night a ganshi adakin nan saisa yakeyi ahankali, gently ya tsugunna jikin gado, wani kalan zufa yaji yana ketomai shi kanshi baisan mesa ba this is not the first time yake feeling boobs na mace why is hers different, why so much effect, ahankali yakai dayan hannunshi yadaura akan fuskanta yana shafa kumatunta he don’t even know what to do samin kanshi yayi da hura mata iskan bakinshi a fuskan wani irin ijiyan zuciya ta sauke tasaki hannun nashi kadan bakaman yanda ta kankame hannun a kirjinta da farko ba, ganin haka yasa yacigaba da hura mata iskan yana shafa kumatun nata dayaji yamafi na jariri taushi sanan gently yashiga janye hannunshi kafin yay nasaran janye hannun duka sanan ya dauke hannun kan fuskan nata dawani irin sauri yatashi yafice yaja kofan nasu ahankali sanan yasauka kasa yafice waje abinshi.

Wuraren 6 tafarka daga bacci daga Mom har Baffa daya shigo dubasu da asuba saida sukaji dadi ganin yanda tai bacci sosai yau dan this last few days dudda ana mata allura bata tabakai war haka bata tashi ba 4 ta tashi ko 3 nadare ma.
Kalle kallen data shigayi yasa Mom data shigo dubata tace “Khairy ya akayi me kike nema? Kin tashi” Dasauri zuciyanta na bugawa fast fast tace “Mama ina take?” Shiru Mom tayi tana kallonta hakan yasa tafashe dawani irin kuka tace “wlh ba karya nake ba Mom naga Mama

adakin nan takwana tareda ni I was even holding hannunta sabida idan kuka tashi kugani, kuma tace bazata kara tafiya tabarni ba” hannu Mom tasa tadafa cinyanta ahankali tace “Khairy idan aka rasu an rasu kenan mutum baya dawowa, sabida rasuwan Mama na ranki saisa kike mafarke mafarke, Mama tarasu, you had a dream about her, tashi kije ki dauro alwala kiyi salla” tashi tayi ahankali tana goge hawayen dasuke zubomata tai bayi, fitowa tayi daure da alwala tai salla, da kyar tasha kunun da Mom tabata shima kadan sanan Mom tabarta da su Batool da Zara’u daketa musu surutu Khairy na kallonsu kuri kaman tazare itakuma Mom ta sauka kasa.

Knocking akayi tareda shigowa dakin, Zayn ne yana sanye da kananun kaya yay kyau yana zuba wani uban kamshi, ganinshi yasa Mom tace “Zayn shigo mana zoka zauna” karasowa yayi cikin falon cikeda girmamawa yace “Mom zan tafi” dasauri Mom tace “harzaka koma” ahankali yace “eh something come up dole nakoma dama 1week naso nayi amman bazai yuba” murmushi Mum tayi tace “Allah sarki to Allah kiyaye hanya, Aida nasan yau zaka tafi dana maka su dambun nama wlh yanzu sai yaushe kenan” dan shiru yayi yana tunani sanan yace “let’s just say 2month intotal nagama komi” ahankali Mom tace “Alhamdulilah Alhamdulillah komi yay farko zaiyi karshe Allah bada sa’a Allah ya kiyaye hanya” Ameen yace yana tashi har waje Mom tarakashi Baffa dasu Hafiz suka daukeshi a mota har zuwa airpDort.

30

This book is 1k pay into 3107021073 aisha Muhammad first bank. Saiki turomin evidence of payment ta watsapp number na 07012181461.

LAST FREE PAGE
Bayan 3 weeks!
Yau 3 weeks kenan chip chip da rasuwan Mama, an dage sosai da addu’a akanta she’s very very much better yanzu, tadena koke koken nan she’s doing everything dakanta saidai she hardly speak, kome aka cemata saidai ta gyadakai tariga ta yarda Mama tarasu and babu abinda zata iyayi dazai dawo da ita, har yau bata iyacin abinci at all, saidai kadan kadan kuma shima liquid, once in a while Besty nazuwa har gidan Baffa dubata dan su Ya Manaf nema suka kawota gidan tasani, sanan Baba yabata number shi yanzu ma haka ance gobe zata koma school danta kira Baba next week zasu fara first semester 400 level exam sauran ta one semester tagama school hakan yasa aketa shiryamata har sababbin dinki Baffa yamata hadadun gaske Mom ma haka, just to cheer her up amman ina bin kowa take da ido dakuma kalman godiya shikenan.

Yau tun safe Mom dakanta ta shigo dakin ganinta zaune kan dadduma yasa tace “laaaa yar nan

Oya maza tashi ki shirya yau kinada lectures 8 kika zauna yanzu har 7 yi maza tashi ki shiga bayi" batai musu ba tashi tayi tai bayi wanka tayi tafito, gani tayi Mom tamata arranging kayan dazata saka akan gado, wasu Riga da skirt ne na atampa cikin sababbin da aka dinka mata orange color ne atampa yanada flowers yan kanana brown, sai brown gyale tahada mata jakan makarantan ta da book sai wayanta da tuntuni aka kawomata gidan bata taba tabawa ba shima Mom dukta saka mata, shiryawa tayi tsaf, Mom tashigo dakin dauke da tea da chips tana kallon yanda kayan suka mata kyau dudda tarame sosai takalli kitson kanta tace "satin nan zamu kwance kan nan ayi wani kitso Khairy" takarasa ta ijiye abincin akan carpet sanan tadauki dan kwalin kayan tamata dauri mai kyau kafin tadauki tea tabata, karba tayi da kyar ta iya shan dan kadan sanan ta ijiye, ita kanta Mom batama iya tursasata taci abinci tashi tayi tadauki jakan a hannu da gyalen ahankali tace "natafi" binta Mom tayi tace "dan Allah Khairy kiyi karatu da kyau kinga jarabawa zaku fara next week karki fadi" Baffa suka gani afalo shima wa'azi yamata sanan yakaita har mota saida tashiga sanan yama Adamu alamun yatada motan yatada suka tafi, titi kawai takebi da kallo, jitayi hawaye ya gangaro mata dasauri ta share, she use to kullum saitaga Mama take tafiya school, school sukakai Adamu yay parking ganin taki tashi yasa Adamu yace "tashi kije class Khairy" kukan datake rikewa taji yazo mata fashewa da kuka tayi sosai tasa gyalenta akan fuska tana kuka shiru Adamu yayi takai kusan 20min sanan ta share fuskan nata da gyalen idanunta sunyi jazur tabude kofa tafita tana tafiya kaman iska ya kadata tafadi tarame babu abinda yarage ajikinta sai nono da hips, su kadai ne basu rame ba but wuyanta duk kashi idanunta sun fada ciki sosai, ahankali take tafiya yan makaranta su natareta suna mata gaisuwa gyadamusu kai kawai take tana wucewa dasauri dan bataso taita kuka ta tarama kanta mutane ahaka hartakai aji da lecturer ma aciki, baa hanata shiga ba hakan yasa tashiga taje tasami chan baya karshe chan tazauna ko abu daya bata ganewa ahaka aka gama lectures din lecturer tafita by 10, basuda wani lectures kuma sai 2, zagayeta yan ajin sukayi ana mata gaisuwa gyadamusu kai take tana danne zuciyanta, ganin yanda takeyi yasa class governor dinsu yace "dan Allah kubar Khairy tahuta let's go guys" fiffita daga ajin suka shiga yi, su Amal sukace "tashi muje cafe Khairy" ahankali tace "kuje ina zuwa" dan jim sukayi suna kallonta babu maison yatakurata hakan yasa duk suka tafi ajin aka watse ita kadai tarage aciki hakan yasa takifa kanta akan desk tahau kuka ita kanta she wants to stop the cry amman bata iyawa tadade ahaka ita kadai a class kaman aljana kanta akife akan table, kaman daga sama taji ance "Ummulkhair!!" Awani irin hankali take dago kanta daga table kafin tadaura jajayen rinannun idanunta kan Aliyu dake tsaye agaban ajin yana sanye da uniform na yan sanda yana kallonta, yarame shima idanunshi sunyi wani kala yana mata kallonda only heart dinshi zai iya sanar da mai kallon ke nufi, jitayi duniyan ya tsayamata chak duk wani bakin ciki emotions, tausayin kanta da sauransu sun taso mata sun tsayamata awuya, jikinta harwani rawa yake ganinshi dan she can't believe shine, wani irin tashi tsaye tayi tana kallonshi kaman yanda yake kallonta kallon dayana mata zuciyanta nafassaramata dawani irin gudu gyalenta na faduwa akasa tai wajenshi kaman dama shitake jira batai wata wata ba kawai tawani kalan fada jikinshi sai kuka sosai as if she ne dama asalin wanda takeso tama kukan, ahankali ya lumshe idanunshi yana feeling kukan datake in every single bone of his flesh, hannayenshi yadaga gently yay wrapping nasu around her back kafin yakai bakinshi saitin kunenta murya chan kasa yace "I am here for you Pickle, I am here" sake kankameshi tayi sosai cikin kuka tace "Ya Aliyu Mama….." murya chan kasa dake nuna he's with her, he's feeling what she's feeling yace "I

know Pickle" takai almost 3min tana kuka ajikinshi sanan ahankali yacirota daga jikinshi yana kallon yanda take kuka hannunta yakama zuwa first kujeran dake ajin zaunar da ita yayi sanan ya tsugunna agabanta still yana kallonta, jikinta ko'ina rawa yake na kuka, hannunshi yasa a aljihu yaciro clean handkerchief dinshi yakai kan fuskanta yafara share mata hawayen murya chan kasa yace "shiiiiiii" shiru tayi tana kallonshi still, tass yashare mata fuskan harda hancin sanan yamike tsaye yay inda take zaune a ajin da, tsugunnawa yayi yadauki gyalenta daya fadi a tsakar class din sanan yakarasa yadauki handbag dinta sanan yadawo har zuwa inda take a zaune, gyalenta ya yafa mata aka yasauka har kan kirjinta sanan yamika mata hannunshi yace "let's go" kallon fuskanshi tayi kafin ahankali tasa soft hannunta cikin nashi yariketa gam sanan suka fito daga class din suna tafiya ahankali sai kallonsu ake amman ko ajikinshi har zuwa parking space, gaban motan yabude mata zama tayi tana kallonshi da jajayen idanunta sanan ya maida kofan yarufe kafin yazagayo yazauna wajen mazaunin direba yarufe motan yatada motan yafice daga school din da ita, sunyi tafiya mai nisa sannan taga ya tsaya gaban wani eatry ya shiga batasan meya siyoba yadai bude bayan motan ya ijiye komi sanan yadawo yatada motan, wani waje yakaita ita kanta duk zamanta a Abuja batasan wajen ba, duwatsu ne masu kyau ga kamshin ruwa awajen da alamun akwai water fall ciki, parking yayi sanan yakalleta yace "I am coming" fitowa yayi yabude baya yadauki ledan daya siyo musu dawani babban dadduman dayake dashi mai taushi sanan yashiga wajen baiwani dade ba yadawo, bude inda take yayi yasake saka hannu yadauki jakanta sanan yamika mata hannu ahankali tasaka nata ciki, saukowa tayi yamaida motan yarufe sanan suka shiga wajen, cikin dutse ne kaman cave sanan ga ruwa atsakiyan wajen yana gangarowa daga dutse babu kowa wajen, wajen is so serene and peaceful bakajin karan komi saina tauntaye dana karan ruwan dakuma kamshin ruwan dutse dakakeji.

Zaunar da ita yayi kan dadduman sanan shima yazauna yana facing nata, ledan yabude yaciro take away na biryani rice da rosted lamb sai ruwa mai sanyi daya siya yabude, ahankali yasa spoon din aciki sanan yadebo abincin a spoon yakai bakinta yana kallonta jitayi zuciyanta yawani tsinke wani sabon kuka yazo mata ahankali tashiga reramai kukan, jaaa idanunshi yayi sanan gently ya girgiza mata kai bude baki tayi yasamata abincin taci saiyau tasan ashe tanajin yunwa, kadan tarage abincin all through harta koshi kuka take, yanabata abaki tanaci tanamai kuka sanan yadauki ruwa yabata shima sha tayi sanan ya ijiye.
Ijiye komi gefe yayi sanan ya matso kusada ita ganin taki daina kukan cikin muryan lallashi da murya dake nuna asalin so da tsantsan so yace "I know! and it's okay I am here for you okay" gyadamai kai tayi tana sauke ijiyan zuciya, hannunshi yakai yakamo hannunta ahankali yadaura hannun nata kan kirjinshi yana kallon idanunta yace "can you feel yanda zuciyana ke bugawa sabida yasan kina cikin damuwa?" Gyadamai kai tayi ahankali murya chan kasa yace "I came to your house tun ranan ban sake samin kwanciyan hankali ba because I know my Pickle is not fine, I lost sleep, I lost peace, bana iya komi sabida ke, kinason zuciyata tabuga because of you ne"? Girgizamai kai tayi ahankali tanajin maganganunshi har a bargon kashinta, murya chan kasa yace "I lost my Mom when I was 25yrs, I know what u are going through Khairy, but if anything yasameki bazan iya rayuwa ba I will die, I love you alot, Ummulkhair I Love You" wani sanyi taji ya ziyarci zuciyanta each magana dayake gayamata zuciyanshi datakejin bugunshi nakara tantance mata cewa gaskiya yake fadi, ahankali yace "when I lost my mum I was

depressed but as time goes on nazo ma fahimci this is not abinda mamana keso, she wants me happy, tanaso na cigaba da rayuwana, tanaso nai fulfilling dreams dina and above all she wants me happy and praying for her, Pickle abinda kikeyi yanzu is that abinda Mama kiso"? Girgizamai kai dasauri tayi alamun aa ahankali yace "to mesa kike hakan"? Lips dinta na rawa kuka na neman kufce mata tace "because banajin magana and nasa Mama fushi dayawa, halama saisa taki fadamin she had blood cancer" tafashe da kuka tana kallonshi girgiza mata kai yayi yace "Mama taki gayamiki she's ill ne because you are her youngest daughter Khairy u can't handle it, and Mama wants wats best for you, that's is the reason, trust me pickle you are not stubborn, ke y'a ce dakowani parent will wish to have, I know Mama is so proud of you, ta haifi selfless and fearless yarinya that can stand for her self a ko'ina, karki kara tunanin Mama is angry with u iyaye basa iya fushi da yaransu, and Wanan kukan dakike da rashin cin abinci shizaisa Mama tai fushi dake, cus instead of kinata addu'a kina using time din to cry and not eating zai baki wani sabon ciwo u want to be sick" girgizamai kai tayi dasauri ahankali yakai hannunshi yakama dayan hannunta yace "promise me daga yau kin chanza, u will stop all this, take care of yayyinki and your Dad, do you have any idea yanda sukeji ga rashin Mama gaki" sake girgizamai kai tayi yace "promise me you will change daga yau, u will always pray for Mama, study well and pass exam dazaku fara next week, did u promise" gyadamai kai tayi ahankali tace "Uhm I promise" murmushi yayi he feels kaman yarungumeta yasata ajikinshi and just stay like that forever" ahankali yace "smile for me i finds it healing is my therapy, smile" dan murmushi kadan tayi ita kanta tamanta the last time datai murmushi.

To jama'a anan nakawo karshen free pages zan barku da tambayan nan ALIYU NE KO ZAYN NE???
Dan samin amsoshin nan kucigaba da bina awanan Littafin mai suna ALKAWARIN ZUCIYA!
Dan son cigaba da karanta Wanan littafin zaka iya turo 1k ta 3107021073 aisha Muhammad first bank saiki turo evidence of payment ta watsapp number na 07012181461 sainai adding naki a group din danake posting.

Dan girman Allah badan niba kubiya ku shiga group ku karanta. Support me🥰

You can chat me up directly by clicking on this link
wa.me/+2347012181461

Thank you
M Shakur🥰

3️⃣1️⃣

WARAKA TEMPLE
wa.me/+2347042419516

Waraka temple gidan maganin kowacce irin cuta da izinin Allah
Karin niima da dadi
Karin dandanonki da duminki
Matsewarki ki dawo yar Sha shida
Gyaran nono
Sa megida sambatu
Sa kyauta
Maganin Sanyi
Da sauran magungunan damuwar da ke addabar mata zaku samu a waraka temple ku tuntubemu a no waya ko Instagram.

Murmushi yamata sanan yamika hannunshi yadauki jakanta wayanta yaciro yakunna yace “this phone should always be on” gyadamai kai tayi ahankali tana kallonshi Ya Aliyu is just….bamatasan taya zatai describing nashi ba, he’s just everything datake so, he’s so cool, calm, religious, selfless, caring, loving and above all very handsome. “will you marry me?” Kaman daga sama taji yajefo mata tambayan dan tayi nisa a tunanin shi while looking at him, ware manyan idanunta tayi da sun soma washewa, ijiye wayan nata yayi akan cinyanshi dayagama saita mata dan komi na ciki ya hargitse sanan yadaura mata mayun idanunshi akan nata, ahankali yace “zaki taimaki Aliyu Hydar ki aureshi yazama mijinki?” Batasan mesaba but wani kalan bala’in kunya ne taji ya lullubeta dasauri takai hannayenta duka biyun tarufe fuskanta dashi tana murmushi sosai kaman ba Khairy ba, dan murmushi yayi ganin yanda tambayan shi yabata kunya, matso da fuskanshi saitin fuskanta data rufe da hannayen ta yayi kaman mai whispering yace “I want to go and seeaBaba fa” girgizamai kai tayi tareda makemai kafada batare data bude fuskanta ba hakan yasa yace “what”? Awani irin shagwabe kaman Yar baby one year tace “ni karkaje wajen Baba yanzu” dasauri yana kallon long yatsun hannunta masu bala’in kyau da fararen kumbunanta kal kal yace “sai yaushe” ahankali kaman bataso tafadi maganan tace “sai nagama second semester exam dina nagama school” dan shiru yayi kaman mai calculating dan yamai nisa, dan yatsine fuska yayi yace “to but will you marry Aliyu”? Shiru tayi kaman bazatai bashi amsaba yana kallonta sai chan yaga ta gyadamai kai wani irin murmushi yayi ya dunkule hannu yadaki iska yace “yessssss!” Juyamai baya tayi akunyace tana daukan jakanta ahankali tace “mutafi inada class by 2” dan murmushi yayi ganin kunyanshi takeji dan tace zata aureshi, yace “ok” tashi tayi ahankali tafice daga wajen murmushi yasakeyi ya kwashe dadduman dasauran abubuwa yafito, discarding nasu yayi sanan yazo yasameta tsaye jikin motan tana kallon wasu tsintsaye dake wasa jikin bishiyan wajen, ga gidajensu birjik a wajen da alamu kiwonsu ake awajen, abayanta ya tsaya yana kallon tsuntsayen shima murya chan kasa yace “u like them”? Gyadamai kai tayi da sauri batare data cire idanunta daga kansu ba, wani mutum dakaman shine mai gadin wajen yakira da hannu ko kadan bamata lura ba dan hankalinta nakan tsuntsayen datake kallo, kawai gani tayi mutum yafito dawani basket cage na gidan tsuntsu yazo wajen bishiyan cikin sauki taga yakamo guda biyu yana kokarin sawa ciki, dasauri tace “Ya Aliyu meyake yi wanchan mutumin”? Ahankali yana tsaye kusada ita yace “I don’t know let’s see” saka tsuntsayen yayi a basket din sanan yataho dasu gabansu da sauri

yamikama Aliyu yace “officer gashinan macen da namijin ne kaman yanda kace” hannu yasa ya karba sanan ya ijiye akan motan Khairy tabishi da kallo, hannu yatura a aljihu yaciro wallet kudi dayawa yaciro yamikama guy din godiya yamai sanan yawuce, hakan yasa yamaida wallet din aljihunshi kafin ahankali yadauki cage din yajuyo yana kallon Khairy dake kallonshi yamika mata yace “take” wani cute smile tasaki sanan tasa hannu takarba tana kallonsu tana murmushi sanan tadago kanta takalli Aliyun dake kallonta tace “they are so cute, they’re so tiny and adorable” matsowa kusada ita yayi yana kallonsu shima acikin cage din sanan ahankali yace “mace da namiji ne, this is Aliyu Hydar” yanuna mata namijin, sanan yanuna mata macen da yatsa yace “and that’s the lady, Miss Ummulkhair” wani kalan murmushi tayi she’s so happy bata taba zatan dan tace tanaso zai sayamata ba harma guda biyu, fuskanta yakalla yanda take murmushi tana kallonsu, ahankali yace “are you happy Pickle”? Juyoda fuskanta tayi takalleshi, gyadamai kai tayi ahankali tace “I am very happy” “mutafi to”? Gyadamai kai tayi da sauri tace “a ina zan ijiye idan zan shiga class”? kofar motan yabude mata shiga tayi dan shiru yayi kaman mai tunani sanan yace “I will keep them for you harki gama class, how does that sound” “perfect” tafadi tana girgiza case din dake jikinta dan suyi attempting flying wani dadi taji tace “yayyyy they’re flying, Ya Aliyu kalli” kallonsu yayi yana mamakin yanda abin kesata murna, maida kofan yayi yarufe yanajin wani kalan sanyi aranshi, duk wani damuwa da kunci dayakeji yatafi ganin yanda take murmushi looking happy.

Shigowa motan yayi yatada yaja motan kusan every minute and second saiya juyo ya kalleta yanda take wasa da tsuntsayen sosai, yana bala’in son Khairy shi kanshi baisan adadin son dayake mata ba, ahaka har sukakai school dinta around 15min after 1 na rana, parking yayi hakan yasa takalleshi daidai shima ya kalleta, dan sunnar dakanta tayi akunyace yace “2 zaku shiga class ko?” Gyadamai kai tayi, what time zaki gama lectures yau, ahankali tace “5” dan ajiyan zuciya yasauke yace “yanzu jeki salla a mosque kafin ku shiga class, I will come back later nakawo miki birds dinki kitafi dasu gida, what do u want me to get for u when coming back?” Girgizamai kai tayi tace “babu komi” jakanta tadauka sanan tadan saci kallonshi ganin kallonta yake kaman yauya fara ganinta yasa tajuya da sauri tareda bude kofan tafita tafara tafiya dan murmushi yayi yakafeta da ido yana kirga step dinta waiting for something, kaman taji kiran da zuciyanshi kemata juyowa tayi dudda motan is tinted but samin kanta tayi damai waving hannu dan tasan yana kallonta sanan tajuya da sauri tawuce feeling so happy da shi can not even deny, bata taba sanin she can feel this happy ba bayan rasuwan Mama gashi she’s feeling it.”

Kaman yanda yace tayi hakan tayi masallacin su tawuce tai salla abinta sanan tazauna ganin 2 batai ba, jin tunanin Mama yazomata rai yasa tadaga hannu sama tamata addu’a sosai ta shafa sanan tafito ganin 2 saura, class dinsu tawuce su kansu Amal mamaki sukayi ganin tazo kujeran dasuke tazauna harma tana karban note dinsu tana dubawa kafin lecturer yashigo wani kalan dadi duk sukaji, shigowa lecturer yayi yafara musu lectures and Alhamdulillah tana gane komi. Wuraren 3 suna zaune a ajin taji wayanta na vibrating hannu tasa ajakanta taciro ganin message ne daga Aliyu Hydar yasa dasauri tabude.

“Are u moody or teary? Concentrate on lectures okay, by the way this birds dinan naki are naughty, sai kuka sukemin sun tsaneni obviously sunsan I am not their owner”
Bakaramin dariya tayiba dataga text dinshi reply nashi tayi.
“I am happy thanks to Ya Aliyu Hydar, tell my birds not to cry, Mommy takusa gama lectures bye”
Saida tai sending message din sanan tafarabin messages din dayake turamata tun bayan rasuwan Mama tana karantawa one after the other tana murmushi, Amal dake kusada ita ta mintsileta tace “Khairy wai waye Wanan new boyfriend din naki” tai maganan tana leken abinda take dawaya dasauri tarufe wayan tamaida jaka tareda murguda mata baki ta maida hankalinta kan lectures din da akeyi.

32

Five daidai suka gama lectures, fitowa tayi suka jero tareda su Amal, kafin su wuce itakuma tai parking space data hango Aliyu tsaye jikin motanshi wanan karan ba kayan yan sanda ne ajikinshi ba, Jean da shirt yasaka, wani black jean dawata dark blue shirt dasukamai bala’in kyau suka haska shi, hannun rigan yakama murdadden muscles nashi sosai, rigan ma kaman yamai kadan sabida yanda yakama kirjinshi fum fum ya kara bayyano da cikan kirjinshi, sajenshi ya kwanta yay lub lub hakama gashin fulanin kanshi sai kyalli yake, lips dinshi yayi so sooo pink kaman ya shafa man baki pink waya nakan kunneshi yana magana, gani tayi kaman ma kayan yan sandan nan ragemai kyau sukeyi yanda jean da rigan nan suka karbeshi zaka dauka wani American celebrity ne ko wani hip hop rapper hakanan, gashi da tsayi, ko kadan bai lurada itaba jidayayi ajikinshi ana kallonshi yasa yajuyo da kanshi, da sauri tadauke kanta kaman bashi take kallo ba, dan murmushi yayi sanan yacigaba da wayan dayake harta karaso inda yake, zare wayan yayi daga kunenshi yana kallonta, dan lunshe idanu tayi sabida wani irin classic kamshi dayakeyi ahankali tabude su, murya chan kasa tace “ina yini” dan murmushi yayi jin yanda tagaidashi bai amsa ba yabude gaban motan yaciro tsuntsayenta dakuma wani paper bag da popsicles ke ciki duka yasamata a hannu, kallon paper bag din tayi ganin sunanshi yasa takalleshi ahankali tace “thank u” murmushi yamata yamaida kofan motan yarufe sanan yace “direban ki yazo?” Gyadamai kai tayi hakan yasa ya karbe cage din yace “muje nakai miki” jerawa sukayi gabaki daya duka tsawonta a shoulder shi ta tsaya, har wajen motan yakaita gaidashi Adamu yayi ya amsa sanan yabude bayan motan ya ijiye case din sanan yakalleta yanda take tsaye gefenshi yace “get in” shiga tayi ahankali tazauna sanan yamaida kofan yarufe yamata waving hannunshi, murmushi tayi itama tai waving nashi back sanan Adamu yaja motan suka wuce, komawa motanshi yayi tashiga ciki yazauna kafin yaja motan shima hankalinshi ya na bala’in kwantawa.

Gidan Baffa suka wuce, parking Adamu yayi tafito rikeda case nata na tsuntsayen dakuma jakan popsicles dinta tai side din Mom, da sallama tashiga ganin Mom azaune tana koyama Zara'u homework yasa tai wajensu tace "Mom nayi tsuntsu" wani ihu Zara'u tayi tana murna tace "Ya Khairy kibani daya" makemata kafada Khairy tayi tace "zandai aramiki amman bani baki" ihu tayi cikeda murna Khairy tai murmushi wani kalan dadi Mom taji ganinta haka dayasa tama manta ta tambayeta waya bata, cikeda farinciki tace "Ya school din?" Ahankali tace "Ipy lau Mom" Popsicles din taciro tabama Zara'u daya tace "ina Batool Zara'u" tana bacci, mikama Mom daya tayi, Mom tace "waaa rabani da kayan zakin nan naku Khairy" dariya tayi takai sauran fridge tarike daya tanasha dayan kuma na Batool tai sama Mom tabita da kallo cikeda mamaki dakuma farin ciki at the same time.

Duka ta dakama Batool dake bacci dasauri tabude ido tana turo baki ganin Khairy ne yasa tama manta dakomi ta rungume ta turata Khairy tayi tace "dalla gashi" dagudu ta karba suka shiga sha tare Batool namata hira, saida ta shanye sanan ta tashi tashiga bayi wanka tayi tafito daure da alwalan magrib salla tayi sanan itada Batool suka tafi dakin Mom.
Adakin Mom Baffa yazo yagansu dukansu sun taru suna koyama Zara'u homework, wani kalan dadi da Baffa yaji zaka dauka kyauta akamai fitowa Mom tayi tasameshi a falon sama wani kalan rungume Mom yayi ahankali yace "thank you for taking Khairy like your own wife" dan hararan Baffa tayi kafin ahankali tace "d'a nakowa ne, karka kara godemin Khairy y'ata ce, Ya Alhaji ya yarda yabika neman Auren kuwa"? Gyadamata kai yayi ahankali yace "amman da kyar, yanzu dai anyi magana nan da sati daya za'a daura auren, for now zan rike Khairy anan duk randa taji tanason zuwa gidan su she can go amman dai tana nan koya kika gani" gyadamai kai tayi tace "hakan yafi, kaga at least nan ga Batool ga Zara'u suna sata surutu, kaga takoma chan ita kadai ba kanne sai Yayyi kuma fita aiki suke abinsu" Gyadamata kai Baffa yayi cikeda gamsuwa da maganan ta yace "bari naje na kwanta nagaji" ahankali tace "mu kwana Ipy" kashema ta idanu yayi yace "ashirya min da kyau gobe ina nan" dan dariya tayi tawuce ciki batare daya tankashi ba tunda yan tsokanan nashi ne suka tashi".

Har wuraren 11 nadare takasa bacci tuni Batool tai bacci amman ita sai juye juye take tarike wayanta gam a hannunta babu abinda kemata dadi muryanshi kawai takeso taji ko zuciyanta zai mata dadi, tana haka wuraren 11:30 wayanta yahau vibrating, har wani dan gajeren ijiyan zuciya tasauke sanan tadauki wayan takai kunnenta dawata kalan murya da ita kanta batasan tanadashi ba tace "Ya Aliyu ina yini" wani dan kalan murmushi yayi da saida taji sautin murmushin tawaya dataji yasa hankalinta yawani kwanta, ahankali yace "how you?" Murya chan ciki ashagwabe tace "fine" dan shiru yayi sai chan yace "I am sorry nan kirada wuri ba, ina tareda Abba ne, most time around 11 yake barina, sorry for keeping waiting" gyadamai kai tayi ahankali tana turo baki. "Kinci abinci"? "Eh" ta amsashi kadan, "me kikaci" ahankali tace "tuwon shinkafa Mom tayi da miyan taushe" dan murmushi yayi yace "iyye kinci sosai" girgizamai kai tayi tace "oh'oh banci ba" murya chan kasa yace "why Pickle" ahankali tace "miyan was peprish, banson yaji yanasa cikina yay ciwo" cikeda kulawa yace "ohh no sorry about that mekika zo kikaci yanzu" dan murmushi tayi da saida yaji sautin murmushin tace "popsicles dina nakarasa

shanye wa” dan zaro idanu yayi yace “duka kika shanye” dasauri ta girgizakai tace “naba Batool da Zara’u, nabawa Mom itama taki karba wai batacin zaki” ahankali yace “who is Batool and Zara’u” anatse tace “yaran Mom ne, Batool ne babba shes 22, itama tana 400level a baze sai Zara’u tana primary one, sai Ammi itakuma ta haifi su Ya Zayn shine Babba, sai Ya Hafiz, sai twin Ya Hassan da Hussain” ahankali yace “Uhm Masha Allah” dan shiru yayi hakan yasa ahankali tace “kaci abinci”? Dan shiru yayi saikuma yay murmushi dan ya bala’in jin dadin tambayan yace “yes, I just had tea yanzun nan tareda Abba, dazu da yamma naci tuwo awajen Gwaggo” wani dan murmushi tayi tace “Gwaggo, u have a grandmom”? Yanda tai tambayan he could feel excitement a voice nata that just tell him batada grandma nata are late.
Ahankali yace “Gwaggo is my grandma ta haifi yara goma amman Abba kadai ya rayu, she’s Fulani daga adamawa, she’s very old though sai masifa da kaima Abba gulma….” Dan dariya kadan dayaji tayi yasa yaji wani dadi hakan yasa tacigaba, yace “she’s very old bata iya tafiya dakanta yakai 10steps haka saida wheelchair nata, but dudda haka garin kaima Abba gulma ranan taje tafadi yanzu ko 5 step bata iyayi dakanta” wanan karan dariya tayi sosai bata taba sani Aliyu ya iya nada labari hakaba. Ahankali yace “why are you laughing I am being serious Gwaggo can gossip” wani irin rushewa da dariya tayi ashagwabe tace “stoppp Ya Aliyu u are so mean” dan murmushi yayi yace “are u supporting that old woman now”? Girgizamai kai tayi tana taushe bakinta, murya chan kasa yace “do you wanna meat her some day”? Gyadamai kai tayi ahankali tace “yes” anatse yace “ok u will meet her some day, zakiga abinda nake fadi, I have sisters also but duk ba anan naija suke aure ba, so they hardly visit sai salla salla, then my little sister Meenah, she’s your age mate kinaso kiganta?” Gyadamai kai tayi tace “eh” ahankali yace “you will I promise, do u have any lectures tomorrow”? Girgizakai tayi tace “a’a gobe Mom tace zanje saloon nai kitso” dan murmushi yayi yace “ayi mai kyau, idan kin tashi da asauba after observing subhi makesure to read Qur’an and ur books afterwards okay” murya chan kasa tace “okay” agogo ya kalla ganin 1 nadare yasa yace “u need to sleep okay” gyadamai kai tayi ahankali tace “saida safe” murya chan kasa dan daso samune suyita magana yace “Allah bamu alkhairi, I love you Ummulkhair!” Dip taji ya katse wayan, wayan tabi da kallo kafin tarungume wayan kam kam ahaka bacci yay awon gaba da ita.

33

This book is 1k pay into 3107021073 aisha Muhammad first bank
Chat me up directly by clicking on this link
wa.me/+2347012181461

Yau bayan sun tashi sunyi salla tama Mama addu’a sosai hana Batool dake kokarin komawa bacci tayi taja hannunta suka shiga kitchen, lafiyayen Moi moi tayi dayaji kifi da kawai sanan tai kosai dakuma kunun gyada koda Baffa yashigo gidan yaganta a kitchen suna girki itada Batool baisan lokacin daya ciro waya yamata video batare datasani ba ya aikama Baba sanan yazauna kusada Mama a falon suna hira sanan suka fito dakomi Baffa saida yazauna yaci

kosan da kunun dudda abincin shi is ready, suna zazzaune saiga su Manaf sunzo dubata as usual once in a while zokaga dadi bajewa akayi akai lafiyayyen breakfast afalon Mom saida aka gama tass sanan sukai clearing tazo itada Batool zasuje sama suyi bacci ganin Baffa namagana dasu Ya Manaf, kiranta Baffa yayi hakan yasa tadawo, zama tayi akasa dan gyaran murya Baffa yayi yace “Khairy kafin mahaifiyanki tarasu tanata fama da Baban ki ya kara aure sabida ku amman fir yaki” yadanyi shiru sanan yace “dazata rasu agaban kowa yayyinki nan duk suna wajen ta barmini wasiyya kan na aurar da Baban ki karna barshi baida mata” dan ijiyan zuciya yasauke yace “dalilin dayasa nakira su Manaf kenan su biyo tanan kafin su tafi aiki, inaso nagaya muku nasamoma mahaifiyar ku mata” yasake shiru yana kallonsu sanan yace “bayan long bincike akanta, yar limamin masallacin Utako ne, ba yarinya bace ta taba aure da yara biyu, amman mijinta yarasu, yaran na hannun Maman mijin, tayi karatu a FCE tana koyarwa Awani primary school dashi take taimakon kanta haka, tanada natsuwa ga kirki gakuma ilimin addini, na nemama Baba aurenta inaso nan da sati daya ayi Auren hope kun yarda Ummulkhairy” Baffa yakirata ahankali, murmushi tayi ahankali tace “Allah sanya alheri” cikeda jin dadi Baffa yace “Ameen tashi to kitafi” tashi tayi tawuce shikuma Baffa yacigaba da magana dasu Manaf.

Zasu koma bacci Mom tashigo tace su shirya suje saloon, shiryawa sukayi driver ya kaisu saloon tsife kan akayi aka wanke ana gyaran kafansu, kitso akamata mai kyau shiku daya fito da fuskanta, aka mata pedicure da manicure sanan suka biya kudi suka dawo gida, ganin yanda taketa duba wayanta yasa Batool tace “wa kike jira ne awayan nan” hararanta tayi batace komiba saikuma chan tace “Besty” hararanta Batool tayi tace “wlh karya kike” hararanta itama Khairy tayi tace “serious bata dawo school ba yakamata kuma tashigo Wanan dazamu fara exam next week” “laulayin ciki hala take” dasauri Khairy takalleta tace “ciki” Gyadamata kai Batool tayi tace “haka kawata Zara tana aure yanda kikasan da cikin tai tuntube abakin kofa sai ciki” dan murmushi tayi saikuma ta kalli flat cikinta tana picturing kanta da ciki, sosai Batool kemata surutu har suka kawo gida, duba kitson da akamusu Mom tayi kitson yay kyau sosai barinma na Khairy dan tanada wani irin gashi mai bala’in kyau, ga tsayi ga ciki gakuma santsi.
*****

Yau asabar tun ranan daya siyamata tsuntsu basu kara haduwa ba sabida yanason tai karatu saidai waya da night, baicika kiranta during day time ba sabida aiki, most time text yake mata just to check up on her, ko Allah yasan tanama Aliyu wani kalan so ne dan he’s super good to her, he’s caring ya iyasa taji all damuwanta are gone, bata taba sanin she can’t put mutuwan Mama behind her ba amman Aliyu helped her to, he’s just like her strength, yau sosai take murna sabida zata ganshi, yace he’s taking her out yatura mata sunan french restaurant din dazasu hadu.

Shiryawa tayi cikin wani dogon riga, silk ne milk color yadin is so lush rigan yazauna ajikinta

dazaka dauka wata black American model ne, zama tayi tadaura wani black cotton dan kwali tai wani plain simple dauri tasaki jelan gyalen agefen shoulder nata, tadanja dan kwalin baya daya bayyana gaban kitson kanta dayay kyau, kwantaccen gashin gaban goshinta tadau karamin brush tai styling nasu da a bit gel daya bada wasu wavy corners subhanallah bakaramin kyau tayi ba, kallon fuskanta tayi a madubi ganin wuyanta empty yasa tadauki wani simple two step necklace dinta dakeda pendant na diamond tasaka awuyanta wuyanta yafara wani kyalli, sanan tadauki kananun dan kunnensu tasaka, mikewa tsaye tayi tanabin kanta da kallo ganin yanda kayan yabi jikinta yanda boobs dinta suka wanisa gaban rigan yay kyau yasa taji wani kalan kunya, wardrobe dinta tayi tadauko wani simple dark army green a bit transparent veil normally dark green goes with milk a whole lot yafashi tayi tagaban hakan yarufe kirjinta but still kana hango kyallin diamond necklace dinta ta gyalen, komawa tayi tazauna kan kujera sanan tadauki brush ta taje full black giranta sanan tadau man baki dake shining ta shafa kan lips dinta dayawani haskaka pink lips din, ganin idanunta sunyi bala'in haske dayawa yasa yadauki kwallin Batool ta zizara Omg, dan murmushi tayi dan ita kanta tama kanta kyau kaman taje studio tai hoto, tashi tayi ahankali yau batajin saka hill hakan yasa tasaka slippers na Hermes shima dark army green daya hadu yau complementing dressing nata gabaki daya, she look very simple but yet super super elegant, wani cute little handbag tadauka na Charles and Keith beige color dayasa tai kaman zata gasan kyau sanan tadauki turarukanta tafesa tanadan tunani mezata gayama Mom tabude kofa tafito, afalo tasami Mom zaune Batool batanan taje gidan kawarta amso note sabida fitanta da Aliyu yasa bata rakataba, ganinta yasa Mom tace "wanan gayu haka sai ina Khairiry"? Dan murmushi tayi ahankali tace "Mom zani wajen Besty dubata batada lpy" ahankali Mom tace "ayyah, laulayi Batool tagayamin dama, ki gaidamin da ita Allah sarki yarinya, haka tadinga sintirin zuwa dubaki, ki gaishemin da ita please" gyadama Mom kai tayi tawuce tafita Adamu na ganinta yatada mota shiga bayi tayi tazauna tagayamai inda zasu suka wuce.

Wani hadadden eatry sukaje, saida Adamu yay parking sanan taciro wayanta daga jaka kafin tai dialing number shi taga kiranshi ya shigo hakan yasa tadauka takai kunenta, murya chan kasa taji yace "come out of the car" sanan ya katse wayan, ahankali tafito daga motan tama Adamu bye yatada motan yawuce sanan tajuyo tana waige waige dan bata ganshi ba. "You look breathtakingly beautiful Miss" taji muryanshi ta gefenta, dawani irin sauri tajuyo da kanta ta kalleshi yana sanye dawani yadi mai laushi fari tass, yana wani irin kamshi mai dadi yasanya black glasses a idanunshi yana kallonta hannunshi rikeda flowers masu kyau combination na white and red yamika mata ahankali yace "flowers for Miss Khairy" fuskanshi takara kallo wani irin murmushi tasaki daya bayyana white teeth nata tasa hannu takarbi flowers din sanan ahankali takaisu saitin hancinta tai breathing in wani irin kamshi taji sunayi mai sanyaya rai kafin ta fuzar tasake dago kanta takalleshi cikin wani classic voice tace "I love flowers thank you Ya Aliyu, they're beautiful" glasses na idanunshi yacire murmushi yamata yace "shall we" gyadamai kai tayi sanan suka wuce ciki tana rikeda flowers dinta kaman wasu english couples, akwai mutane amman badayawa ba table din daya musu reserving yakaita wajen sanan yajamata kujera zama tayi ahankali tace "thank you" sanan ta ijiye flowers nata agabanta tana

kallonsu tana shafasu da hannunta, zama yayi kujeran dake facing nata yana kallonta baisan maisa ba but yau kyan datamai daban ne kodan yakwana biyu bai ganta ba, abincin daya musu placing order aka shiga kawomusu abinma mamaki yabata dan abincin sunyi yawa, this is a brunch date wow! Murya chan kasa yace “do you like it” gyadamai kai tayi ahankali tace “thank u” murmushi yasakeyi yace “zakici kosaina baki abaki” makemai kafada tayi akunyace sanan tadauki cutlery tashiga cin lasgana dashi yafi shiga idanunta tsayawa yayi yana kallonta Khairy nada wani irin natsuwa da inba kana tareda ita ba bazaka taba cewa tanadashi ba, she does everything a natse calmly batada rawan jikin nan, kaman taji ajikinta ana kallonta hakan yasa tadago kanta hada idanu sukai dashi akunyace ta sauke kanta tanajan gyalenta zata rufe fuskanta dasauri yace “nooo Pickle sorry bazan kara kallonki ba look nazama makaho” kallonshi tadanyi ganin yanda yay da idanu abin yabata dariya dan dariya tayi shima yayi sanan yafara ciCn nashi .

34

Saida sukaci suka koshi sanan suka ture ga uban abinshi sun rage akwai wayanda bama sutaba ba ahankali yace “shall we?” Gyadamai kai tayi yatashi hakan yasa itama ta tashi suka fito maiikatan eatry namai godiya suka wuce motanshi yabude mata shiga tayi sanan yamaida kofan yarufe yadawo yazauna yatada motan suka bar wajen bini bini yake satan kallonshi ganin sunzo wonderland yasa tawani ware idanunta aljihun motanshi yasa hannu yaciro mata 2 ticket dinsu yamika mata Wanan Karan takasa boye excitement dinta tace “wowwwwww Ya Aliyu I am so sosoooooo happy thank uuu” u welcome baby yay maganan yana shiga ciki parking yayi a inda ake parking sanan yafito itama fitowa tayi she’s so happy datama kasa boyewa zagayowa yayi ta inda take yace “are u happy” gyadamai kai tayi tana dan tsalle tace “yes thank uuu” murmushi yamata yace “let’s go” ciki sukayi yariga yay recharging card nasu yace “me and u competition yau zamuyi kin yarda”? Gyadamai kai tayi tace “and I will win cus I am a born winner” murmushi yayi yace “let’s see then” da bumper cars suka fara suka shiga, both of them were literally screaming suna bubbuge juna da motan shi kanshi Aliyu baitaba sanin he could do this childish play ba sai yau, bugeshi tayi motanshi yakoma baya tahau ihu ta waigo tanamai gwalo kwafa yayi sanan yatashi yafita itama fitowa tayi tana tsalle sosai kaman Yar yarinya tace “I won yayy” hararanta yayi yay gaba dasauri tabishi sukaje next game dayakeso suyi shooting target, indai target ne babu wanda yakaishi but da gangan yabarta shima taci wayyo Ummulkhairy kaman zata zuba ruwa akasa tasha dan dadi, ice cream yasaya mata takarba tanasha saida yajiraa ta shanye sanan suka shiga wajen 3D zasu buga car race, nan ma ita taci, yanda takemai dariya ko shi kanshi baisan ta iya dariya hakaba she was really feeling herself, ta iya game sosai sabida su Maheer dan sunayi a gida, all games na wajen nan saida tayi har teddy bear saida taci katuwa tadauki abinta tana dariya, hararanta yayi yay gaba dasauri tabishi tace “Ya Aliyu wait, fushi kake sorry but I told you I am a winner” juyowa yayi yace “nine looser ko” hannu tadaura akan bakinta tana hadiye dariyan dake zuwa mata tace “uhm’uhm” hararanta yayi yace “let’s go waje kiga wanda zamuyi I promise u will be the one to

loose” dasauri with confidence tace “eh muje” tabishi dasauri gaban rollercosta taga sunje koda tana yarinya bata yarda tai abin nan ba sabida tsoro hakan yasa ta ware idanu, magana taga Aliyu yayi da mutanen sanan yazo inda take tsaye yace “harkin fara tsoro ne” turamai baki tayi tace “never” dan bakinta data turamai yakalla saikuma ahankali yace “mutafi to aga who will lost, and yarinya kikamin kuka ko” dasauri tace “ni Bana kuka saikace wata baby” dariyanshi yahadiye dan he already saw d fears a eyes nata, yace “let’s go” tana bite dashi suka shiga wajen, ganin tsoro a fuskanta yasa bai bari ta shiga wajen one person ba, two sitter slot suka shiga na mutane biyu, zama yayi sanan itama tashigo tazauna kusadashi ahankali sakamusu abinda zai rike mutum yahanasu faduwa yayi sukadai akan makeken roller coaster dinan sanan Aliyu yakalleta yace “kin shirya” gyadamai kai tayi gabanta na faduwa tim tim, juyowa Aliyu yayi yakallesu yace “we ready” ajiyan zuciya tasauke hakan yasa yay dan dariya yaciro wayanshi yana bude camera yace “I need evidence” turo baki tayi tana hararanshi sanan aka kunna abun, rawa hannunta yafara tun kafin su fara moving, kawai jitayi sunyi sararin samaniyan Allah wani kalan ihuuu tayi. “Wayyoooo Ya Aliyu banyi banyi nafasa, huuuuu wlh nafasa kayakuri” tai maganan tana kankame idanunta jin kaman hanjin cikinta zai fito shiko dariya kaman zai mutu yana musu video, jin suncigaba da sama abin nawani chillarasu kaman zai kaisu lahira yasa kawai tawani kankameshi tana boye fuskanta akan kirjinshi. “Innalillahi, Ya Aliyu zanyi fitsari, wlh u won, Dan Allah kayakuri kace subari wayyooo Allah na na shiga uku, Ya Aliyu zan mutuuuu” alamu yamusu da hannu dasu kashe jin yanda heart nata ke beating, amman har suka dawo kasa bata saniba ta kankameshi gam gam tana cewa zatai fitasari, yadade yana zaune ahaka feeling her ajikinshi kafin ahankali yace “sokike kimin fitsarin ajiki cus we are down already” dago kanta tayi daga jikinshi ahankali kaman matsoraciya kallon idanunshi take dake cikeda dariya sanan takalli ko’ina ganin suna kasa, dan hararanta yayi yace “matsoraciya kawai harda kuka” dan turo baki tayi sanan akunyace tasake takoma gefenta, ciremusu abin rike mutum din yayi sanan yabude sit din yafita dagangan yashiga duba jikinshi yace “hope bakimin fitsarin ajikina ba” rufe fuskanta tayi da hannu tace “ni banyi ba” sanan ta sauko tagefenshi tabi da gudu tai restroom dan tagani wajen dasuke zuwa, shikuma yawuce dan sayomusu snacks yana kallon video daya musu awayanshi.

Popcorn yasai musu, unsweetened yasaima kanshi dan baicin sugar shi ko kadan itakuma yasaimata mai milk sanan yazauna yana jiranta.

Fitsari tayi sanan tafito tanadan murmushi ita kunya ma takeji, tana cikin tafiya taji an kwalamata kira Ummulkhairy dasauri tajuyo, ganin class governor dinsu yasa tadan tsaya tana murmushi shima yakaraso wajenta da sauri yana rikeda cotton candy guda biyu a hannunshi da alama bashi kadai bane, ganinta yasa yace “wow kema kinzo shakatawa” murmushi tayi tace “eh Governor ya aiki ya shirin exam” ahankali yace “Alhamdulilah” yana kallonta ganin yanda tai kyau yadade yanason Khairy amman yakasa gayamata dan yake yayi yace “u look good Khairy” murmushi tayi tace “thank you bari naje” tajuya zata wuce dasauri yabiyota gabanta yasha sanan yamika mata one cotton candy dake hannunshi yace “atleast take this” girgizamai kai tayi tace “no thank you Governor” dasauri yace “I insist Allah saikin amsa, nawane dana little sister na dama, nakoma nakara sayowa, idan baki amsa ba zanta binki ne wlh” badan taso ba

bataso taga kaman wulakanci tamai wanan ma daya rantse saita amsa yasa gently tamika hannu takarbi wanda yake bata sanan tace “thank u” tawuce da sauri binta dawani irin mayen kallo yayi sanan yace “see you on Monday Khairy” ko tankashi batayiba dasauri take tafiya kanta akasa dan tabata lokaci tabar Ya Aliyu chan, jitayi ajikinta ana kallonta, ahankali tadaga kanta, Aliyu tagani tsaye rikeda pop corn guda biyu a hannu, fuskanshi kadai tagani ya tabbatar mata da yaganta tareda class governor dinsu, jitayi kawai jikinta yahau rawa sakin cotton candy don tayi akasa sanan ta taho da sauri kafin takaraso gabanshi gani tayi cikeda bacinrai yawani irin jefar da pop corns din akasa yajuya fuuu kaman zaki yawuce dasauri tabishi tana kiranshi. “Ya Aliyu Ya Aliyu” amman ko waigowa baiyiba har wajen dayay parking mota kafin ta isa wajen dan one step dinshi shine like 3 or 4 step nata harya shiga mota wani irin jan motanshi yayi Saura kiris yabuge wasu yarama ita kanta saida tai ihu Allah yakiyaye bai bugesu ba yafita daga wajen da balCa’in gudu.

35

Jiyayi kafafunta sun mata sanyi wani dan dakali tasamu tazauna bata taba sanin cewa Aliyu nada fushi dakuma zuciya hakaba sai yau, sabida yaganta dawani saiya tafi yabarta anan, jiyayi duk wani iri zuciyanta badadi kaman ba ita bane tagama dariya yanzun nan ba, ahankali tabude jakanta taciro wayanta kiranshi tayi amman har kiran ya katse bai daukaba, hakan yasa takira Adamu tafadamai inda take, baa dauki cikakken 20min ba saiga Adamu yazo mota tashiga suka wuce gida.

Amota ma sake trying nashi tayi amman bai dauka ba, kaiwa gida sukayi hakan yasa tamaida wayan jaka ta fito tashiga ciki, Mom tagani afalo tareda Batool Mom tace “yamai jikin” murmushi tayi tace “yaji sauki Mom tace na gaidaku” “muna amsawa, jeki chanza kaya kiyi wanka ana ma kiran salla saiki salla ki sauko kici abinci” gyadama Mom kai tayi tawuce, daki tashiga wanka tayo tafito salla tayi sanan tazauna shiru jin Mom nakiranta yasa tafice taje abinci taci tadawo daki wasa wasa har 12 bai kirata ba kasa hakura tayi she called him twice bai dagaba kuma bai kirata ba da kyar bacci ya kwasheta ranan hakan yasa washe gari duktai wani kala data tashi takasa tabuka komi koyasan da hakan ne message dinshi taga ya shigo wayanta. “Go and study for exam naki u have paper tommorow”
Dudda message din baiyi acknowledge na calls nata but tadanji nauyi yasauka daga mind dinta, kasa hakura tayi tamai reply.
“Ya Aliyu I am sorry, please kayakuri” jin shiru baimata reply ba yasa tasake turamai wani sakon.
“I know him, class governor namu ne saisa nama amsa maganan shi, but I will not do it again I promise”

Almost 5min but bataga reply ba, sosai taji ta bala’in damu sake turamai wani sakon tayi.

“Ya Aliyu I am sorry”
 Tana turawa yamata reply.
“I said kije kiyi karatu” gyadamai kai tayi kawai ta ijiye wayan book dinta tadauka ta tashi taje tazauna kan dadduma dudda karatun rabi tunanin shine but hakanan ta tursasa kanta tayi.

Yau rabonta dajin muryan Aliyu sati daya chur kenan dan gashi nan wata asabar din ta zagayo, exam ma adaddafe take tabashi hakuri harta gaji yaki hakura dudda kullum saiya mata text yasata tayi karatu but other than that shiru kakeji, har dan ramewa tayi dayake ansan exam take babu wanda yabama abin attention, yau tunda gari yawaye Mom tasata ta shirya taje tagaida matan Baba da tuni akai biki harta tare, bataso taje amman bazata iya cewa no ba hakan yasa ta shirya dan yau at the same time zaa raba gadon Mama abinda yasama bataso taje kenan.

Parking direba yayi acikin gidansu gani tayi gidansu ya chanza an sake penti, Baba tagani akujera a tsakar gidan da alamu shan iska yake yasa farin jallabiya ga flask don shayi agabanshi dawasu papers yarame sosai ganinta yawani fadada murmushin fuskanta yabude mata hannu dawani irin gudu tazo batai wata wata ba tawani rungume shi she miss baba so much, sun dade ahaka sanan tasakeshi yazauna kan kujeran dake kusada shi tace “Baba ina yini” murmushi yamata yana tana kumatunta yace “Khairy na ya jarabawa next week zaki gama ko” gyadamai kai tayi yace “yaushe zaki dawo gida” gidan tabi da kallo sanan ahankali tace “bayan jarabawa Baba” Gyadamata kai yayi sanan yadauki papers dake gabanshi yabata yace “ga gadon Maman ki nan dakika samu na filaye biyu dakuma gidan kifinta guda daya, sai kayayyakin ta, duk wani abu na Maman ki daidai da cokali an raba, duk suna store, su Manaf duk sunkai nasu gidan marayu sunyi sadaka dasu naki kome kikace ayi dasu haka zaayi” ahankali tace “Baba akai gidan marayu, kayanta na sawa zan cire wanda nakeso sauran sai akai” Gyadamata mata kai yayi sanan ahankali yakama hannunta yace “I am here for you Khairy okay, hope bakida any damuwa” dan murmushi tayi tace “Baba I am fine Allah kuwan, ina su Ya Manaf” “sun tafi office” gyadamai kai tayi ahankali tace “ina new Mom”? Yadade yana kallonta sabida yanda tafadi sunan kafin ahankali yace “tana ciki” tashi tayi tace “bari naje nagaidata” tawuce ciki Baba yabita da kallo, ahankali tabude kofar falonsu wani sanyi yamata sallama tadade tsaye kafin ta shiga cikin falon daidai da foot mat nabakin kofa an chanza har tv bango an chanza komi tatas kaman ba gidansu ba kaman ba falon Mama ba, abin was so strange, mutuwa mutuwa wlh karshe ne! yanzu shikenan this falo is not for Mama again na wata ne, Anya zata iya cigaba da zama agidan nan kuwa Anya bazata koma da zama gidan Baffa gabaki dayaba Dan what she is feeling right now jitayi kaman ta kurma ihu hatta labule duka bana Mama bane jin kuka yazo mata sosai dawani irin sauri tajuya zata fita taji ankirata. “Ummulkhairy” chak ta tsaya, sanan takai hannuwanta ta goge hawayen dasuka zubomata daga idanunta tass kafin ahankali tajuyo, sabuwar matan Baba tagani batada wani makusa Babba ce itama amman daga gani Mama ta girmeta sosai, doguwa da ita kana ganinta kaga natsassiyar mace, murmushin dole Khairy ta kakalo ahankali tace “ina yini uhnnn” tama rasa sunan dazata kirata dashi murmushi matan tayi daidai takaraso gabanta hannunta tasa ahankali takama hannun Khairy tace “sunana Mariya, maisa kika tsaya anan bakin kofa keda falonku shigo mu gaisa” taja Khairy cikin falon danne kukanta Khairy tayi sosai sanan ta zauna akan

kujeran da Mariya ta zaunar da ita sanan tace “ina zuwa” dasaurinta ta wuce kitchen tafito da drinks a tray takawoma Khairy ta ijiye sanan tasake zama kusada Khairy data kasa kallonta dan wani iri takeji, ahankali takai hannunta tadaura kan cinyan Khairy cikeda tausayawa tace “ina tunamiki da mahaifiyanki ko” dauke kai Khairy tayi da sauri tana kokarin danne hawayen dake gab da zubowa tace “uhn uhn” ahankali Mariya tace “Khairy I am so sorry about your mother’s death, Allah ubangiji ya haskaka makwancinta, Allah yasaka mata da gidan aljanna” ahankali Khairy tace “Ameen” murya chan kasa tace “Khairy mijina na farko nima yarasu so I understand pains dinki sabida yarana suma sunma mahaifinsu kuka, at first da akazo nemama babanki aurena nariga nai alkawari bazan kara aure ba but danaji matarshi tarasu tabar yara abinda yasa na aure mahaifinki kenan sabida inaso nazama uwa ga yaranshi dan ni bansami chance dinan nama yarana hakaba” dasauri Khairy takalleta tana share hawayen daya zubomata, Gyadamata kai tayi tace “bayan rasuwanshi iyayenshi suka karbe yaran, kafin naga yarana yanzu sai Hutu Hutu akawosu sumin kwana biyu, tuntuni naso nazo dakaina ma har gidan Baffan naku ko Baban ki ko yayyinki sukawoni nadawo dake gidan mahaifinki, Khairy just know this, nasan ba lallai ki daukeni ko ki kalleni a matsayin mahaifiyanki yanzu ba saidai a matsayin kishiyaneuwa, I want to assure u ke y’ata ce Khairy, u can come to me for everything and anything, zan rikeki da yayyinki amana kaman yaran da na haifa, bazan taba cutar daku ba kinji” Gyadamata kai Khairy tayi sanan ahankali tace “thank u” hannu Mariya tasa tashare mata hawayen sanan tace tashi muje sama binta Khairy yayi Baba dake kofa yaji komi baitaba jin sonta aranshiba sai yau, tunda akai auren basuma taba kwana daki daya ba dan gani yake kaman yacuci Mama amman yau yakudiri aniya komi zai chanza zai saki ranshi da ita.

Khairy bata bar gidan ba sai bayan sallan magrib shima saida matan Baba tasa tamata alkawari dazaran tagama jarabawa zata daCwo gida.

36

Yauma hartai bacci Aliyu bai kirata ba ita at this junction tama fara tsoro haka Aliyu keda fushi, abinma haduwa yayi yataru yamata yawa hakan yasa ta tashi da zazzabi jikinta zafi gashi hancinta yatoshe mura, wuraren 7:30 tafito kasa, ganinta wani iri yasa Mom tace “meke damunki idanunki sundan kumbura da hancinki” ahankali tace “mura ne” jin yanda take magana da hanci yasa Mom tace “Ayyah sannu zoki breakfast bari nakowa miki maganin mura” kunu tadeba tafara sha bata wani dade ba Mom tasauko rikeda maganin mura karba tayi tasha sanan takarasa shanye kunun ta tashi tama Mom sallama ta tafi.

Tun kafin sukarasa wajen parking space din ta hango Aliyu tsaye yay wani irin bala’in kyau yakara haske kaman wani balarabe, yana sanye da uniform din yan sanda jingine da motanshi yay folding hannunshi a kirji yana kallon motansu tunda ta doso, idanunshi sun fada ciki kadan

kana ganinshi kasan shima yawahala yan kwanakin nan kaman yanda itama ta wahala.

Jitayi wani abu yazomata wuya amman ta danne, parking Adamu yayi hakan yasa tafito daga motan ahankali kallonshi tayi kaman yanda yake kallonta, hawayen dataji yazo mata yasa takauda kanta gefe dasauri taredakai bayan hannunta tashare sanan ahankali tadaga kafanta tafara tafiya wuceshi tayi ahankali kaman bata ganshi ba dawani irin sauri yasha gabanta hakan yasa chak ta tsaya batare data dagokai ta kalleshi ba dan dazaran ta kalleshi zata iya kuka kuma bataso tayi, ahankali tace “excuse me please I have exam by 9” dan ijiyan zuciya yasauke tareda lumshe idanunshi jin muryanta sanan ahankali yabude su yadaura akanta, murya chan kasa yace “Ummulkhair!” Wani abune yataso mata tundaga cikinta harzuwa wuyanta dataji inbata amayar dashiba zata iya mutuwa dago idanunta dasukai jaa tayi sun cikada kwala tace “don’t call my name again Ya Aliyu, nadauka ai kadena daukan wayana, kadaina kirana, kadaina texting dina? Why are you here then? Mekazo nema wajena”? Kallonta yake idanunshi sundanyi ja, jiyayi zuciyanshi na tafarfasa, ko kadan baiso yanunama Khairy fushin shi that’s the reason why he avoided her yamaki wayada ita, wani irin zuciya yakawomai wuya ciki wani irin harsh tone that’s not loud yace “kinmin laifi and kina fushi dani? Why would you talk to anyman har kina karban abinshi why?!” Yamata wani kalan ihu da saida tadan firgita tadan koma baya tana kalle kalle tagodema Allah dababu kowa awajen, zuciyanshi yanuna mata yace “kinsan what you did to me? To my heart haaa? Why will you talk to anyman why?? Akanme zaki tsaya kinama wani namiji magana bayan kinsan I love you! My heart beats for you! You are my life! U are my happiness! You are my everything Khairy haaa” yanda idanunshi taga sunyi jajir saida abin yabata tsoro kaman zai daketa, jijiyoyin kanshi sun fito, bayan hannunta tasa tagoge hawayen daya zubomata kafin ahankali tace “Ya Hydar akanme zakai tunanin wani abu bayan nacemaka class governor dinmu ne, is it my fault we bumped into each other that day? Ya Aliyu akanme zakai tunanin wani nakeso bayan nariga nama zuciyata alkawari cewa ita taka ce, zuciyata, gangan jikina, ruhina duka nakane Ya Aliyu Wanan shine ALKAWARIN ZUCIYA na, akan me zakai tunanin bana sonka uhmm”? Hawayen daya zubomata ta share, kawai tawuce fuuuu hannu yamika zai kirata amman yakasa cikin wani irin fushi yadaki motanshi da kafa shikanshi baisan mesa yake da mugun kishi nan ba.

Adaddafe tai exam din ranan, inda ace batai karatu ba dababu abinda zata iya rubutawa sabida yanda babu abinda kemata dadin nan, bata taba sanin haka akeji idan akai fada da masoyi ba sai yau, she miss Aliyu badly, she just miss him.
Tana gama paper tafito bata tsaya jiran su Besty da Amal ba sabida yanda batajin dadin komi ga jikinta yakara zafi, fitowa tayi yanda takeji batajin zama ta iya jiran Adamu yazo daukanta ba hakan yasa tafara tafiya tai hanyar gate, wani irin shan gabanta da mota Aliyu yayi tana ganin motan tajuya zata chanza hanya da sauri yafito baima tsaya mata magana ba hannunta yaja ganin mutane yasa tabishi dan ayanda yake zai iya cewa daukanta zaiyi gaban mutane idan bata bishi ba, bude mata yayi tashiga batare data kalleshi ba sanan yamaida kofan yarufe yazagaya yashiga mazaunin direba yaja motan, batare data kalleshi ba tace “kana fita daga gate kasauke ni natare cab natafi gida” kallonta yayi da jajayen idanunshi cikin husky voice

dinshi yace “idan naki fa” hannunta tadaura akan fuska tafashe da kuka sosai cikin kuka tace “I said I am sorry, I don’t have anything to do with class governor munhadu ne by accident, he said yazo wajen da sister shine, and he insisted saina karbi candy hannunshi, I don’t wanna be rude koyaga namai wulakanci saisa na amsa, nabaka hakuri kaki hakura what do you want from me, what do you want from me?” Wani irin fizgota taji anyi da bala’in karfi, dawani irin sauri tabude idanunta jikinta na rawa, tuki Aliyu yake da hannu daya akan titi amman ya fizgota da karfi tana jikin kafadanshi yakai hannunshi ta waist nata yariketa gam ajikinshi takasa kwace kanta yana kallon hanya, dasauri takalli hanyan jikinta narawa tace “Ya Aliyu dan Allah zamuyi accident kayi parking” gangarawa gefen hanya yayi yawani kalan taka burki kaman motan zai kife kankameshi tayi tareda runtse ido gam gam jikinta narawa still, habanta dataji ankama yasa tabude idanunta ahankali, hada idanu sukai da Aliyu da idanunshi sukai ja faduwa taji gabanta nayi, cikin wani irin murya yace “you ask wat do I want from you” gyadamai kai tayi tana wani irin shakkan shi, wani kallon fuskanta yake ahankali yace “I want you Ummulkhair! I want you so bad saisa my heart can not stand yaga kinama any namiji magana, zuciyana yakusan bugawa ranan I had an accident” dan zaro idanu tayi cikeda mamaki, lumshe idanu yayi sanan ahankali yakai fuskanshi dab da nata yana kallonta dawani irin sauri ta lumshe idanunta gabanta nafaduwa dasauri dasauri yadade yana kallon fuskanta ahaka kafin ahankali yadaura goshinshi kan nata yanajin saukan numfashinta akan fuskanshi, cikin wani whispering voice dake nuna so yace “I am sorry for hurting you, I couldn’t help it, Ummulkhair ina sonki da yawa and Aliyu is a very very jealous man bayin kaina bane, can you put up with me? I can’t help it bazan iya magance kishina akanki ba, zaki iya rayuwa dani eh Ummulkhair?” Jitayi zuciyan ta gabaki daya yasaki gyadamai kai tayi ahankali tace “but don’t ever hurt me the way you did by not answering and responding to my calls, Ya Aliyu I….Love yhuu” this is the first time tafadimai kalman daya dade yakeso yaji daga bakinta, ahankali yace “you are the PROMISE OF MY HEART Khairy” ahankali tace “Ya Aliyu nima kaine ALKAWARIN ZUCIYA ta” ahankali yamata peck a forehead sanan yakai hannunshi yashare mata fuska tass sanan gently yasake ta yamaidata kujeran datake kafin ahankali yatada motan zuwa pharmacy, magunguna yasayo mata da ruwa da kanshi yabata sai kallonta yake sanan yadawo motan yatada har anguwan su Baffa yakawota nesa da gida yay parking sanan yakalleta, kallonshi tayi sanan ahankali tabude motan tasauka tawuce saida yaga shi ganta gida sanan yatada motan yabar anguwCan.



Wanan Littafin na kudi ne karki karanta batare dakin biyaba kika karanta min littafi ban yafeba.

wa.me/+2347012181461
To chat me up on watsapp

This novel is 1k
Pay 1k into 3107021073 aisha Muhammad saiki turomin evidence of payment ta watsapp

number na 07012181461
Thank u❤️

Wuraren 10 yau taga kiranshi wayan na gabda katsewa tadauka ahankali tace “Ya Aliyu” ahankali shima yace “Ya muran? Jikinki yadena zafi” gyadamai kai tayi tace “eh yadena naji sauki” dan ijiyan zuciya yasauke kafin ahankali yace “I am sorry for hurting you Pickle, will you forgive me” gyadamai kai tayi tace “bakomi yawuce” dan ijiyan zuciya yakara saukewa ahankali yace “kinada paper ranan Monday” gyadamai kai tayi tace “yes but in the morning” ahankali yace “good, I want to invite you to my promotion stuff zakizo” wani irin murmushi tayi tace “za’ayi promoting naka awajen aiki”? Dan yatsine fuska yayi yace “kind of and I want you to be there for me, ina stage ina ganinki ina murmushi” dan murmushi tayi sosai tace “to baranzo ba” Dasauri kaman dan yaro yace “pleaseeee Khairirin Baba” dan dariya tayi ganin yanda yake tsokanta ahankali tace “okay shikenan zanzo but kaizaka daukamin jakana” dasauri yace “zanma goyaki like my baby idan kinas…….” katse wayan yayi dasauri jin alamun mutum tsaye adakinshi, dago kanshi yayi ganin Abba tsaye yana sanye da jallabiya ya rungume hannunshi yana murmushi yasa yaji wani kalan kunya, daman abinda yasa baije wajen Abba ba sabida yay wasu manyan baki ne, patient dinshi saisa baije ba.

Ahankali Aliyu yatashi zaune daga gadon kasa kallon Abba yayi dan murmushin da Abba keyi kadai ya tabbatarmai da yaji all maganan dayake da Ummulkhair, akunyace yace “Abba bakin sun tafi” dan murmushi Abba yayi yamaida kofan yarufe sanan yashigo dakin har zuwa inda Aliyu yake zaunen sanan yazauna agefenshi, ahankali yace “Aliyu so kanada yarinyar dakakeso haka baka sanar dani ba” kunya yasakeji ganin yakasa magana yasa cikeda kulawa Abba yace “what’s her name”? Ahankali murya chan kasa Aliyu yace “Ummulkhair” dan murmushi Abba yayi yadade yanaso yaga Aliyu yayi aure amman ko budurwa Aliyu baidashi, daurewa yayi yay hiding farin cikin shi karya nunamai yace “yaushe zamuje mu nemamaka aurenta”? Dan murmushi yayi dashi kanshi Abba saida yaga murmushi hakan yakara tabbatarmai da yanda Aliyu ke sonta sanan yace “inaso dama takarasa gama school ne Abba” ahankali Abba yace “nan da kaman yaushe kenan” ”sauran mata just one semester, Accounting takeyi” gyadamai kai Abba yayi saikuma yatashi tsaye yana kallonshi ganin yanda har yanzu yakasa hada idanu dashi, cikeda tsokana yace “bari natafi nabarku kucigaba da soyayyan ku, anyway greet my daughter in law for me” dan dariya yayi Abba yawuce yafita ranshi fess. Kiran Khairy yakarayi sai after 1 sanan sukai sallama.

Yau Monday wuraren 12 tadawo gida dan 11 tagama paper ta na yau, tanacin abinci tai bacci dan 4 zata wajen ceremony na karin girman Aliyu.

Washegari jummaa yaune kamu, gabaki daya tadawo wata kalan tausayi babu wani abu na duniya dake mata dadi she just wish akwai wani abu dazata iyayi ace all this things mafarki ne, Mama bata mutu ba ta barinmata wani littafi ba or anything of such, takasa daina tunanin Aliyu, duk idan tai tunani yanachan baida lpy suffering saitaji zuciyanta na shattering, saiyau yanzu ta yarda soyayya yafi komi dadi sanan yafi komi daci, condition da situation kesa kadandana kowani part, inda tasan cewa ahaka soyayyanta da Aliyu zai karake da batama hadu dashi arayuwanta ba dayafi mata alkhairi, tanaji tana gani wuraren 4 aka shiga shiryata ana mata makeup za'ayi kamu mai makeup dake mata tayi ta tsaya kusan sau hudu sabida sai anacikin yi kawai tashiga kuka, saida Anty Mariya tazo sanan ta lallasheta tai shiru aka gama mata aka shiryata cikin wata atampa na kampala pink sabida is her colour kuma anaso ayi kamun da abinda takeso aka fita da ita tsakar gida mata na gudu kawayebta sun cika gidan dan Batool da Besty duk sun gayyace su wani irin kuka na zuci kawai take, ana haka akai announcing zuwan ango da abokanenshi saiga Zayn dayaci wani irin gayu Subhanallahi kaman balarabe yayi kyau da Mamu da Faisal zaka dauka turawa ne nan kawayen Khairy aka shiga rawan jiki, da dollars yabiya kudin siyan fuskanta sanan aka budemai fuskanta tsugunnawa yayi agabanta yana kallonta tamai kyau iya kyau kasa dagakai tayi ta kalleshi kanta nakasa, hawaye taji sun zubomata sharrrr ahankali yakai hannunshi kan fuskanta murya chan kasa yace "don't cry Mrs Zayn" wani kalan guda aka dauka awajen ana shewa jin sunan daya kirata dashi, dan murmushi Zayn din yayi dan baisan anjishiba sanan yajuya suka fice daga gidan yana murmushi Mamu yace "wowww Zayn kagama iskancin ka ka auro natsassiyar kamilan yarinya haka" murmushi yadanyi yace "itace first ever girl dana taba so dakaina" ahankali Mamu yakama kafadanshi zaiyi magana Zayn yace "please don't ruin my mood da maganan that Ayshu I was never and will never be interested in that girl, is not like am a bad person banma taba bata fuskan tasoni

ba" ahankali Mamu yace "but you f*cked her" yatsine fuska yayi yace "I never wanted to, dudda haka i paid her ai ko so bata bina any bashi nima haka let her go her way I go my way" shiru Mamu yayi dan yana bala'in tausayin Ayshu dake neman kashe kanta kanshi, ahankali Mamu yace "kaini gidanku to naje na dauko suitcase dina tunda kace kai anan kake" yatsine fuska Faisal yayi yace "nidai bai hotel i need sleep" baima jirasu ba yawuce yashiga dayar motarsu yawuce abinshi, yatsine fuska  Zayn yayi yace "kasan dai I've been running away from that old woman ko, sokake taganni ta tasani gaba da bala'in masifan ta" dasauri Mamu yace "wlh bazama tasan kazo ba gidanku cikeda jama'a, let's go please wajenka nazo agarin nan babu abinda zaisa naita bin direba yana kaini ko'ina zani" hararanshi Zayn yayi yace "kana dan Abuja amman tsabagen rayuwa outside babu inda kasani agarin ku" shiga motan sukayi yaja motan har zuwa gidansu parking sukayi Zayn na mota bai saukoba dan baimaso aganshi Mamu ne kadai yasauko yawuce side dinsu shikuma yajingina kanshi jikin kujeran motan yana tunanin fuskan Khairy murya chan kasa idanunshi a lumshe yace I love her, knocking glass din motan da akayi yasa yabude idanunshi ahankali ganin Yar aikin Ammi yasa gabanshi yafadi, ahankali tace "Ammi tace kazo tana falon ta" Gyadamata kai yayi tawuce tafice, dan gajeren tsaki yaja sanan ahankali yatashi bude kofan yayi yafice daga motan zuwa flat din Ammi.
******

Yau tunda gari yawaye kuka Ummulkhairy keyi sabida tasan dagayau shikenan itada Aliyu, har kasan ranta jitake inama ace Mama batabar wanan wasiyyan Auren Zayn din nan ba, da kyar su Batool da kawayenta suka shiryata sukasa tai shiru aka mata kwalliya babu wanda zai kalli Khairy dabazai kara kallo ba sabida yanda tai kyau fatarta taji gyara kaman me, ta tsumu iya tsumuwa shi kanshi Baba daya ganta rungumeta kawai yayi sabida all the thing was so damn emotional he can't believe his little Ummulkhairy is going to gidan mijinta yau.
Karfe 2 daidai na rana za'a daurama both Manaf da Mu'az aure awani Babban masallaci dakenan cikin gari, tunkafin 2 tayi mutane suka cika makil ana jiran 2 yayi adaura Auren dan daga Baba har Baffa sunada mutane gakuma tawagan yaransu, daga Baba har Baffa dukansu kaya iri daya suka saka duk suna tsaye waje suna amsan bakinsu ana gaggaisawa, parking mota ahankali Mamu yayi dayasha wanka yay wani kala sanan yafito, Baffa dake gaisawa da jama'a kaman ance ya waigo ganin Mamu natahowa shi kadai babu Zayn yasa yay murmushi yacigaba da gaisawa da mutanenshi daidai Mamu yakaraso gabansu, Baba yace "ahh Mamu kunzo ina Zayn din"? Baba yay maganan yana duba motar da Zayn yay parking, juyowa Baffa yayi yakalli Mamu da akama tambaya yay shiru yakasa amsawa kai tsaye Baffa yace "ina Zayn"? Ahankali yasa hannunshi a aljihu sanan yaciro wani envelope fari yamikama Baffa yace "Zayn yace nakawo maka Dad" kallon envelope din Baffa yayi sanan yasaki yar murmushi yasa hannu ya karba sanan yabare envelope din yazaro doguwan paper dayake ciki yana karanta abinda ke ciki Baba na kallonshi saida yagama karanta takardan tass sanan yakalli Mamu yace "wuce kaje Mamu nagode" ahankali Mamu yawuce yatafi dasauri Baba yace "menene a wasikar" mikama Baba wasikar yayi sanan yasa hannu yaciro wayarshi daga aljihu yay dialing number Ammi kai tsaye yace "na sake ki saki daya!" Ihu Ammi tahauyi kawai ya katse wayan yajuyo yakalli Baba dake kallonshi ranshi a bala'in bace yace "mehaka bansanka da irin wanan

fushin gaggauta yanke hukuncin b….” Hannu Baffa yadagamai sai kawai yakama hannun Baba yajashi zuwa chan nesada masallacin anatse yace “ka yarda dani amini na”? Gyadamai kai Baba yayi, Baffa yace “ka yarda da hukunci na”? Ahankali Baba yace “sama da kowa aduniyan nan” anatse Baffa yace “inhar hakan ne kuma na isa nacemaka kayi abu aduniyan nan kayi inada wanan kiman a idanunka kiramin mahaifin Aliyu yazo wajen nan yanzun nan” wani kalan kallo dayakemai yasa Baffa yace “amini na, akwai wani abu damu karan kanmu amatsayin mu na iyaye bamu da iko akai, nasan mahaifiyar Ummulkhairy taso Zayn da Khairy amman karka manta da abu daya koda take raye mahaifiyar Zayn bata taba sonta ba hasalima basa shiri, Wanan sakin datasa Zayn yama Khairy Allah yasa hakanne mafi alkhairi bazan maka karyaba naji dadin hakan tun yanzu kafin aje ko’ina yasaketa ba sai bayan aureba bayan yagama wulakantata ba yasako mana ita ba, ni nan da kai mun yarda da tarbiyan Aliyu dakuma natsuwanshi, sakin da Zayn yamata was not his fault trust me Allah shine jagoran abin nan dan haka karmuyi gardama komujada hukuncin Allah, kira mahaifin Aliyu atare dasu Manaf yau za’a daurama Khairy da Aliyu aure” ijiyan zuciya Baba yasauke ko Allah ma yasani batun yauba har cikin ranshi yanason Aliyu inda ace babu aure akan Khairy dazai bashi, kiran Dad yayi yacemai dan Allah kome yakeyi yabari yazo it’s urgent, Dad bai musaba dayake clinic dinshi inda Aliyu yake kwance baida wani nisa da masallaci duka duka cikin 5min saiga Dad yazo yana sanye da manyan kaya.

Dad hawayen farinciki ne kawai baiyiba da aka fadamai komi atake yanke aka tafi masallaci aka daura Auren Manaf da Aisha, Mu’az da Maimuna, sai kawai sukaji Liman na gyara speaking kawai ji sukayi an daura Auren UMMULKHAIR DA ALIYU akan sadaki dubu dari uku wanda sune all the kudi dake aljiJhun Dad.

ARE YOU GUYS HAPPY💃
Wanan Littafin na kudi ne karki karanta batare dakin biyaba kika karanta min littafi ban yafeba.

wa.me/+2347012181461
To chat me up on watsapp

This novel is 1k
Pay 1k into 3107021073 aisha Muhammad saiki turomin evidence of payment ta watsapp number na 07012181461
Thank u❤️

5️⃣7️⃣

Wanan Littafin na kudi ne karki karanta batare dakin biyaba kika karanta min littafi ban yafeba.

wa.me/+2347012181461
To chat me up on watsapp

This novel is 1k
Pay 1k into 3107021073 aisha Muhammad saiki turomin evidence of payment ta watsapp number na 07012181461
Thank u❤️

Ana gama daurin Auren duksu Manaf sukazo zasuma Baba magana hannu yadaga musu alamun later sanan shida Dad suka gaisa kafin su rungume juna ahankali Dad yace “thank you” cikeda farin ciki Baba yace “thank you nima, anjima ku aiko adauki amaryan ku and In sha Allah zuwa dare idan mutane suka ragu zamuzo mu gaida Aliyu” sakinshi Baba yayi suka rungume juna cikin aminci da Baffa sunama juna godiya sanan yajuya yatafi, sai alokacin su Manaf sukazo wajen su Baba kafinma suyi magana Baba yabawa Manaf takardan hakan yasa yakarba dasauri yashiga budewa.
“Abba, Baffa ina neman gafarar ku, ku yafeni banda haka inaso na shaidamuku da gaskiya ta wanda Allah yaga zuciyana yasan hakan ne, Abba inason Ummulkhairy da duka rayuwana, inaso zama da Ummulkhairy amatsayin matata har zuwa karshen rayuwana, Abba……” sai maganan ya yanke kafin yaje next paragraph.
“Nasaki Ummulkhairy saki daya, biyu, uku, Abba Ummulkhairy deserve happiness and some light arayuwanta, ayanda Ammi hates her Kona aureta I doubt I can give her that, kuyafeni Zayn!” Linke takardan Manaf yayi ahankali yabama Abba sanan yawuce abinshi Mu’az biyedashi bawai ya tsani Zayn bane kodaya shi dama bayason auren da Zayn sabida tun mama nada rai ba shiri suke da Ammi ba, Ammi har Baffa ma tana nema tafi karfinshi ballema so bayason kanwarshi taje taita wahalanta, banda haka Aliyu is a great guy infact he’s even happy, Zayn din yaje chan yakarata da wacce Ammi keso ya aura atleast sister shi yanzu tasami Aliyu datakeso shima yake sonta so Alhamdulilah dagashi har Mu’az da Maheer babu wanda abin yama ciwo.

**
Waiwaiye Baya Kadan!
Falon Zayn yashiga ahankali yana kallon ko’ina yanda yake nan tsaf tsaf an gyara, wata Yar aikin Ammi yagani tana saukowa daga sama cikeda girmamawa tace “Hajiya tace kasameta adakinta na sama” danjim yayi sanan yawuce sama ahankali yana hawa benen, bude kofan dakin Ammi yayi da sallama chan kasa yashiga Ammi na zaune kan gado as usual taci gayun nan kaman wata matan shugaban kasa tabi Zayn din da mugun kallo yanda yay wani kyau shi adole ango sanan tace “kazaci bansan abinda nakeyi bane dani kake wasan buya Zayn” ahankali yamaida kofan yarufe sanan yazo gabanta ashagwabe zaikai hannu yatabata cikeda lallashi tawani irin dakamai tsawa tace “don’t touch me Zayn, don’t you dare” tsayawa yayi chak yana kallon, hawaye yaga sun zubo daga idanunta cikeda kunci tace “bantaba nadaman

haihuwa ba sai akanka Zayn” wani irin zaro idanu yayi cikeda damuwa yace “Ammi why are you talking like this mena miki ne dan Allah” nuna kanta tayi sanan ta bubbuga kirjinta tace “Zayn ni mahaifiyar ka kake tambaya mekayimini iyye?? Ni, Zayn nikake nunama banda daraja da amfani a rayuwanka eh? Okay listen bari kaji abinda yasa nakiraka” sauka daga gadon tayi tamike tsaye jaraba fall idanunta sanan takai hannunta takama nononta guda tana kallonshi tace “inhar nacika uwarka Zayn wacce ta tsugunna tahaife sanan tabaka wanan nonon kasha, ta raineka sanan ta tarbiyantan dakai harzuwa kawowa wanan lokacin, inhar nakai matsayin uwa agareka Zayn to ayau ni mahaifiyarka nake baka uBmarni kasaki Ummulkhairy ka auri Aisha yarinyar kawata dana zaba maka”….
Wanan Littafin na kudi ne karki karanta batare dakin biyaba kika karanta min littafi ban yafeba.

wa.me/+2347012181461
To chat me up on watsapp

This novel is 1k
Pay 1k into 3107021073 aisha Muhammad saiki turomin evidence of payment ta watsapp number na 07012181461
Thank u❤️

58

Wanan Littafin na kudi ne karki karanta batare dakin biyaba kika karanta min littafi ban yafeba.

wa.me/+2347012181461
To chat me up on watsapp

This novel is 1k
Pay 1k into 3107021073 aisha Muhammad saiki turomin evidence of payment ta watsapp number na 07012181461
Thank u❤️

Wani irin kallon mahaifiyar shi yake yana mamakin wanan wani irin tsana ne me Ummulkhairy da mahaifiyarta sukama Ammi datakisu haka, cikin fushi sosai Ammi tace “nikake kallo kamaida Yar iska ko bari kaga” filon kan gadonta tadaga tadauko wani sharp wuka tace “ai ita Ummulkhairy wish din dead mahaifiyarta ake cikawa akanta nima bari na kashe kaina maybe

alokacin ne zakabi umarnina” kawai Ammi tadaga wukan da gaske zata chakama kanta dawani irin sauri Zayn yazo hannunta da wukan kekai yakama chak yana kallonta saiga hawaye sun zubo daga idanunshi sharrrrr murya chan kasa yace “Ammi basai kin dauki rayuwanki bane zan miki biyayya ba” ijiyan zuciya yasauke kana ganinshi kasan abin namai ciwo sosai hawaye yasake gangarowa daga idanunshi yana kallonta still. Ahankali yace “Ni Zayn nasaki Ummulkhairy” da dayan hannunta dabai rikeba Ammi tanunamai uku, wasu uban hawaye ne sukai gushing daga cikin idanunshi zuciyanshi namai ciwo ahankali yace “saki uku” sanan yakarbe wukan hannun Ammi ahankali kafin yajuya zai fice cikeda zafi tace “ina zaka sami paper ka rubuta kabama Mahaifinka nasan zaice nina saka amman na shiryamai kome zaimin yayi, dolenshi dai yaje ya nema maka Aisha ka aura” bude kofanta yayi yafice yana goge idanunshi yay side dinshi jiyayi yama tsani komi da komai bazaima iya kara 1 good minute anan Nigeria ba, flat dinshi yawuce koda yashiga Mamu na bathroom hakan yasa yadauki paper da buro yashiga rubutu yana share hawaye kafin ya linke yasa a envelope yadaura kan gadon sanan yadauki wani bag pack yadauki su international passport dinshi da other necessary abubuwa dayake bukata kafinma Mamu yafito yawuce kawai yafita yashiga mota straight to airport.
Wanan kenan!!!

Wuraren 4 Baba da Baffa suka dawo gidan bikin dudda akwai mutane cikeda gidan sama sukayi zuwa dakin Baba sanan suka tura Batool taje ta taho da Ummulkhairy.
Ummulkhairy na zaune adakinta abin duniya yamata yawa babu abinda kemata dadi aduniya, tai wani irin zuru zuru Batool yashigo dakin tace “tashi muje su Baba nakiranki zaa fara miki fadan Amarya” kallon Batool tayi tama kasa tashi ita kanta bazata iya explaining yanda takeji yau dinan ba kaman tamutu kawai takeji, kamata Batool tayi tana gyara mata lullubi sanan suka wuce zuwa falon Baba da ita suka bude kofa suka shiga, daga Anty Mariya sai Mom da Baba da Baffa zaune suka shigo zama sukai akasa Baba na kallonta yanda tai kyau sanan yay gyaran murya yace “Ummulkhairy nazo miki dawani sabon labari dudda nasan ba lallai bane kiso kijishi ba” Baba yadanyi shiru kafin ahankali yace “dazu muna wajen daurin Auren yayyinki babban amincin Zayn yakawo mana wata wasika daga Zayn” Baba yasakeyi shiru, ahankali Baffa yace “Ummulkhairy d’ana Zayn ya aiko da wasika dake dauke da saki, yace yasakeki saki uku!” Dawani irin sauri daga su Mom har Batool da ita kanta Khairy ke kallon Baffa, dan ijiyan zuciya Baffa yasauke anatse yace “I don’t want to go into details Ummulkhairy, nasan Auren Zayn burin mahaifiyar kine, amman wanann da tunkafin akai ko’ina Allah ya wargaza al’amarin inaga akwai wata aya da Allah ke kokarin nunamana Ummulkhairy dan haka kiyakuri” wani irin gyamboo taji zuciyanta namata tun dazu zuciyanta namata ba dadi amman na yanzu is like times 1000, Aliyu kawai take tunanowa da wulakanci datamai, ta wulakanta wanda ke sonta kaman zai haukace, tacimai mutunci, tamai gori da Zayn, tayi insulting pride na Ya Aliyu gashi yanzu wanda yasa tamai haka yasaketa tunkafin akai ko’ina kaico! Wani kalan kuskure tayi arayuwanta ne haka Ummulkhairy! Baffa ya katse mata tunani ta hanyar kiranta hakan yasa ta kalli Baffa, anatse Baffa yace “Ummulkhairy mun daura miki aure da Aliyu ga sadakin ki nan!” Wani irin zaro idanu tayi tanajin maganan kaman amafarki taga Baba yatashi ya ijiye mata wasu

bandir na kudi akan cinyanta, ahankali Baffa yace “saidai mijin naki Aliyu baida lafiya sosai har yanzu yana gadon asibiti mahaifinshi yace ayanzu haka baimasan wanda ke kanshi ba, anjima dukanmu nan bayan sallan magrib zamubar kome mukeyi muje mu duboshi, kekuma nan bada jimawa ba dan mahaifinshi yariga yakiramu za’azo daukanki gidansu za’akaiki for now, idan yazo yaji sauki In Allah ya yarda sai ayi duk bikin dazasuyi akaiki gidanki ki tare kinsan yanzu babu wani shirye shiryen da akayi bikin yazo mutu bakatatan” Baffa yay shiru sanan Baba yace “Ummulkhairy inaso idan kinje gidan mijinki kiyi koyi da halin mahaifiyarki, nasan Aliyu baida mahaifiya tarasu, amman yanada Kaka da Matan Baba da kanne, nasanki da girmama mutane inaso kibisu sau da kafa karnaje complain akanki sai yabo, ki kasance mai tsoron Allah da biyayya ma mijinki dan yanzu aljannar ki na karkashin mijinki ne……..” Baba yashiga mata fada mai ratsa jiki dayasa tafara kuka, har cikin ranta dataji ance an aura mata Aliyu jitayi kaman an cire mata wani babban kaya azuciya amman kuma aliyu ya tsaneta, but ba matsala idan shine battling dinta agidan mijinta she is ready zatai fighting for her love back she will win Ya Aliyu back and taroki gafaranshi lokaci yayi yanzu dazata zama dat sensible and matured girl da Mama koda yaushe kEhso tazama.

Wanan Littafin na kudi ne karki karanta batare dakin biyaba kika karanta min littafi ban yafeba.

wa.me/+2347012181461
To chat me up on watsapp

This novel is 1k
Pay 1k into 3107021073 aisha Muhammad saiki turomin evidence of payment ta watsapp number na 07012181461
Thank u❤️

5️⃣9️⃣

Wanan Littafin na kudi ne karki karanta batare dakin biyaba kika karanta min littafi ban yafeba.

wa.me/+2347012181461
To chat me up on watsapp

This novel is 1k
Pay 1k into 3107021073 aisha Muhammad saiki turomin evidence of payment ta watsapp number na 07012181461
Thank u❤️

Daga Baffa, Anty Mariya, Baba da Mom babu wanda bai mata fada da wa'azi cikinsu ba, wajajen 6 Baba yace "wife kutafi da ita ta shirya motocin daukanta na hanya" gyadamai kai Anty Mariya tayi sanan suka dagata ahankali tana kuka sosai daki aka kaita wanka akasa tayi sanan aka bata ruwan turare tayi dashi sanan tafito shiryata sukayi cikin wani milk hadadden lafaya mai bala'in kyau, 6:40 hadaddun motoci sunyi layi gaban gidansu kowane mota dan sanda ne da full uniform keja dan duka boys sun Aliyu Dad yakira.
Tsaf aka shiryata bakaramin kyau tayiba aka lullubeta sanan aka fito da ita takasa daina kuka she can't believe shikenan dagayau tabar gidan iyayenta rungume Baba tayi gam gam ana guda ana ayiriri sun dade ahaka shima Baba idanunshi sunyi ja sosai sanan yadagota yace "ya isa haka kukan kar kanki yayi ciwo" ahankali yakama hannunta yasaukar da ita kasa ana binsu suka fita tsakar gida har zuwa kofar gida da kanshi yabude kofar motan kafin ahankali yace "go in peace Ummulkhairy, ubangiji Allah yama aurenki albarka, ina rokon Allah to bless your new home yakuma haskaka rayuwan aurenki, go my daughter" yay maganan yana sata cikin motan ta zauna ahankali tana kuka, shiga motocin su Mom sukayi da kawayenta da Batool sanan aka tafi da ita.

Tsakanin gidansu Aliyu da nasu nada nisa sosai, dan sai wajajen 8 nadare sukakai, wowww Batool dake gaban motan tafadi ganin Babban gidansu Aliyu, an bude gate wato kudi nada kyau dudda su kansu basusan da bikin ba but they were able to pull something an zuba kujeru hadadun agidan ga DJ an kawo, yan uwa sun cika gidan ko'ina hayaniya ga girke girke abinci kala kala na yawo a tsakar gidan, kafin sufito daga mota Gwaggo da Mami dasukaci gayu na gani afada sukazo taransu idan kaga Gwaggo zaka dauka an mata bushara da Aljanna ne, fito da Khairy akayi daga mota kawai Gwaggo tafashe da kuka Dan she can't believe Ummulkhairy ce aka kawomata amatsayin Matar Aliyu danta, taruwa akai kan Gwaggo dake kuka cikin kuka tace "ni kubani y'ata na rungume" murmushi su Mom sukayi sanan suka kawo mata Ummulkhairy dakenan alullube tawani irin rungumeta tana mata ruwan saman addu'a a godiya aka sanan tasaketa tace "kushigo" shigowa sukayi babban falon Mami aka fara kaita aka zaunar da ita atsakiyan dakin ana waka ana rawa Mami na murmushi ana cemata saita saya baki zata ganta, kudi Mami takawo da box na warwarayen zinare tadaura kan jikin Khairy ana ihu ana guda sanan aka bude mata fuskan Khairy kallon fuskan Khairy da idanunta ke kasa tayi sanan tamata addu'a kafin a dauketa akaita dakin Gwaggo, Gwaggo da dan kafafunta dababu lafiya rawa tahauyi Haba zokaga dariya sanan takawo turaman zani guda ashirin tabama Khairy da bandir na yan dubu dai dai guda uku, da zoben azurfa da warwaron azurfa da sarkan azurfa masu kyau sosai aka dinga guda, tashi Mom da Anty Mariya sukayi sukai sallama da su Baffa najiransu suzo aje aduba Aliyu,  da Kyar Khairy tasakesu suka tafi sai kuka take sanan Kaka takaita dakinta dan fir tace "ita awajenta Khairy zata zaune har zuwa aliyu yaji sauki tanada dakuma daban daban dayawa a side nata, wani hadadden daki aka kai Khairy gadon ciki ma sabone fill dan dazu da rana Dad yasa wani furniture company suka kawo aka chanza komi na dakin aka fitarda nada zaunar da ita akai akan gado itada Batool da Amal kawarta sauran

mutane duk suka tafi.

Wuraren 10 su Baba sukakai asibitin Dad, Dad dakanshi yazo yadauke su akasa yace “barkanku da zuwa” gaisawa sukayi suna sama Baba yace “yajikin nashi” ijiyan zuciya Dad yasauke yace “Alhamdulillah muje” sukai sama har zuwa wajen wani daki, bude kofan Dad yayi ahankali yashiga su Baba biyedashi Aliyu na kwance kan wani hadadden gado da kayan asibiti idanunshi akulle he’s attach to wani machine, salati su Baba sukayi, Baffa yace “what’s the plan yanzu” dan ijiyan zuciya Dad yasauke yace “wanan machine din shine taimakama heart dinshi to beat, beating na heart nashi is very slow, so yanzu dai gobe zamu fitardashi zuwa Oman akwai wani heart Dr achan he’s my very close friend tare mukai karatu a Ukraine yace nakawoshi Aliyu will be fine” dukansu ajiyan zuciya suka sauke Baba yace “In sha Allah zaiji sauki, please if u need anything we are here for you yanzu munzama family” murmushi Dad yamusu cikedajin dadin maganan su yace “Allah yabar zumunci nagode sosai” motsi da Aliyu yayi yasa dukansu suka kalleshi dasauri Baban yay wajen gado yana kama hannunshi yace “Aliyu, Hydar I am here can you hear me”? Wani irin bude idanunshi Aliyu yayi kadan da kana gani kasan baya cikin hayyacinshi sanan murya chan kasa yace “Um….mulk….hair” kafin yakara lumshe idanu kaman bashi ne yay motsi ba, sakinshi Dad yayi yadanyi murmushi yajuyo yakalli su Baba da jikinsu yay sanyi sosai yace “tun shekaran jiya haka yake saidai yadan bude idanu kadan yakira sunan Ummulkhairy yakoma” dan murmushi Dad yasakeyi sanan yakalli Aliyun yace “one thing I am sure of shine d’ana na bala’in son Ummulkhairy so thank you Alhaji dakuka auramai Ummulkhairy bazan taba mantawa da wanan kyautatawan dakukamin da d’ana ba” yay maganan yana juyowa yakalli su Baba daduk sukejin badadi suna addu’a Allah yabashi lpy, sun dade a asibitin sai wajajen 12 na dare sanan suka tafi, Baba da Baffa sun dade suna magana sanan kowa yawuce gidanshi.

Saida sukakai gida sanan Mom takalli Baffa kafin tafita daga cikin motan ahankali tace “one thing danasani cewa inaso gamedakai shine rashin yanke hukunci acikin fushi, nasan ba hurumina bane nan amman inaso na roki alfarma biyu daga wajenka” tai dan shiru tace “nafarko shine inaso kamaida Ammi and inaso kai kokari and look at her situation and understand her, batasan da Auren nan ba itace mahaifiyar Zayn, taci buri kan danta is understandable idan taki yarda da Auren nan kowa da kalan zuciyanshi, kuma yanda Zayn bai auri yarinyar nan ba barabonshi bace wlh inda rabonshi ne daba Ammi ba ko duk aduniyan nan ne basu isa suraba Auren nan ba, sai alfarma tabiyu shine ko’ina Zayn yaje ka kirashi danka ne, nasan yanachan cikeda damuwa yasa kazama karamin mutum da sauransu kanunamai bahaka bane yadawo gida, Auren Ummulkhairy ko rashin aurenta won’t change kai mahaifinshi ne yazo idan yanason wacce Ammi keso ya aura wato Aisha kaje ka nemamai Auren idan bayaso yakawo kowa yakeso ya aura, rayuwa batada tabbas kowa datashi kaddaran just look at Aliyu yanzu yanachan kwance rai hannun Allah yay giving up but Allah yaga zuciyanshi cikin sauki yabashi Ummulkhairy, komi yafaru nada dalili sometimes abinda mu iyaye kesoma yaranmu is not the best or Khair for them, I know u are hurt amman kayakuri and forget everything let this family

continue to be in peace kaji”? Gyadamata kai Baffa yayi ahankali bude kofa tayi zata fita dasauri yakamo hannunta hakan yasa tajuyo takalleshi, ahankali yace “I am so lucky to marry a wife like you, Allah yamiki albarka” murmushi tayi tace “Ameen” sanan tawuce ta tafi shikuma yadan dade zaune a motan sanan yaciro wayanshi yakira number Zayn ringing yake yana gab da tsinkewa yadauka.

Ahankali Zayn yace “Abba kayafemin I am so sorry” murya chan kasa Baffa yace “shiiiiiii Zayn i understand you Allah yasa hakanne mafi alkhairi, kana ina”? Murya chan kasa tace “ina wani hotel ban sami flight ba yau saida safe” anatse Baffa yace “dare yayi yanzu dan haka forget about tafiyan nan gobe dasafe kadawo gida kajini, I am not angry with you one bit hakama Baffan ka shima he’s not, so kadawo gida kadauki komi amatsayin kaddara inda Ummulkhairy matarka ce da Ammi n ka bata isa taraba Auren nan ba, so it’s okay, kadawo gida inaso kafito dawata yarinyar ka aura idan wacce mahaifiyarka keso ne to idan ma ba ita bane duk daya kaji” gyadamai kai yayi ahankali yace “thank you Abba” murya chan kasa Abba yace “don’t cry again good night son” ya katse wayan.

60

Wanan Littafin na kudi ne karki karanta batare dakin biyaba kika karanta min littafi ban yafeba.

wa.me/+2347012181461
To chat me up on watsapp

This novel is 1k
Pay 1k into 3107021073 aisha Muhammad saiki turomin evidence of payment ta watsapp number na 07012181461
Thank u❤️

Jirgin karfe 6 nasafe Dad da abokinshi sukabi aka wuce da Aliyu Oman.
****

Dukansu adakin sun makara sabida yanda akai bacci late jiyada daddare, Ummulkhairy tafara bude idanunta wuraren 8 nasafe, saman dakin tabida kallo komi nadawo mata sabo she can’t believe ita Amarya ce and tana gidan iyayen mijinta Aliyu anan ta kwana, tashi zaune tayi ahankali tana kallon Batool da Amal dake shargan bacci sanan ahankali tamike tsaye tawuce bayi, shiga tayi ta maida kofan tarufe sanan tabude tap wanke fuskanta tayi takalli madubi tai wani irin fresh fatarta tayi da sulbi sulbi yakeyi tsabagen dirzan gyaran jikin da aka mata tarame babu abinda yarage ajikinta banda boobs da hips, ijiyan zuciya tasauke ahankali sanan tadauki brush sabo dake dakin tadauro alwala tafito daga bayin ganin Batool zaune yasa tashimfida dadduman dake dakin tadauki hijabi tasaka tai salla.

Koda ta idar zama tayi tai shiru tana tunani, Aliyu kawai zuciyanta keso yagani tabashi hakuri, tsayawa akanta Batool data fito daga bayi tayi tace “tashi kije kiyi wanka ki shirya” gyadama Batool kai tayi sanan tamike tsaye ahankali tana kallon Amal dake bacci still sanin bata salla yasa tawuce bayi batare data tadata ba.

Wanka tayi tafito daure da towel set na akwatin da Baba yamata Batool tashigo da daya shigo daga cikinsui sanan ta ciro mata wani lafiyayyen lace ja, shiryawa tayi da taimakon Batool duk wanda yaganta saiya kara kallonta, mayafi Batool takawo mata tayafa mata aka sanan ta feffesa mata turare tace “fita kije ki gaida Gwaggo tana falo” Gyadamata kai Ummulkhairy tayi sanan tabude kofa ahankali tafice tanabin corridor dake kamshin turaren wuta sanan tadaga labule tafito falon, Gwaggo na zaune afalon kan daya daga cikin jerin kujerun dake falo 3sitter tana burga wani lafiyayyen fura a kwarya, Meena na zaune kusada ita itama tasaka atampanta mai kyau sosai, ganin Khairy yasa tawani irin ijiye wani empty kwaryan dake hannunta wanda tarike tana jiran Gwaggo tagama ta tsammata tadauke kai, kaman ance Gwaggo ta waigo sabida kamshin turaren da jikin Khairy keyi ganin Khairy gaban corridor kanta akasa kana ganinta kasan kunya takeji yasa tawani washe baki tana kallonta tace “jama’a kuzo ku kalli Matar jikana Ali Gadanga kusar yaki” dan gajeren tsaki Meena taja mara kara tana kara dauke kai kaman taga kashi, ahankali Khairy takaraso gabanta sanan ta tsugunna har kasa akunyace tace “Gwaggo ina kwana” dungure kan Meena Gwaggo tayi tsabagen dadi tace “dan gidanku kalli yanda ake gaida manya ba irinku ba da kullum kedamuna da kud moni daga tsaye kuna shanyemin jini masu bakin hali, tashi tashi kinji diyata Allah ya lullubeki da albarka, zauna kenake dama ma fura zo zauna nan kusadani ke Meena matsa mata” gyara zama Gwaggo tana kara matsa mata girgiza matakai Khairy tayi akunyace tana kokarin zama akasa dasauri Gwaggo tace “kul karki zauna akasa, sokike sanyi ya shigeki kina amarya, zauna nan kan kujera kusadani kiga, matsa mata Meena” tai maganan tana tunkude Meena wani mugun kallo Meena tama Gwaggo kaman ta maketa sanan ta tashi fuuuu tafice daga dakin Gwaggo tabita da harara tace “kinga bakin hali yan gidan nan ko dukansu haka suka gaji Wanan bakin halin daga wajen ubansu, zauna kiga” zama ahankali Khairy tayi kan kujeran Gwaggo itama ta gyara zama da kyau sanan takarasa kada furan tamika mata tace “ungo sha kena dama mawa” ahankali tasa hannayenta biyu takarba tana murmushi sanan takai bakinta takurba furan kadan dadi sosai tadade bataci abinci hakaba tass tashanye furan Gwaggo nawani irin murmushi sanan takarbi kwaryan tace “kawo nan kiga banson kiyi komi, ko sauro banson ya cijeki zan taya Aliyu kula dake harsu dawo daga kasan waje” kallon Gwaggo Khairy tayi dan batagane metake nufiba hakan yasa Gwaggo tace “yauda sassafe aka tafi dashi kasan waje sabida zuciyanshi ba lafiya Baban shi yakaishi wajen wani abokinshi likitan zuciya kidinga ma mijinki addu’a kinji In sha Allah zaiji sauki” gyadama Gwaggo kai tayi ahankali tana kokarin rike hawayenta dan duk itane dalilin Wanan rashin lafiyan nashi.

Yan aikin Mami ne suka shigo da manya manyan kulolin abinci zasu ijiye a falo tace “tafin musu dashi chan dakin Amarya” wucewa cikin sukai sa abincin, ahankali Gwaggo tace “tashi kije kiyi Kari ki kwanta ki huta anjima kawayena zasuzo su ganinki kinji” gyadama Gwaggo kai tayi

sanan ahankali tace “nagode Gwaggo” wani irin washe baki Gwaggo tayi tace “ohh Allah yabani mai mini godiya, gantalallun yaran gidan nan kome zan musu babu godi bare nagode, yimaza jekiyi Kari ki kwanta kihuta Khairiya Allah yamiki albarka” wucewa ciki tayi tana dan murmushi.

Da rana kawayen Gwaggo tsofaffi su kusan goma sukazo gidan damai kidan kwarya, wasu tsofaffin wakoki suka dingayi suna sa Khairy rawa sai dariya ake kafin daga baya su bata gift nasu, buhun gishiri, goruba, aya dasauransu sai dariya ake sanan suka tafi wajajen 6.

Bayan sallan isha’i mota yazo zai tafi da Batool da Amal Khairy tai kuka kaman me hakanan tana gani suka tafi babu yanda ta iya aka barta ita kadai agidansu Aliyu danma Gwaggo na sonta kaman tahadiyeta da abin duniyan sun mata yawa.
*****

Shigowa yayi falon Ammin nashi ahankali yana sanye da  jumper na faran shadda yayi kyau saidai yadan rame da ita kanta Ammin tagani but she knows he will be fine, tashi Baffa yayi babu yabo ba fallasa yakalli Ammi dabasa wani good times yanzu sosai saidai yamaida ita yace “muje ko” gyadamai kai tayi tana murmushi sosai ta mike juyawa Zayn shima yayi sanan suka fito Mmotan Baffa suka shiga Zayn najan motan Ammi na nuna hanya harsukakai gidan Aminiyanta dasuke kira da Hajiya Kwangila.

Babban gidane sosai ga ma’aikata ta ko’ina suna parking a compound din wata mata wacce kibanta kenan kaman na Ammi bakinta hakoran makka guda hudu na gold sama biyu hakiran kasa biyu tafito cikin shiga na alfarma tareda mai gidanta wanda yakenan business mogul Chanchangii kenan, karasowa sukayi matan tawani rungume Ammi tace “barka da zuwa aminiyata, ina yini Alhaji” tai magana tana gaida Baffa dake gaisawa da mai gidan cikin mutunci sanan takalli Zayn da kanshi ke kasa ahankali yace “ina yini” cikeda fara’a tace “surukina Zayn Oya dan Allah kushigo kun tsaya anan” tai maganan tana kama hannun Ammi sukai ciki shikuma Zayn yagaida Baban daya rungume shi cikin ao sanan akai cikin gida, wani lafiyayyen falo suka shiga aka zazzauna yan aiki suka shiga kawo kayan kwalama shaaaaa kafin sugama suwuce.
Cikeda natsuwa Baffa yay gyaran murya yace “Alhaji to ga d’ana nan Zayn, da izininka inaso idan ka aminta dashi kabashi permission na neman yarka, idan sunga juna sun aminta da juna sai mufara maganan aure ko” wani kallon juna da Ammi da Hajiya sukayi sanan suka kama hannun juna suna murmushi, Alhaji yace “Alhamdulillah Alhamdulillah, naji dadin hakan kuma ina fata Allah yatabbatar mana da alkhairi kira Aisha wife” tashi Hajiya tayi tai sama sanan Alhaji yace “sunan Y’ata Aisha, a UK tai karatu tayi Mass com, Aisha nada kirki dakuma hankali da girmama na gaba da ita” ahankali Baffa yace “Masha Allah”
Wani hadadden daki Hajiya tashiga ganin wata yarinya zauna gaban madubi tasaka hadaddun kaya tajuya ma kofan baya yasa tace “wai dan gidanku Aysha bazaki sauri ba maisa bakijin magana ne namiki alkawari zakiso Zayn” hawayen idanunta tashare ahankali tace “Momy ni

Zayn din danakeso daban dan Allah ki karamin 1month na nemeshi yana nan Abuja kinji" fizgota Mom tayi tadagata ciked masifa tace "wlh zan kwada miki mari nizaki maida karaman mutum ga yaro chan da iyayenshi afalo da babbanko kinki fitowa dau gyalenki jor" ahankali tadauki gyale zata yafa karba Mamanta tayi tayafa mata tana murmushi tace "kinga yanda kikai kyau kuwa wuce muje" yakama hannunta saukowa falon sukayi, tunda suka fara saukowa Zayn ke kallonta idanunshi kur akanta jiyayi zuciyanshi na bugawa fat fat fat ahaka har suka karasa saukowa kasa kanta nakasa tace "ina yini Abba, Mom ina wuni" daga Baffa har Ammi murmushi sukayi ganin yarinya mai natsuwa gata kyakkyawa gatanan fara kaman Zayn din, murmushi Ammi tayi sosai tace "Zayn tashi kuje garden ku zanta mu muna nan muna namu na manya" dasauri Hajiya tace "kai shi Garden Aisha" tashi tayi ahankali kanta akasa hakama Zayn shiya fara gaba suka fita tana biyedashi kanshi akasa har zuwa garden suna shiga garden yawani irin fizgota da mugun karfi baki tabude zatai ihu yadaura hannunshi kan bakinta yana mannata da bango yana wani irin huci ware idanu tayi gabanta na mugun faduwa ganin Zayn Zayn data dade tana nema, hannunshi yazare daga bakinta yanunata da yatsa yace "how dare you Ayshu" wani irin murmushi tayi tanaji kaman zuciyanta zai fito sabida murna tace "Zayn" da yatsa yanuna ta yace "listen to me kome zaki fadama iyayenki kifada musu baki sona karki sake kibari ahada Auren nan dan bazaki taba jin dadin aure na, i can't marry a girl datasan namiji awaje" wasu hawaye masu zafine suka zubomata murya chan kasa tace "Bantaba son wani namiji kaman ka ba Zayn" yana kallonta in the eyes yace "amman kuma kika bama wani chan virginity naki" jitayi zuciyanta yamata zafi, ahankali tace "I regretted everything, I had sex once u were the second sex danayi in my life dan Allah that shouldn't be a barrier to aurenka Ya Zayn idan bansameka amatsayin miji ba I can die" dauke kai Zayn yayi yawuce kawai yaje yazauna rayuwan shi babu abinda kemai dadi but he just feel Allah ne ke kamashi, he has been a bad boy, yaci mata daban daban turawa yasha shisha gashinan yanzu the only woman daya taba samu bai sameta ba, look at yarinyar da Allah yahadashi da ita his life is ruin.

61

Wanan Littafin na kudi ne karki karanta batare dakin biyaba kika karanta min littafi ban yafeba.

wa.me/+2347012181461
To chat me up on watsapp

This novel is 1k
Pay 1k into 3107021073 aisha Muhammad saiki turomin evidence of payment ta watsapp number na 07012181461
Thank u❤️

Yau one month kenan da bikinta, Baba, Anty Mariya dasu Ya Manaf babu wanda baya kiranta

yaji yaya take hakan namata dadi.
Ko kadan babu wani wanda yake kuntata mata agidan kawai dai she feels agidan Gwaggo kadai ke sonta da Dad sauran harda Mami duk basa sonta barinma Meena, ko Meena natare da Gwaggo dazaran tazo wajen zata tashi fuuu tafice, hakama su Amal da Khadija, Mami kam ko kallo bata isheta ba gashi batada hanyan waya da Ya Aliyu taga yayake, tana zaune da Gwaggo dabata barin ko tsinke ta taba kullum cikamata ciki da abinci da magani, bata wani iyacin abinci ko Gwaggo ta lurada hakan fura indomie sune tafici indomie shine kadai aikin da Gwaggo tabari tanayi shima sabida taga tana sone.

Yau ma kaman kullum tana zaune adakinta taji Gwaggo ta kwala mata kira, da sauri ta sauka daga kan gadonta tana sanye dawani simple dogon Riga na atampa kai kyau, dan kwali tadauka tadaura sanan ahankali tafito daga dakin nata tabude kofa tazo falon ganin Dad yasa wani irin kunya yakamata da sauri tajuya takoma daki Gwaggo tai dariya tace “kaganta nan Abdul haka yarinyar nan keda kunya wlh naji dadi da Aliyu yasami yarinya mai natsuwa haka, mayafi takoma tadauko fa” dan murmushi Dad yayi danshi kanshi ta burgeshi, bata wani jimaba tafito da Babban mayafi sanan tazo har gaban Dad ta tsugunna zata gaidashi dasauri yace “Ummulkhairy zauna zauna” ahankali tazauna sanan kanta na kasa tace “Abba ina kwana andawo lpy” ahankali yana kallonta yace “lpy lau Ummulkhairy yaya kike hope babu wani matsala ko” gyadamai kai tayi ahankali zuciyanta namata wani kalan dadi buri ta kawai taga Aliyu, kaman Dad yashiga mind dinta anatse yace “Aliyu yaji sauki garau Alhamdulillah, amman mun baroshi chan ya tsaya yin wasu abubuwa nan bada jimawa ba shima zai dawo” gyadama Dad kai tayi ahankali tanajin hawaye na zuwan mata amman tadaure tahana kanta yi, dan murmushi Dad yayi yace “Bayan aurenku nai tafiya batare dana baki gift dinki ba Ummulkhairy, ungo” Dad yay maganan yana mikamata key mota, ahankali tadago kanta takalli Dad dake mikamata key ahankali tasa hannunta takarba kafin tamai godiya Dad yace “mota nasiyamiki as my gift, nasan baki iya tuki ba nai hiring direba dazai koya miki tuki cikin 3 weeks yatafi kidinga jan motanki da kanki kullum zai dinga zuwa yana daukanki 3hrs daily kinji” wani irin murmushi tayi har ranta taji dadi tace “Abba nagode Allah yakara budi” sanan ta taho wajen Gwaggo anatse tace “Gwaggo Abba yabani mota” wani irin murmushi Gwaggo tayi tace “Iyye akashe lafiya muje Muga motan” tashi tayi tana kama Gwaggo suka fice Dad yabita da kallo now he sees why danshi ke sonta Ummulkhairy is extremely calm ga natsuwa hankali ga kunya wani mad Benz Dad yabata sabo fil ko Leda baa cireba, fitowa Mami tayi kallo daya tama motan takoma daki abinta, Gwaggo tace “Oya shiga kitafi kifara koya kai ka ko yamata mota ahankali kajini ko” Gyadamata kai direban yayi sanan suka tafi, shi kanshi Direban saida yay mamakin yanda tai catching up kome yake ko yamata fast.

Kullum direban ke zuwa before one week Ummulkhairy ta kware saidai yan abubuwan dabaza arasa ba bayan 2weeks direban yafadama Dad ta iya, Dad dakanshi ya shiga motan nata tajasu har zuwa inda zaai mata license, nan da nan aka mata komi sai murmushi take, sanan Dad yakaita shopping just to make her happy dan harga Allah yanason Yariyan kuma kome yaranshi keso yanaso dudda Aliyu na claiming baya sonta kawai jinshi yake u can’t fight love bari

yadawo, duk wani abu datakeso saida Dad yasaya mata saida yamma sanan ta tukosu suka dawo gida parking tayi a compound din batare da Dad yafita daga motan ba yace "Ummulkhairy" kallon Dad tayi ahankali tace "naam" ahankali Dad yace "I know kin damu this is almost 2month dabikin ku bakiga Aliyu ba, Aliyu is fine he's just going through a lot now, but I assure you yakusan dawowa, all I want from shine ki kwantae da hankalinki idan wani abu nadamunki always come to me, always come to me, sanan duk randa kikeji zuwa wani gu saloon or wani abu ko bananan kifadama Gwaggo ko Mami kafin kitafi, ki kula da kanki kinji, everything will be fine, Allah yamiki albarka" ahankali tace "Ameen Abba nagode" tashi kije zan sa'a kawo miki kayanki ciki" gyadama ABBA kai tayi sanan tawuce ta tafi.

62

Bayan 3 month!
Sosai Ummulkhairy tai kyau kyau da wayansu barinma some kawayenta cewa suke tanada ciki nan ko basusan haryau batama saka angon nata a idanu ba, tayi kyau sosai fatarta tai fresh yana wani walkiya, jikinta ne har yanzu bai dawo ba sabida rashin iyacin abinci, yanda Gwaggo da Dad ke sonta abin har mamaki yake bata ita badadan tamasan yanda Baba ke sonta ba dazata iya cewa Dad yamafi Baba sonta itadasu Mami dasu Meena haryau suna nan yanda suke. Wuraren 10 tashiga bayi danyin wanka bayan tagama gyara dakinta dana Gwaggo dudda Gwaggo tahanata amman ina taki tasaka turaren wuta, wanka tayi tafito tana kallon wani kofin tsumi da zafinshi akan madubinta tasan aikin Gwaggo ne tun kafin bikinta har zuwa yau babu ranan da baa bata magani dauka tayi tasha tana tabe fuska sanan ta shafa mai tadauko wani pencil gown na atampa light blue da ash tasaka yama jikinta dam yafito da kyanta fitowa falo tayi Gwaggo tace "wuce kiyi kari kafin kitafi saloon din amiki kitso, Baban ku yama ijiye miki kudin saloon din kafin yafice asibiti yanakan gadona jekiyi kari tukunna masa ce da farfesu" gyadama Gwaggo kai tayi sanan tawuce ahankali tadebo masa biyu kachal tazuba farfesun tadawo kusada Gwaggo tazauna tagumi Gwaggo tayi tace "ohh ni bantaba ganin makiyar abinci irin Khairiya ba" dan murmushi tayi tafara ci biyun ma sabida Gwaggo tasata agabane tacinye tass sanan ta tashi takai kwanon cikin wankewa tayi takife sanan takoma daki, wani karamin gyale ash tadauka da karamin hand bag da wayanta da car key dinta tafito, Gwaggo tabita da kallo tace "yarinyar kirki kinga yanda kikai kyau kuwa" murmushi tayi Gwaggo tace "saima kinyi kitso da lalle zakiga yanda zakiyi kyau yau jedauko kudin akan gadona" wucewa dakin Gwaggo tayi tadauki kudin datagani kan gado yan 1k bamatasan iya yawansu ba tafito rikedasu zatabama Gwaggo Gwaggo tace "inyi me dasu wuce kitafi sabida agama dawuri" gyadama Gwaggo kai tayi tace "Gwaggo natafi insiyomiki goro idan zan dawo"? Dasauri Gwaggo ta Gyadamata kai tace "eh adawo lpy ayi tuki ahankali" gyadama Gwaggo kai tayi sanan tawuce tafita daga dakin, wajen motarta tahango Meena tsaye taci gayu kaman fita zatayi hango Khairy nazuwa yasa tajuya baya ta tashi daga jikin motarta karasawa wajen Ummulkhairy tayi harzatata shiga motanta saikuma taji no bazata iyaba she needs to talk to this girl today, dawowa tayi sanan tasha gabanta tana kallon fuskanta ahankali tace "Meena ina zaki I can drop u naga

direban ku bayanan, let’s go with my car” dauke kai Meena tayi tace “I don’t need anything na wacce tayaudari Yayana taso takashe shi, I hope idan yadawo yarabu dake cus u don’t deserve Ya Hydar wlh” ji Ummulkhairy tayi jikinta yay sanyi all this while dama tasha zargin fushin da Meena keyi da ita kenan gashinan yau ta tabbatar, kasa motsi tayi ganin haka yasa Meena kawai taja tsaki tawuce side din Gwaggo, Khairy takusan 3min ahaka sanan tawuce tabude motarta tashiga sanan tadata aka budemata gate tafice, wani babban saloon taje aka wanke mata kai akai drying kalaba tasa aka mata yan kanana sanan tasa amata red lalle dan batason baki nan aka shiga mata wani lafiyayyen jan lalle atafin hannu da yatsu dakuma kafanta, bayan angama around 3 tasa aka mata facials da lip therapy, wani irin kyau fuskanta yakarayi lips dinta yay jajir wuraren 5 tagama komi tabiya kudi sanan tafito, tsayawa tayi agaban building din tasaima Gwaggo goro sanan tadawo tashiga motanta ta tada motan taja tana kallon hannayenta yanda sukai kyau kaman wata Amarya tana kallon fuskanta ta madubi kaman ba itaba fuskanta yay kyau lips dinta kaman na new born baby tsabagen pink din dasukayi, ahankali take driving abinta looking so adorable harta shigo anguwansu, tsayawa gaban gate tayi tai horn daidai wayanta na ringing kallon wayan tayi ganin Batool ne yasa da sauri tadauki wayan da hannu daya tasa akunne daidai ana bude mata gate batare dayama kalli cikin gidan ba taja motan tana waya.

“Mara mutunci wai bazaki zo wajena ba” parking tayi awajen parking sanan takashe motan tabude tafito ahankali waya na kunenta still tana sauraron labarin da Batool kebata awaya, sanan tasa hannu tadauko jakanta da ledan goron Gwaggo kafin tadauki gyalenta dake kan sit tarike a hannu shima sanan tamaida kofan tarufe tafara tafiya tana murmushi tace “are you serious Batool, yanzu yaushe zasuzo asa ranan I am so happy for you Batool” tai maganan tana kokarin saka hannunta tabude kofan dakin Gwaggo daidai anrigata bude dakin,  Amal da Khadija suka fito dagudu dan Gwaggo ce tabiyosu sata sukai mata ko kadan basusan da ita ba suna bude kofan suna fitowa aguje suna bugeta wani irin ihu tayi daga jakanta wayanta dake kunnenta da car keys din hannunta zubewa sukai akasa itama tai wani irin baya zata fadi dan gabaki dayama tasadakar faduwa zatayi chak taji an tarota bayanta yafada kirjin mutum hannunshi gabaki daya kan flat cikinta ta kankame idanunta gam sabida yanda ta bala’in tsorata ahankali ta furta “Ya Aliyu” danshi kawai yafado mata arai yanda he always hold her idan zata fadi, tsayawa chak Amal da Khadijan sukayi jikinsu narawa suna kallon Gwaggo datafito arude tace “Innalillahi badai ihun Khairy naji ba zubarmin da diya kukayi” murya dakuma kamshin turaren da bazata taba manta kalanshi ba da jikin datasaba jinshi ba yasa ahankali tashiga bude idanunta tadaurasu kan Gwaggo dake gabanta tana kallonta, dasauri Gwaggo tace “sannu Khairiya da Aliyu bai tareki ba dakinyi mummunan faduwa barayin banza kawai ku kwashemata kayayyakinta” ahankali tagyara tsayuwanta jikinta narawa gabanta nafaduwa sotake tajuya takalli Aliyun amman takasa tsoron yin hakan ma take tanajin beating heart dinshi abayanta, gently taji yana zare hannunshi dagakan cikinta kafin yacire gabaki daya, gently taji yaraba jikinshi da nata yajuya dasauri, dasauri Gwaggo tace “bazuwa kayi kasha furan ba

dakace nadama maka” kaman daga sama Ummulkhairy taji maganan Aliyu.
“Nafasa sha adakin ki, kiba yaran nan sukawomin” Dawani irin sauri Ummulkhairy tajuya tadan saci kallonshi bayanshi kadai ta iya tagani dudda bataga fuskanshi ba gani tayi yakara wani irin haske gashin kanshi yakara yawa kaman tunda yaje baiyi aski ba gashin yay baki sun nannade looking so coily, hannunta dataji an kama yasa dasauri tajuyo Gwaggo ce tana rikeda kayayyakin ta dasuka fadi akasa tace “wuce muje kukuma barayi duk wacce tashigomin daki wlh saina chanza mata kamanni” dariya su Amal sukayi suka wuce flat din Mami abinsu.

Suna shiga daki Gwaggo tace “dazu kina tafiya Saloon mijinki na dawowa nai nai da shegun yaran nan sukiramin wayanki nace ki dawo sukaki, zoki kaimai furanshi flat dinshi kidawo” kallon Gwaggo tayi dasauri hakanan taji gabanta nafaduwa kwaryan furan Gwaggo tabata data rufe ahankali takarba tana kallon Gwaggo, Gwaggo tace “wuce ki kaimai tunda yadawo baici komi ba yanzu ma da kyar nasamu yace zai sha furan, tafi kafin yay fushi” Gyadamata kai tasake yi sanan ahankali tajuya jikinta rawa yake sosai tafice daga dakin tai flat din Ya Aliyun kirjinta na bugawa more the more she’s getting closer to flat din, tsayawa tayi agaban kofan takasa motsi ahankali tadaga hannunta knocking kofar tayi shiru babu wanda ya amsa babu wanda yabude mata takai kusan 3min ahaka sanan kaman wacce tazo sata tasa hannunta tabude kofan ahankali tana kallon falon ganin bataga kowa ciki ba yasa ahankali tashiga cikin falon dakenan sanyin Ac mix da kamshin turarenshi, ahankali takai kwaryan furan kan centre table na dakin tsugunnawa tayi ta ijiye sanan tamike tsaye dasauri tajuya zatai kofa tafice kaman daga sama taji muryan Ya Aliyu yakirata. “You!” Chak ta tsaya batare daya juyoba gabanta nafaduwa sosai, cikin wata kalan murya da she will define it more of hatred voice yace “zokidau abinda kika ijiye and take it out” gyadamai kai tayi ahankali sanan tajuyo batare datama iya dagakai takalleshi balle tamasan daga ina yakamata maganan ba sanan tazo ahankali ta taugunna tadauki furan sanan tamike tsaye. “Next time idan tanason naci kome tamin tabama wani yakawomin not you” wani irin sanyi jikinta yayi dasauri tadaga idanunta dasuka wani cikeda hawaye ganinshi tayi yana tafiya akan stairs zai koma sama bakinta harwani rawa rawa yake tace “Ya…..Ali….yu” chak ya tsaya batare daya juyo yakalleta ba, ahankali takai dayan hannunta dat is very tashare hawayen dasuka zubomata sanan gently tace “Ya Aliyu I am sorry, dan Allah kayafemin”



Wucewa sama taga yayi abinshi batare daya juyo yakalleta ba, tadade tsaye awajen sanan ahankali tajuya tafice daga dakin rikeda kwaryan furan jitayi babu abinda kemata dadi, dakin Gwaggo tashiga ganinta da kwaryan furan yasa Gwaggo tace “ya shanye”? Girgixama Gwaggo kai tayi tace “yace bazai sha ba” cikeda masifa Gwaggo tace “shiya sani ijiye kije kihuta abinki kinji” ijiyewa tayi sanan tawuce dakinta tana shiga tafada kan gado kwanciya tayi dasauri tafashe da kuka sosai murya chan kasa tace “he hates me, he hates me” tama rasa mezatayi

